INDA RAI

BOOK 2 PAGE 1

AYASHA ALIYU GARKUWA

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

Yar uwa kinsan illar dake tareda infection kuwa,to bari kiji kadan daga cikin illar da infection yake da ita,kinsan cewa infection yana hana haihuwa,yana hana ma'aurata jindadin mu amala,yanasa warin gaba kowane irin tirare kika sa bazai hana wannan warin fita daga jikin kiba fitar farun ruwa kaikayin gaba tusar gaba duk suna daga cikin illar da infection yakewa Ifyr ki. Ina masu fama da ulcer, Asthma,sickle, ina matar dake fama da fibriod, matsalar rashin haihuwa ko bushewar jiki da fata haddake mai son hibs da breas ina uwar gida maison faranta ran oga a othe room kema ba abarkiba jawarawa da yanmata ku garzayo kuma ku kwada ku gani da ikon Allah da izinin Allah munada VIP chair akwai blood circulatory machine kedai kira number nan domin karin bayani 07035275119 ko kiyi joining group dinmu dan gani da ido👀 sai kunzo ngd https://chat.whatsapp.com/LqcXIrhogcQC1iLdGGNJcZ

Spjg
“Ban fahimci me ɗaya kake son bayyana mana ba Tajudden kana neman mu baka izinin fara neman Mamana ne ko,ko kana gabatar da soyayyar kane? Ko neman Aurenta kakeyi gaba ɗaya!?”.
Ya kai karshen maganar yana kallon Taj kallon cikin ƙwayar Idanu saboda tuna cewa shin meyesa Tajuddeen bai zo da iyayensa ba saboda duk cikin falon baiga ɗaya daga cikin wanda zai iya kasancewa mahaifansa tunda dai yasan shi ɗan ƙasar Ethiopia ne waɗanan kuma duk yasan mutanen ƙasarmu be kuma sanannun ma, sai kuma ya juya idanunsa ya kalli Tajj jin yana cewa.
“Duk abu uku nake haɗewa awaje ɗaya Uncle Bello idan zan samu duk abinda kuka min akai ku mallaka min Ishmah shine burina da Fatana shine kaɗai abinda zai samar min nutsuwa ita kaɗai ce zata zame min tsagi da zai cike gurbin da na rasa, itace kuma zata zeme min inuwa da zan samu in fake”.
Cikin rashin walwala da jin wani irin kallo mai nuni da bincika yace.
“Kuma sai gashi banga waliyyanka ba ko kuma ince magabatan kaba”.
Cikin sauri Sheikh Tijjani Taju Usman Bauchi yai gyaran murya wanda shine Babban ɗa ga Sheikh Tajuh Usman yace.

“Gamu nan mune matsayin waliyyansa kuma magabatansa kuma shaƙiƙansa”.
Anutse Abba ya gyara zamansa tare da sakin wani lallausan murmushi.

Atare suka juya suka kalli Sheikh Tajuh Usman Bauchi jin yana cewa
“Ni da kaina zan wakilci Aurensa sannan in daura auren zan kuma yi farin ciki idan kuka bashi Auren Ishmah zan kuma shugabanci al'amarin in shige masa gaba akan komai saboda matsayinsa mai girma ne awajena nima kuma matsayina halattaccene a wojensa”.
Cikin sanyi suka sauƙe numfashi sai kuma suka kalli juna tare da yin ƙasa da kansu jin Dottijon nayi musu kalamai masu kama zuciya.

Cikin sanyi suka fara yunkurin miƙewa tsaye jin Sheikh Taju Usman Bauchi na cewa.
“Ku tashi mu tafi saboda lokacin sallah ya ƙara to”.
Daga nan suka fita suka bar gidan...

Acan cikin gida kuwa Ishmah ce zaune a falo yayin da akwatina set biyu ke gabanta set ɗaya Maroon color set ɗaya Milk color suna zaune ta juya ta kalli Aunty Nana tare da jan gajeren tsaki saboda wani irin iska mai sanyi da take ji yana ratsa jikinta haka nan kawai take jin zuciyarta yana mata sanyi haka gangar jikinta yayin da jikinta ke amsar baƙon yanayi wanda yafi kama da samar da nutsuwa da kwanciyar hankali wanda batasan sanadinsa ba cikin sanyi tace.
“Aunty Nana ki gani fa har yanzu babu wanda yazo kuma fa sun san munyi dasu ƙarfe uku zamu tafi mu kai kayan saboda mu samu kafin huɗu mu dawo muyi sallar la'asar agida kuma har yanzu basu zoba”.
Juyawa aunty Nana tayi ta kalleta tare da cewa.
“Wallahi fa nima abinda nace kenan?,Shiyasa ma kika ga nayi abinci da yawa saboda ina tunanin za'a zo muci abincin rana ne anan kafin mu tafi”.
Maryam dake shigowa ne ta karbi maganar da cewa.
“Ai dama sai da nace miki Kada kiyi wani abinci ki wahalar da kanki saboda Nasan da wuya azo da wuri kasancewar yau juma'a kuma in munje can ma Nasan abubuwan da zasu bamu in mun dawo shi za'a cicci abinci anan shiyasa ni ban shiga kitchen Bama”.
Ta ƙare maganar tana zama gefen Ishmah.
Dariya Rahama dake fitowa daga bedroom tayi tare da cewa.
“Ke dai Aunty Maryam kina nan wani lokaci idan mutum yace Miki marowaciya bai kyauta ba kina nan kamar Gajimare saboda kyauta, wani lokaci kuma in kinyi magana kamar ta marowata”.
Murmushi Maryam tayi kana tace.
“In kinga dama ma kice ni marowaciya ce”.
Dariya Rahama ta sanya tare da faɗin.
“Kuma kona faɗa babu yanda zakiyi dani tunda nice Autah shiyasa nake fadan abinda naga dama kuma in kwana lafiya”.
Murmushi sukayi dai-dai lokacin kuma suka jiyo sallamar Garkuwa.

Cikin jin daɗi da farin ciki Ishmah ta miƙe tare da amsa mata sallamar kana ta nufi Kofar Falon

ta rungumeta fuskarta ɗauke da Murmushi tace.
“Sannu da zuwa kece kika riga kowa fara zuwa”.
Murmushi Garkuwa tayi tare da cewa.
“Aikuwa dai na riga kowa zuwa dama cewa nayi sai an saƙko Daga sallar Juma'a in zo”.
Hannunta Ishmah ta riƙe suka zauna akan 2sitter tace.
“Gashi kuma kinga nima har yanzu babu wanda yazo yanzu nake ta faɗa”.
Kai Garkuwa ta gyaɗa tare da faɗin.
“Eh toh kin sani mafi akasari lokacin Sallar Juma'a yayi mafi akasarin tituna an rufe Nasan da yawa shine abinda zai hanasu fitowa may be idan an idar da sallar juma'a zasu zo kinga kafin su zo ukun zaiyi sai mu tafi”.
Daga nan suka Cigaba da hira...

Acan cikin Yola kuma a masallacin Lamiɗo Aliyu Mustapha bayan an idar da Sallah har da yawa daga cikin mutane sun fara yunƙurin tashi zasu tafi.
Suka jiyo limamin na cewa akwai Ɗaurin Aurerrakin da za'a yi dan Allah jama'a su zauna.
Hakan ne yasa da yawa daga ciki suka koma suka zauna sai ƙalilan ne daga ciki masu manyan Uzurarrika suka tafi...

Cikin nutsuwa da kamala kana da mutumtaka Liman yayi gyaran murya kana ya sanar da ɗaurin Auren da za'a yi bayan an ɗaura aure na ɗaya anyi na biyu Liman ya gyara zaman microphone ɗin hannunsa cike da farin ciki yace.
“Yanzu kuma in sha Allah akwai ɗaurin Auren da za'a gabatar wanda zamu iya cewa mun godewa Allah da wannan al'amarin”.
Akuma dai-dai lokacin Bappa Kawu ya gyara zamansa wanda yana ɗaya daga cikin mutanen dake cikin masallacin...

*Ethiopia*

Adaya ce kwance agefen gado tana lulluɓe da bargo saboda zazzaɓin da ya rufeta tun daren shekaran jiya bata warware ba.
Ahankali Ummey ta tasa hannu ta taɓa wuyanta cikin tsananin zazzaɓin da take ji ta buɗe idanunta da take jin suna rufe wa ta sake lumshewa.
Ummey kam wasu siraran hawayene suka zuba ta gefen idanunta.
Asina dake gefenta ne ta sauƙe ajiyar zuciya tare da cewa.
“Sannu Adaya Ubangiji Allah ya baki lafiya”.
Cikin ruwan murya irin na wanda zazzaɓi ke bugunsa tace.
“Ameen”.
Ta ƙare maganar tana murmushi,irin murmushi dake nuna jin daɗin cikar buri..

Ita ko Ummey cikin sanyi da rauni ta mike ta koma bedroom ɗin ta.
Adaya kuwa cikin zazzaɓin da take ji da ƙarfin hali ta juya ta kalli Asina.
Da damuwa Asina tace.
“Wannan mutumin bai kyauta mana ba Adaya bai mana adalci ba ya mana tabon da baza mu taɓa man tawa ba yazo ya tafi ya barmu da abinda har mu mutu ba zai fita cikin rayuwar mu

ba”.
Murmushi Adaya tayi kana tace.
“Ni dai ya gamamin komai tunda ya ban takardan saki ko abinda ya min ma sai naji banajin komai akai tunda ni na jawa kaina, wlh bashi da laifi nice nayiwa kai kuma, nayi hakane saboda burina ya sakeni dan in samu damar cimma babban burina na in ciyo mana gasar rawa ta duniya baki ɗaya kuma Alhamdulillah tunda ya sakeni ya gama min komai Nagode mishi, duk da dai ya sabaibayi rayuwata Amman wlh na san ba laifinsa bane”.
Kai Asina ta gyaɗa cikin fesar da numfashi tace.
“Gaskiya kam nima abinda nake tunawa kenan inji sanyi araina saboda already kafin ya tafi ya ajiye mana takardan saki kinga yanzu kina warware sai muci gaba da harƙoƙinmu kuma yanzu ina da tabbacin Abpu da kansa bazai sake sha'awar jo gana Miki Auren dole-dolen nan ba tunda gashi yaga zahiri an Aurar dake ɗin kuma mijin yazo ya sake ki yayi tafiyarsa”.
Cikin jin daɗi ta ɗan runtse idanunta kana ta miƙe ta jingina bayanta da gado saboda tana jin wani irin azabebben zazzaɓi dake cinta daga cikin ƙasusuwan jikinta tunda ziyarar Taj da yayi mata hankaɗar kob ɗaya,  take jin wannan ciwon bayan da ɗan zazzaɓi wanda har yanzu bai sake taba...
Cikin sanyi tace.
“Wannan ke nuna min in sha Allah inada sa'a da rabon ciyowa ƙasata gasar, in sha Allah sai Na zubar da india a wannan shekarar”.
Cikin jin daɗi da karsashi Asina tace.
“Sosai ma dan wlh ko ni in naga yadda keda Izzin kuke juya gabbai tamkar baku da ƙasusuwa a jiki ji nake in sha Allah mune da nasara”.
Rumtse idanunta tayi tare da cewa.
“Ke kina ganin yadda naki ɗaukar hankali kowa”.
Murmushin sukayi tare da tafa hannun.

Agefen Ummi kam kuka take tayi acikin bedroom ɗin ta dai-dai lokacin kuma Aminullah ƙanin Adaya ya shiga ya sameta tana kuka da damuwa ya zauna gefenta daga ƙasa kana ya daura hannunsa Kan gwiwoyinta ahankali Ummi ta ɗago ido ta kallesa cikin sanyi da tarin tausayinta yace.
“Ummi kiyi haƙuri duk kan abinda yayi tsanani ina da tabbacin in Sha Allahu yana tare da sauƙi ki daina kuka in Allah yaso kuma ya yarda za muyi farin ciki matsalar Aunty Ada in Sha Allahu zata zama kamar ba ayi ba mu cigaba dayi mata addu'ar shiriya kuma shima da yayi wannan abin mu kyautata masa zato bamusan dalilinsa nayi haka ba kuma Ummi dama ai.
 Dole na zargi haka zai kasance saboda duk namiji mai mutunci da daraja in dai yaji kuma yayi bincike akan Aunty Ada Nasan dole zai iya sakinta koda anyi Auren”.
Sai kuma ya ɗan furzar da iska mai zafi daga bakinsa cikin tausayi da takaicin halin da ƴar uwarsa ke ciki ya cigaba da cewa.
 “Gwara ma in ace shi ya ganta duk da halayenta da ɗabi'unta ahaka ya ganta yace yana sonta ya Aureta amma mutumin da bai santa ba bai taɓa ganinta ba mahaifinsa ne yasa akayi Aura mishi ita sannan kuma ke kanki kin sani na sani duk duniya Aunty Ada bata da kowa sama damu kuma muma bamu da kowa sama da ita aduniya amma mu kanmu mun shaida halayenta ba masu kyau bane duk da bata kasance mazinaciya ba wannan Allah ya sani mu mun sani ba

mazinaciya bace. Amman ai tana da ɗabi'un da dole mutane zasu ƙyamaceta dayi mata munanan zato".
Runtse Idanu Ummi tayi tana mai jin zafi akasan zuciyarta Aminullah kuwa cikin sanyi ya cigaba da faɗin.
"Kuma kina ma sane Aunty Ada ita kanta take ƙoƙarin watsa Auren da Abpu ke shiryawa akanta so wannan mutumin bashi da laifi akan wannan al'amarin abinda Abpu ma da kanshi ya faɗa yanzu yace ya sani baza arasa.
Makircin da Aunty Ada ta ƙulla ba shine sanadin da bawan Allah nan ya saketa".

Zazzafan Ajiyar zuciya Ummi ta sauƙe tare da girgiza kai tace.
"Aminullah Ni kaina nayi zargin haka nayi tunanin haka Nasan Wacece Adaya Nasan tasan duk wata hanya da zatabi dan ta lalata auren nan Shiyasa nake ta jin tsoro da taraddadi nake ta fatan inga anyi an tare".
A hankali ta furzar da iska mai zafi hawaye na cigaba da zuba tace.
"Yau da muke da wowo nan da muka haɗu dashi suna fita ba ƙaramin farin ciki nayi ba amma sai gashi abin takaici Mahaifinku na baisan Angon ba baisan fuskarsa ba wai abin takaici mai gadin daya samu agidan ma baiga fuskarsa ba ita kanta Adaya da suka zauna awaje ɗaya cewa take batasan fuskarsaba saboda bata ƙare masa kallo ba ko za'a kasheta ita ba zata gane kamanninsa ba da yake shashace".
Sunkuyar da kai Aminullah yayi yana mai jin zafi a ƙasa zuciyarsa yana so yaga Yayarsa ta inganta rayuwar ta ta dawo nutsatstsiyar mace mai aji da kamala ta rabu da ballagantar da kanta, kansa ya dago jin Ummi na cigaba da cewa.
"Yazo duniya ta shaida an daura mata Aure sannan yanzu duniya ta cigaba da ganinta tana zaune agida tana fita tana raye-raye da rawa,tana yawo gari harda ƙasa da ƙasa, wannan al'amari yana yimin ciwo yana ƙona min raina Aminullah al'amarin Adaya yana yimin ciwo".
Cikin ƙarfin zuciya Aminu yace.
"Bakomai kiyi haƙuri kada abin ya mana yawa kinga yanda Abpu yake fama yau lafiya gobe ba lafiya sannan matsalar Aunty Ada ya sake ingiza rashin lafiyarsa musamman ma jin batun sakin nan".
Sai kuma ya ɗan dakata kafin ya cigaba da cewa.
"Da farko Dr da kanshi yace za'a sallamesa amma jin abinda ya faru yasa jikinsa ya kara rincaɓewa dole an ɗaga batun maganar sallama dan Allah ki kwantar da hankalinki kar in rasa inda zanji sanyi inje wajanta in kalli rayuwar da Aunty Ada ta ɗauka ba daɗi in duba mahaifin mu inga ba lafiya sannan in tuna Miyminmu ta rasu keda kike madadinta in kin kwanta ya zanyi? Ko domin Ni ki cire damuwar aranki".
Cikin sanyi tace.
"In sha Allahu Aminullah zanyi dangana zan cigaba da yiwa Adaya addu'a Ubangiji Allah ya kawo mata sauƙi ya kuma shirya mana ita".
"Ameen ya hayyu ya ƙayyum ".
Ya amsa...

*Nigeria*

Daga harabar gidansu Ishmah motocine guda takwas wanda suke jere bisa duk kan alama

akwai wani ɗan ƙwarya-ƙwaryan hidimar da za'a yi yayin da can cikin falon kuma yake cike da mutane wa'anda sun haɗu ne saboda kai kayan Auren Adam can cikin Yola.
Mafi yawan su Ummomin Ishmah ce da kuma ƴaƴayen su da kuma friends ɗin ta ƙarfe uku dai-dai suka shirya suka kai kaya.
Bayan sun kai kaya sun dawo duk sukayi alwala sukayi sallah kana suka baje abubuwan da aka babbasu wanda na tukuicine.
Ajiyar zuciya Aunty Hauwa ta sauƙe tare da cewa.
"Kai gaskiya mutanen nan sunyi ƙoƙari".
Murmushi Garkuwa tayi tare da cewa.
"Toh Aunty Hauwa ba dole suyi ƙoƙari ba ai muma kayan da aka kai musu munyi ƙoƙari sannan babu kayan ƙaranta aciki gaba ɗaya".
Murmushi Ishmah tayi tare da cewa.
"Duk da haka sunyi ƙoƙari tukuicin da suka bada har yayi yawa ai".
Kai Aunty Maryam ta gyaɗa kana tace.
"Gsky dai tukuicin yayi yawa dubu ɗari fa tukuicin".
Garkuwa ce ta karɓa da cewa.
"Aikam sun kyauta tukuicin dubu ɗari  a wannan marra da ake ciki gashi komansu ba ƙaranta".
Ta ƙare maganar tana buɗe Cooler paper chicken sai kuma na gabansa Donut, Cake da sauran abubuwa kana ga Catoons² na juice da faro water da dai sauransu.

Juyawa Aunty Nana tayi jin Ishmah na cewa.
"Aunty Maryam da an ɗauko plate an sassakawa mutane su suci".
Kai ta gyaɗa Aunty Nana kuwa saurin cewa tayi.
"Yawwa ga nan abinci na ma kafin kuci nasu sai kunci abincina".
Ta ƙare maganar tana nufar kan dining tana kwaso Warmers tazo ta ajiye atsakiyar su kana ta dauki tirurrika ta ajiye da plate ta zubawa Aunty Hauwa nata daban kana ta zubawa Hajia Aisha wacce itace ƴar farin su Daddy cike da girmamawa tacem
"Ga naku".
Murmushi Ishmah tayi tare da cewa.
"Mu ma dai in Allah ya yarda mun kusa mukai wannan matakin in da zamuje surai sukarrama mu su bamu komai namu daban Aunty Nana keda  Maryam in banda wulaƙanci Babu abinda kuke mana agidan nan".
Dariya Maryam ta sanya cikin fahimtar junansu tace.
"Toh ba dole muyi muku ba kufa ƙannen Mijine sai ki bari idan Adam ɗin yayi aure nan ne zaku samu Power tunda kun fara zama yayun miji".
Dariya suka sanya Garkuwa kuwa kafaɗar Ishmah ta dafa kana tace.
"Ishmah kwantar da hankalin ki kwana nawa ne ma ya rage matar Adam ta ware Miki kwananki da ban".

A dai-dai lokacin kuma Adam ya shigo duk haɗa baki sukayi wajen cewa.
"Ango!, Ango!!, Ango!!".
Idanunsa ya wara tare da cewa.
"Ina anata Angwaye wa yake ta angoge aini angoge ne ba Ango ba".

Duk juyawa sukayi suka kallesa kana suka ce.
“ kamar ya Angoge”.
Murmushi yayi mai nuni da zallan farin ciki da tsananin annurin dake nuna madaukakin jin daɗinsa yace.
“Ai Ango yana waje ba kuji yadda gidan yaketa baza ƙamshi ba ga Amarya agefenku”.
Da mamaki Garkuwa tace.
“Wace Amaryan kuma?”.
Still fuskarsa ɗauke da Murmushi yace.
“Yar ɗakinki Aunty Ishmah mana”.
Cikin mamaki suka hada baki wajen cewa.
“Ishmah kuma?”.
Kai ya gyaɗa cikin tabbarwarta yace.
“Eh Ishmah mana”.
Kafin suce wani Abu Yah Muhammad ya shigo yana shigowa ya durƙusa gaban Aunty Hauwa da Hajia Aisha da kuma Aunty Amina ƙannen Daddy da yayarta kenan
Wasu hawayen farin ciki suka fara zuba akuncinsa cikin sauri Aunty Hauwa tace.
“Muhammad ya dai?”.
Cikin matsanancin farin ciki yace.
“Aunty Allah ya ƙaddara Allah ya nufa yau an ɗaura Auren Ishmah yau Allah ya nufa Ishmah tayi Aure”.
Da wani irin sauri suka haɗa baki wajen cewa.
“Ishmah?”.
Ishmah kuwa zamewa tayi ta zauna sandan-dam tamkar an daskarar da ita sai kuma ta juya ta kalli Adam dake cewa.
“Tabbas Alhamdulillah”.
Cikin al'ajabi Aunty Hauwa tace.
“Muhammad Bama haka da kai wace iriyar magana ce ka faɗa min gaskiya tsakani da Allah”.
Cikin gaskiya da gaskiya yace.
“Wallahi Aunty Hauwa an daura auren Ishmah tun bayan Sallar Azahar bamu dawo bane saboda mun tsaya anyi sallar la'asar”.
Da mamaki Aunty Hauwa tace.
“Innalillahi Uncle Bello yazo ko”.
Cikin sanyi jiki da wani irin yanayi mai rauni da karyewar zuciya Ishmah tace.
“Uncle Bello yazo Yah Muhammad waye Uncle Bello ya haɗani dashi”.
Ta ida maganar hawaye na tsatstsafo wa cikin ƙwayar idanunta..
Kai yah Muhammad ya girgiza mata dai-dai lokacin kuma suka jiyo sallamar Abba da kansa Abba na shigowa fuskarsa ɗauke da Murmushi  mai nuni da maɗaukakin farin, ciki  sauri Aunty Maryam da Aunty Nana suka koma gefe ganin Surukinsu...

Kallon ƙannen Matarsa yayi tare da cewa.
“Hauwa".
Cikin sanyi tace.

“Na'am Ya Abdullahi”.
Fuskarsa ɗauke da maɗaukakin farin ciki yace.
“Alhamdulillah yau dai Allah ya ƙadarta ɗiyarki ta zama matar Aure an ɗaura Auren A'isha Mamana yau itama ta kasance cikin Inuwar Aure”.
Cikin matsanancin farin ciki Aunty Hauwa ta juya tayi Sujudur Shukur Garkuwa kuwa komawa tayi ta jingina da jikin kushin fuskarta ɗauke da wani irin murmushi mai nuni da zallan farin ciki take faɗin.
“Alhamdulillahi³”
Ishmah kuwa cikin wani irin yanayi da yafi kama da tsoro gami da al'ajabi take kallonsu.

Abba kuwa har zuwa lokacin fuskarsa ɗauke da Murmushi ya ƙaraso cikin Falon ɗan risinawa kan Ishmah yayi kana yace.
“Mamana taso”.
Ya ƙare maganar cikin farin ciki.
Ita kuwa Ishmah jiki na tauna da wani irin sanyi dake saƙƙo mata ta yunƙura sai kuma ta gaza tashi.
Ganin haka yasa Garkuwa ta tallafeta ta tashi tsaye.
Hannunta ya riƙe kana suka juya suka fita.

Sai alokacin Aunty Hauwa ta ɗago daga Sujudur Shukur sai kuma ta kalli Aunty Amina dake cewa.
“Yah Ali baka faɗa mana waye mijinba”.
Murmushi yayi tare da cewa.
“Ɗanku zai faɗa muku”.
Ya ƙare maganar yana fita daga Falon.

Ishmah kam cikin sanyin jiki take biye dashi kai tsaye taga ya nufi BQ.

Ahankali ya tura ƙofar ya shiga idanunta ne suka sauƙa akan Taj dake zaune atsakiyar Falon ya jingina kansa da jikin kujera kana idanunsa alumshe ya fuskanci Alƙibla kasancewar ƙofar falon tana fuskantar alƙibla.
Ganinsa ne yasa ta buɗe idanunta cike da tsananin mamaki lokaci ɗaya taji wani irin sanyi ya sake sako mata tun daga kan maɗigar ƙafarta har zuwa tafin ƙafarta.
Abba kuwa hannunta ya cigaba daja har suka shiga tsakiyar falon gaban Taj.
Ishmah kuwa zuciyarta ne ya buga da wani irin masifeffen ƙarfi bawai ganin Taj bane ya bata tsoroba ramar data ga yayi ne yayi masifar bata mamaki da kuma yanayin data ganshi cikin hargitsi da tashin hankali shine yayi matuƙar tayar mata da hankali tare da gigita mata lissafi cikin rawan baki da rawan murya tace.
“Tajjjjj”.
Maganar ya fito ne daga can ƙasan zuciyarta wanda ya maƙale asaman Lips ɗin ta.

Taj kuwa sai alokacin ya samu damar ɗago kansa duk da cewa ya amsa sallamar su amma bai ɗago kansa ba saboda yanda yake jin kansa ya masa nauyi arayuwarsa yana tuna abubuwa da

dama daga cikin abubuwan da suka yiwa rayuwarsa rubdugu a cikin kwanakin nan, daga cikin abinda suka fi Daga masa hankali shin taya Ishmah zata karɓi sabon lamarin nan da baƙon alaƙar aure da yasa aka kulla musu ba tare da izinin ta ko saninta ba.
Hankali ya ɗago kansa ya ganta da Abba cikin sanhi ya yunƙura.
 Abba ne yafara girgizasa masa kai tare da faɗin.
“Koma ka zauna”.
Ba musu ya koma ya zauna Abba kuwa akan 3sitter dake fuskantar Taj ya zauna kana yaja hannun Ishmah ta zauna a ƙasa ya zamana duk suna gabansa.
Ahankali ya riƙo hannun Taj ya buɗe kana ya riƙo hannun Ishmah ya ɗaura akan nasa sai kuma ya saki nannauyan ajiyar zuciya haka nan yake jin kansa cikin wani farin ciki mai daɗi yau ya sauƙe abu mafi nauyi dake damunsa acikin zuciyarsa, yau Auren Ishmah shine abu mafi daɗi arayuwarsa sama da shekaru goma baiji abinda yasa shi farin ciki ba kamar wannan.
A lokaci ɗaya Taj da Ishmah suka saki wani nannauyan ajiyar zuciya asanda hannunsu ya haɗu...

Cikin girma da Dattako da sanin Yakamata Abba yace.
“Tajuddeen ga Matarka”.
Jin wannan kalmar yasa Taj ƙara sauƙe nannauyan ajiyar zuciya kana ya sake Runtse hannun Ishmah dake cikin nasa.

Ishmah kuwa jin kalmar da Abba ya faɗane yasa zuciyarta ya buga da masifan ƙarfi, wanda hakan yasa ta Runtse idanunta da tsananin ƙarfi.
Sai kuma ta buɗe jin Abba yace.
“Aisha”.
Sunan da baya kiranta dashi sai da babban dalili ahankali take ƙoƙarin buɗe idanunta amma sunyi mata nauyi saboda kalmar da taji ya daketa sai kuma ta sake ƙoƙarin buɗe idanunta jin ya kirata a karo na biyu nan ma still idanun nauyi suka mata da ƙarfi ta buɗe idanun jin Abba ya sake kiranta a karo na uku.

Tana buɗe idanunta yace.
“Mun daɗe muna barwa Allah zaɓi akan lamarin aurenki bana bacci acikin kaso ɗayan ukun ko wanne dare arayuwata A'isha acikin shekaru bakwai ɗin nan addu'a nake ina faɗawa Allah ya Miki zaɓi da miji mafi Alkhairi, wanda zai riƙe ki da amana da gaskiya. Nayi ta shan ƙunci arayuwata a lokuta da dama idan al'amarin aurenki ya ɓaci amma nakan miƙa lamurana ga Ubangiji na kan yarda da cewa lallai suɗin ba mazanki bane da Ubangiji ya hukunta, da su mazan kine A'isha da dole sai anyi Auren”.
Sai kuma ya sauƙe nannauyan ajiyar zuciya mai cike da farin ciki kana ya cigaba da cewa.
“Allah ya amsa mana a lokacin daba muyi zatoba bamunyi tsammani ba Allah ya sauƙaƙa mana abinda yayi tsanani. Alokaci ɗaya Allah ya bamu abinda muka rasa tsawon shekaru wanda hakan ya tabbatar min da cewa Taj shine mafi. Alkhairin da mukayi ta roƙa miki ni da majaifiyarku atsawon shekaru bakwai zuwa takwas da kikayi ba aure, haka ya nuna min cewa Taj shine mafi Alkhairin da Mahaifiyar ki tayi ta roƙa Miki har lokacin da zata bar duniya.
A'isha a yanzu Tajuddeen ya tashi a matsayin abokin mutuncinki ko matsayin abokin sanayya

Tajuddeen mijine agareki wanda aljannarki take ƙarƙashin diga-diginsa. Yau an daura aurenki da Tajuddeen a masallaci Lamiɗo ya samu shaidun dubban Al'ummar Annabi musulmai manya da yara sun shaida aurenki da Tajuddeen, kuma inaji a jikina in sha Allah zai share miki hawayen da maza da kika aura a baya sukayi ta ƙunsa miki kamar yadda aurensa ya share mana ƙuncin tarin masu neman airenki sai komai ya kankama su kuma ce sun fasa".
Ba Ishmah kaɗai ba hatta Tajuddeen wani irin bugun zuciya mai sarƙafe da tunani ke fusgarsa.
Abba kuwa cikin kamala ya cigaba da faɗin.
"Tajuddeen mijine agareki, wanda kuma yasan komai a kanki, kuma yanzu mijinki ne wanda Aljannarki take karkashin ƙafarsa, kuma mijine da in kin mishi biyayya zanyi farin ciki dake, kana mijine da in kika zauna tare dashi zanyi alfahari dake, nayi Miki wannan zaɓin batare da neman izinin kiba duk da kasancewarki bazawara wacce shariya tace a baku dama kuyiwa kanku zaɓi, kiyi haƙuri ki yafe min da rashin baki wannan damar.
Ban zaɓa miki shi domin na gaji dake ko bana sonkiba a'a sai domin ina ji ajikina wannan shine zaɓin da Allah ya Miki A'isha.
Bani ne nayi Miki zaɓi ba Allah ne ya miki zaɓin. Ni dai Fatana zaki min ɗa'a kiyiwa mijinki ki biyayya ki zauna lfy dashi, ki maida yan uwansa naku, iyayensa naki".
Tuni hawaye ke kwaranya a idanunta kwata-kwata bata cika fahimtar duniyar da takeba sai kalaman Abba da duk suke zama a kanta tamkar hadda suna ratsa ma'adanin ƙwaƙwalwarta tana jin yanda suke ratsa dodon kunnenta suna bugun zuciyarta. yanayin da taga Taj aciki shi yafi ɗaga mata hankali.
Ahankali ta buɗe idanunta da suke jiƙe da hawaye ta tsakan kanin gashin idonta take kallon ƙafarsa dake gefenta wanda ke kumbure sai sheƙi yake inda Kwalba ya yankesa kafin ya fito gida.
Abba kuwa kallonsa ya mayar kan Taj tare da faɗin.
"Taj na mallaka maka Mamana da yaƙinin zaka riƙe min amanarta da yarda cewa abinda ka faɗa gaskiya ne na mallaka maka Mamana da yaƙinin kai mutum ne nagartacce dan haka ga Mamana amana ce na baka".
Kai kawai Taj yake gyaɗa mishi domin baya jin zai iya mgna Abba ya bashi kyauta Mafi daraja da gode mishi yayi kaɗan saidai addu'a da kyautatawa ɗiyarsa..
Cikin jin daɗi Abba yace.
"Allah ya muku albarka".
Da kyar ya iya motsa lips inshi yace.
"Ameen".
Abba kam miƙewa yayi ya fita yana mai sa musu albarka tare da jan ƙofar ya rufe.

A hankali ya kalli gefen damanta inda wayarta ke zaune jin tana ringing.
Bappa Kawu. Ya faɗa a ransa a fili kuma ɗaukar wayar yayi tare da amsa kiran tare da yin sallama

Cikin sanyi Bappa Kawu yace.
"Taj ko?".
Cikin sanyi yace.

“A'a Mijin Ma'eesha ne!”.
Sassayan numfashi Bappa Kawu ya fesar tare da cewa.
“Uhmmm kace mai sa'a kenan da yayi ta buge soyayyarmu.
Mai hasken taurari da yayi nasarar samun mallakar Ishmah.”
Cikin ɗan jin sassaucin kishi yace.
“Dama ai kune kukayi tayi min kutse a muhallina”.
Ya ƙare maganar yana kallon Ishmah ta gefen idonshi.
Ita kuwa Ishmah gefen lip inta na ƙasa take ta tsotsa.
“Yanzu dai ai bamu da bakin mgn tunda kayi nasara akan mu, dama na kirane inyi mata fatan alkhairi da sallama da neman gafarar ta Amman fa in ka amince”.
Yana ɗan sauƙe numfashi yace.
“Na amince duk da dai nasan yanzu kai tunanin neman amincewata”.
Cikin sanyi ya manna mata wayar a kunnenta lumshe idanunta tayi jin Muryar Bappa Kawu na cewa.
“Aisha na kasance ɗaya daga cikin waɗanda suka shaida ɗaurin aurenki keda Tajuddeen miji ma ɗaukaki, ina mai tayaki farin ciki domin Allah yayi Miki zabi da mijin da yafimu duk manemanki da komai haƙurin da kikeyi duk sanda aurenki ya watse kike maida komai ga Allah har aci gaba da yin zumunci da iyayenki Kinga Allah yayi Miki kekkyawan sakamako da miji na kerewa sa'a, inayi Miki fatan alkhairi. Allah ya baki zaman lfy da zuriya ɗaiyiba, kiyiwa mijinki biyayya kiyi kuma haƙurin zama gidan miji, ni kuma ki yafe min akan yadda mgnar aurenmu keta zama kamar yaudara.”
Tunda ya fara mgnar hawayenta suka fara kwaranya cikin sanyi tace.
“A'a ni bakayi min komaiba Mukhtar ba yaudara bace kawai dama can Allah bai ƙaddara kasancewarmu ma'aurata ba ne. Na yafe maka nima ka yafe min a zaman da mukayi.”
Murya na rawa yace.
“Na yafe miki A'ishah kuma zanci gaba da zumunci da Abba”.
Daga nan ya katse kiran saboda hawayen dake zubo mishi.

Shi kuwa Taj ajiye wayar yayi a gefentan tare da lumshe idanunsa kana a hankali ya m....

Littafin INDA RAI na kiɗine. Ki biya ki karanta ki rabu da haƙƙin wani a kanki 1k ne 0661110170 GTBank Aisha Aliyu Garkuwa sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276. Mutanen kasar Niger kuma 1000fc jaka ɗaya kenan rak zaku biya ta wurin Mommy +22790899076.

By
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 📝🕋💉🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*INDA RAI*

*BOOK 2 PAGE 2*

*AYASHA ALIYU GARKUWA*

To Kufa matson ayi gyara saboda sauyawar weather kun san cewa, muna buƙatar gyara, dan kauda busher da jiki yake yi a samu damshi da ni'ima da ɗumin jiki.
 Kayane gasu nan kala-kala ko wanne irin haɗi kikeso akwaishi carans. Haɗin amarya budurwa mai ƙarancin shekaru da mai matsakaicin shekaru da kuma mai ɗan yawan shekaru. Kana haɗin amarya bazawarar da take da ragowar ƙuruciya, da mai matsakaicin shekaru da wacce shekaru sun ɗan ja, hadi dai-dai da halittarki ƴar uwata, ƙawata, ƙanwata, ƴata, ƴaƴata, kai harma da ke kakata, akwaisu masu maida tsohuwa yarinya, duk mutuwa da sakewar fatar nan zata tattare ta tsuke ta matse ta rayu da ni'imtaccen yayyafin gyaran zaman aure.
To wai ke mai jego ina kike akwaisu fa naku haɗin, in ma yawan haihuwa yasa wurin ya sake ya kuma ƙafe, barden goyo ko ɗanyen goyo, akwai haɗinku.
Zaki min bayanin me matsalarki!
Sakewa ne? Rashin ni'ima ne? Rashin feeling ne, ko rashin kuzari ne.
Duk fa akwai haɗinshi sai in Miki haɗinki dai-dai aljihunki
Bana barin kuɗin Customers na suzo su koma duk ƙanƙantarsu ko yawansu saboda set ɗin kayansu hawa-haeane.
Akwai manyan set akwai kuma ƙananan. Ƙananan set ɗin daga 40k ne zuwa ƙasa 35k 30k 25k 20k 15k 13k  10k   sai ɗan autansu ɗan robor ƙasaitacciyar macen 5k akwai abu kusan kala biyar a ciki. Sai kuma manyan set ɗin daga 50k ne zuwa sama 60k 70k 80k 90k sai sha kunɗum uban aikin 100k. In kin shirya yar uwa kawai bulbulo min kuɗi in bulbula Miki kaya 0005388578 Jaiz back Aysha Aliyu Garkuwa sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 08069423567. Gareku mutanen Niger kuma ina ita tura muku kaya, in kina da mai amsa Miki shi a Kano ko Sokoto.

Spjdd.
Matse hannunta dake cikin nasa yayi, tare da rumtse idanunsa da ƙarfi.
Itama rumtse idanunta tayi cike da bugun zuciya kusan a tare suka ja numfashi mai kama da ajiyar zuciya ba tare da sun sauƙe numfashinba.

Acan cikin gida kuwa baki ɗaya shiru sukayi a falon suna jin recording ɗin kalaman Taj da ya

riƙa faɗa a Falon Abba kafin su tafi masallaci wanda Yah Abubakar da bai daɗe da shiga ba ya saka musu.
Garkuwa kam Murmushi take tana gyaɗa kanta.

Bayan sun gama saurara Yah Abubakar ya kashe kana ya maida wayarsa cikin aljihu tare da cewa.
“Alhamdulillah, dama bahaushe yace wani jinkiri Alkhairi ne hakan ya zamewa Ishmah baiwa ta samu Mijin nunawa Sa'a ”.
Murmushi Garkuwa tayi cikin matsanancin farin ciki da kasantuwar abin tace.
“Abinda nake faɗa da fata ya zama gaskiya ko kuma ince abinda muke faɗa ai tuntuni na daɗe da gane cewa Sheikh Afif son Ishmah yakeyi amma taƙi yarda shi kuma zurfin ciki ya hana shi bayyanawa saboda iya abinda na fahimta da Ishmah ita batama fahimta ba, shi kuma zurfin ciki ya hana shi ya fito fili yayi bayani.
Amma tuni ni nasan wannan amintaka tasu tafi ƙarfin abota ko amintaka sai ko so, sai dai soyayya mai ƙarfi”.
Da sauri Aunty Hauwa tace.
“Abinda nima kullum nake faɗa wa Ishmah amma ta gaza fahimta ta kasa ganewa bare ta yarda”.
Cikin dariya sosai harda riƙe ciki Aunty Nana tace.
“Habawa bawan Allah yaji soyayyarta zai kashe sa acikin zuciyarsa, itama taƙi fahimta ita sam bata ma gane ba yaga in yaci gaba da ajiyewa soyayyarta zata fasa masa zuciya ta kashe shi.
 Gashi tasa yazo ya fallasa sirrin zuciyarsa agaban su Abba”.
Dariya suka sanya tare da juyawa suna kallon Aunty Maryam dake cewa.
“Tana ƙasa tana dabo, ai ni dama tun randa muka haɗu dashi a Mall ɗin Abaya a Saudi naga harda su bata niƙab daga baya ya ƙara da bata Safar hannu nace, wannan fa sonta yake, Amman a lokacin naƙi yarda da maganar zuciyata dan ina tsoron kar akasa min Yayana Barrister Kamal gashi kuwa bamu tsiraba”.
Sai kuma ta maƙawa Rahma harara jin tana cewa.
“Mu kuma kikayi mana wuff da Yah Abubakar ɗinmu ba”.
Dariya duk suka saka cike da raha.
 Cikin gyara zama Garkuwa tace.
“Aikam da gaskiyar Taj in ba haka ba sai amasa sakiyar da Babu ruwa”.
Murmushi Yah Muhammad yayi still idanunsa na zubda hawaye cike da farin ciki yace.
“Wallahi ya mance cewa agaban Abba yake ya mance cewa agaban mutane masu tarin shekaru yake baki ɗaya ya mance inda yake, kawai zubo kalamai yake akan Ishmah tamkar ruwa na zubowa daga sararin samaniya”.
Murmushi Yah Abubakar yayi yana tuna yanda Taj ke magana da duka gaskiyarsa.
Yah Muhammad kam cikin jin daɗi ya cigaba da cewa.
“Kawai faɗin abinda yake ji acikin zuciyarsa yake na fahimci idan ba abarshi ya faɗi wa'anan kalaman ba zuciyarsa zata iya bugawa ta fashe, Shiyasa Abba ya kasa cewa komai sai murmushi yake yana kallon yanda yake maganganu kamar wahayin maganar ake masa”.
Murmushi Rahama tayi cikin jin daɗi tace.
“Kai Alhamdulillah yau burin Daddy ya cika bayan ranta”.

Baki ɗaya suka haɗa baki wajen cewa Allah ya jikanta da rahma Allah yasa ta huta...

Anutse Garkuwa ta kalli Rahama tare da cewa.
“Yanzu me zakiyi Rahama?”.
Kai Rahama ta girgiza kana tace.
“Ba abinda zanyi Aunty Garkuwa ni na rasa mai ma zanyi arayuwata farin ciki kawai nake ji”.
Garkuwa kuwa kallonta ta mayar kan Adam tace.
“Yawwa Adam ka Kaita gidana zan kira Paulina akwai sakon da zata baku ku kawo min da sauri ina jiranku”.
Kai Rahama ta gyada tare da faɗin.
“Toh”.
Batare data miƙe ba.
Cikin sauri Garkuwa tace.
“Sauri fa nake dashi abu yazo mana abaxata a ƙurarren lokaci ba dole muma mu fara gyara da gaggawa da rawan jiki”.
Murmushi Aunty Hauwa tayi tare da faɗin.
“Allah dai ya miki albarka Garkuwa Ubangiji Allah ya biya ki ina son wannan al'amari ya kasance, kina samun ladan gyara zamantakewar ma'aurata ke Rahama maza tashi”.
Mikewa Rahama tayi Adam kuwa kallonta yayi yace.
“Toh kizo mu tafi”.
Kai ta gyaɗa kana tabi bayansa suka shiga motarsa yaja suka tafi.

Garkuwa kam suna fita ta janyo wayarta ta ta kira Ikraam tare da faɗa mata ta gayawa mai akinta Paulina tashiga dakin kaya ta lissafa mata wasu abubuwa na Musamman da take buƙata ta bawa rahama ta kawo.

Kafin Rahama su isa tuni Paulina ta gana haɗa kayan har ta kawowa Ikraam ɗin.
bayan Rahama ta shiga sun gaisa Ikraam ta miƙa mata ledar tare da cewa.
“Momyna tace idan kun zo in baku dama gashi an haɗa tun kafin kuzo”.
Karɓa Rahama tayi kana tace.
“Toh mungode”.
Sai kuma suka juya suka fita suna fita madadin Adam yabi hanyar gida sai taga ya ɗauki hanyar gidan Hajja Umma ɗan ware idanunta tayi tare da cewa.
“Yah Adam ina zamuje”.
Yana murmushi yace.
“Wannan abin farin ciki Ni nake so inje in yiwa Hajia albishir duk da nasan cewa Uncle Naseer da Uncle Ali nacan dasu aka ɗaura Auren amma sauri nake kada su rigani isa wajen suyi mata albishir”.
Kai ta gyada tare da faɗin.
„Toh shikenan ”.
Koda suka isa suka faɗawa Hajja Umma farin ciki ya rufe ta atake hawaye ya shiga bin kuncinta still tana murmushi kasancewar abu biyu ne ya haɗu mata Auren Jikarta da kuma tuno ɗiyarta da Allah bai nuna mata wannan auren ba da take ta fata da burin ganinsa basu daɗe anan ba

suka fito suka dawo...

Acan gida kuwa kusan baki ɗaya ƴan Uwa sun hallara wannan yakira wancan lokaci ɗaya suka taru Al'amarin auren Ishmah yazo abazata anata addu'ar Allah ya bayyana mata mijin Aure na Alkhairi sai Allah ya saƙko musu da abin alokacin da basu zata ba basu tsammata ba abin yazo musu abazata Akuma ƙanƙanin lokaci Yah Muhammad da har zuwa yanzu bai tashi gaban Aunty Hauwa bane ya juya ya kalli sauran Ummomin sa cikin sanyi yace.
“Alamarin Ubangiji akwai bada mamaki akwai abin tsoro aciki”.
Kallon Aunty Hauwa yayi jin tana cewa.
“Sosai ma Muhammad”.
Cikin sake jinjina girman Ubangiji Aransa yace.
“Al'amarin yanda Auren nan ya kasance da yanda ya faru har tsoro ya bani”.
Hajia Aisha wacce itace babba adakin su Daddy tace.
“Babu komai sai alkhairi in Sha Allahu ”.
Ajiyar zuciya ya sauƙe da faɗin.
“Nima haka nake ji amma wani sashe na zuciyata sai ina jin tsoron yanda abin ya kasance cikin gaggawa".
Yah Abubakar daje gefe yace.
“In sha Allahu sai alkhairi da izinin Ubangiji".
Mikewa Yah Abubakar da Yah Muhammad sukayi jin Abba na cewa kuzo mu tafi.
Sallama suka musu tare da ficewa.

Nan su Aunty Hauwa da Garkuwa Da sauran duk suka dinga al'ajabi akan lamarin Ubangiji daya saƙko da Auren nan lokacin da ba'a yi zato ba ba'ayi tsammani ba...

Acan gefen su Taj kuwa tunda Abba ya danƙa masa hannun Ishmah bai sake ba kana ya kasa buɗe baki yace mata wani abu ba...
Ishmah kam tunda ta Zaurawa ƙafarsa dake yanke ido ta kasa janyewa sai hawaye dake kwaranya daga idanunta.
Jin ya saki nannauyan ajiyar zuciya mai haɗe da zazzafan iska daya fito daga cikin ƙahon zuciyarsa hankali ta ɗago idanunta dake jiƙe da ruwan hawaye ta kallesa.

Kansa ya fara jujjuya mata ahankali alamar ta daina kuka so yake ya buɗe baki yace ta daina kuka amma yana jin harshensa yayi nauyi ta wace siga ta wane yanayi kana da wani furuci ko laɓe ko harshe ko kalmar zai fara gabatar mata da tsananin sonta da yake yi kana da bata hakuri bisa laifin daya mata na aura masa ita batare da saninta ko amincewar ta ba, abubuwan sun taru sunyi masa yawa azuciya haka yasashin jin ya rasa ta ina zai fara bata haƙuri.
Ga kuma Babbar damuwar dake tattare dashi na abubuwa uku fushin ya Abana! Batun cikin Laylah!! Da lamarin wannan karuwantacciyar yarinya Adaya, da ya baro a Ethiopia wanda ya danne ko wanne kuzari dake cikin zuciyarsa arayuwarsa hakan sai yasa ya zuba mata idanun.

Idanu Ishmah ta zuba masa tana kallon yanda ya rame du-du-du da komarsa kwana talatin da biyu ne amma yayi wata ramar data firgitata ta ruɗa mata hankalinta acikin kwanaki talatin da

biyun ma du-du-du sati ɗaya ne baiyi Update na new video saba a Tik-tok wanda har take tunanin meyesa bayayi.

Sosai zuciyarta ta raunata saboda ganin yanda fuskarsa ta rame da kuma yanda sajensa ya burkice ga kuma idanunsa da sukayi Jawur suka sauya launi daga ainihin launin data sansu cikin rauni mai ɗauke da rawa murya tace.
“Tajjjj”.
Kallonta yayi amma baice komai ba saboda bazai iya amsa kiran da take masa ba.
Ahankali ta janye idanunta dake cikin nasa ta mayar kan ƙafarsa dake kumbure yana ƙyalli ga kuma tafin ƙafar da ƙirjin ƙafar da yayi wani irin yanka ahankali taja hannunta dake kusa da ƙafar ta manna akan ƙafar cikin sauri ta Runtse idanunta jin ƙafar tayi zafi jau.
Cikin rauni da bugun zuciya ta maida idanunta cikin nasa tare da cewa.
“Tajj”.
Sai kuma ta fesar da sassayan numfashi tare da lumshe idanunta wanda hakan ya bawa hawayenta damar ci gaba da tsiyayowa.
Shi kuwa Taj tsira mata idanunsa yayi tamkar wahayin kallonta akayi nishi.
Murya ciki da rauni, kulawa, tausayawa da taushin lafazi mai cike da jinƙai tace.
“Tajj me yake faruwa?,Me yasameka?,Tajj meke damunka!?”.
Kai ya girgiza mata kasancewar bazai iya cewa komai ba.
Ganin haka ne yasa ahankali tasa hannunta ta ɗauki wayarta dake gefenta number Rahama ta kira.
Adai-dai lokacin kuma Motarsu Rahama ke shigowa gidan jin Rahama ta ɗauka tace.
“Rahama kawo min First aid box”.
Kai Rahama ta gyaɗa tare da cewa.
“Ina yake Aunty Ishmah?".
Cikin sanyi tace.
“Yana ɗakina”.
“Ok bari na kawo".
Dai-dai lokacin kuma ta shiga cikin Falon bakinta ɗauke da sallama tana shiga Aunty Amina wacce itama ƙanwar Daddy ce ta amsa mata sallamar tare da cewa.
“kin dawo?”.
Kai ta gyaɗa sai kuma ta mayar da kallonta kan Garkuwa dake cewa.
“Ya kuka daɗe haka Rahama?”
Ta ƙare maganar tare da amsar ledan hannunta ahankali tace.
“Wallahi Yah Adam ne yace dole sai mun biya gidan Hajia munyi mata albishir ɗin wannan auren”.
Garkuwa na bude ledar tace.
“Kai haba Shiyasa mana naga kun daɗe baku dawo ba”.
Murmushi Rahama tayi tana kallon Ummominta tace.
“Gaba ɗaya Hajia na gaisheku ta kuma ce tana tayaku farin cikinki Auren ɗiyarku”.
Murmushi Aunty Amina tayi tare da faɗin.
“Mun gode mata itama mun tayata farin cikin Auren Jikarta"
Murmushi Rahama tayi tare da nufar bedroom ɗin Ishmah...

Ita kuwa Garkuwa Da sauri ta miƙe tare da kallon Aunty Nana tace.
“Aunty Nana”.
Aunty Nana dake magana da Aunty Maryam ta ɗago tare da faɗin.
“Na'am”.
“Zan samu kaza?”.
Cewar Garkuwa tana sake buɗe ledan.
Kai Aunty Nana ta gyada tare da cewa.
“Eh akwai wani iri kike so?,na gida kike so ko kuma”.
Shiru tayi sai kuma tace.
“Eh toh tun da dai abin gangawa ne duk wanda ya samu amma in so samune ai Zabuwa muke buƙata”.
Murmushi Aunty Maryam tayi kana tace.
“Ai akwai a wajena”.
Dai-dai lokacin Rahama ta fito daga ɗakin Ishmah hannunta riƙe da First aid box murmushi tayi tare da faɗin.
“Aunty Garkuwa ke dai kinyi farin jini Aunty Maryam bata Miki rowa”
Dariya Aunty Maryam tayi kana tace.
“Rahama cigaba da samin sunan Marowata.
Ta ida maganar tana fita tare da nufar ƙofanta...

Rahama kuwa direct BQ ta nufa abakin Kofar ta tsaya tayi Knowking jin shiru yasa ta sake sallama tare da ɗan ɗaga saurin murya.
Daga ciki Ishmah tace.
“Shigo”.
Shiga tayi ganin Taj yasa ta saki Murmushi lokaci ɗaya fuskarta ya koma kalan rauni ganin yanda fuskar Taj ya rame cikin sanyi ta ajiye First aid box kusa da ita kallon Taj tayi cikin sanyi tace.
“Uncle Taj Barka da Yamma”.
Cikin sanyin murya mai gauraye da tarin damuwa ya motsa Lips ɗin sa tare da cewa.
“Barka dai auta”.
Tana tanƙwashe ƙafafunta tace.
“Yasu Ummeey?”.
Kai ya gyaɗa batare da yace komai ba.
Tana sauƙe ajiyar zuciya tace.
“Uncle Taj ina Laylah?”.
Ahankali ya motsa Lips ɗin sa sai kuma ya kalleta yace.
“Tana gida”.
Cikin farin cikin kasancewarsa mijin yayarta tace.
“Uncle Taj Allah ya sanya Alkhairi Allah ya baku zaman lafiya”.
Wannan kalmar ne yasa ya ɗanji sanyi Aransa kallon idon Ishmah yayi sai yaga bashi take kallo ba first aid box take buɗewa sai kuma ya kalli Rahama dake cewa.
“Uncle Taj sai anjima”.

Kai ya gyada a sanda take rufe musu Kofar...

Ishmah kuwa tana buɗe box ɗin taga duk wasu abubuwa da take buƙata suna ciki ɗaya gefen kuwa magunguna ne buɗewa tayi tare da ɗaukar hydrogen kana ta Ciro auduga da karamin almakashi   ta kama auduguar kana tasa acikin hydrogen ɗin ahankali ta daga Idanunta ta kallesa sai taga shima ita yake kallo.
Ahankali ta motsa Lips ɗin ta still hawaye na zuba musamman idan ta kallesa sai taji wasu sabbin hawaye na zirya a kuncinta cikin sanyi tace.
“Tajj”.
Zanyi maka dreesing”.
Idanunsa ya lunshe tare da buɗewa alamar tayi.
Baya tayi kaɗan kana tasa ya tsarta manuniya da babbar ta riƙe babban yatsarsa na ƙafa na ta jawo.
Tare da ƙunsa
 hauhawar tausayisa cikin zuciyarta da yake motsa mata rauninta

Jin ta jawo ƙafar ne yasa ya ware ƙafan tare da miƙa mata sai ya zamana kafar yana gabanta.
Ahankali ta gyara tankwashe ƙafafunta da tayi ta jawo  pillow dake kam kushin ta ɗaura ƙafarsa akai.
A hankali tasa ya tsarta  inda taga yankan, ɗan dannan gefe-gefen ya kan tayi.
 “Shythhmmmm”. yaja wani daskararren sauti wanda yafi kama da ajiyar zuciya.
Wanda yasa ya daki dodon kunnen Ishmah amma ta gaza fahimtar sautin na menene.
Ɗagowa tayi ta kallesa shima itan yake kallo.
Sai kuma ya nuna mata cikin box ɗin da hannunsa alamar ta ɗauki hangloves ta saka.
Kai ta gyaɗa kana ta janyo hangloves ɗin ta sanya tare da ɗaukar almakashin mai audugan data sama sa hydrogen ta saka abakin yanka.
Atake ciwon ya fara fitar da kumfa duk da cewa bawai datti ciwon yayi ba ga dai yanda yankan yayi ja alamar danye ne babu datti ko alamar ƙura, sai dai saboda bacteria  bashi da ƙanƙantar shiga jikin mutum.
Ganin yanda ciwon yayi yasa ta daga Idanu ta kallesa Araunane tace.
“Ka gani fa , Amatsayin ka na likita kaji ciwo kana wasa da lafiyarka da,  kake dauka kamar bata da muhimmanci”.
Sai kuma ta lumshe raunatattun idanunta dake cike da hawaye tana sharce hawayenta wasu na turo wasu murya cike da tausayawa taci gaba da cewa.
“Kuma idan ma bata da muhimmanci awajenka tana da muhimmanci awajen Ummey da Yah Abana, Ma'eesha kamata yayi ka kula da kanka ko dan Ummey, Ma'eeshah Meymer, Adaya da kuma Laylah”.
Lokaci ɗaya ya Runtse idanunsa sunan Ummey data kira yasa yaji zuciyarsa ta karye har yana ji kamar wani abu ya fito daga cikin ƙwaƙwalwarsa ya faɗa zuciyarsa sai kuma sunan Meymer da Adaya data kira kansa ya bada sautin Dimmm wanda har kunnuwansa sukayi Dimmm na dan wani lokaci hakan yasa baya jin zafin hydrogen ɗin ahaka ta cigaba da wanke wajen.
Sai yatsunta daya tsurawa ido.
Zazzafan Ajiyar zuciya ya sauƙe tare da ɗago idonsa, tsirawa sirrin sajenta yake kallon yanda

ya sake ƙawata kyawun fuskarta.
Sanyayyan ajiyar zuciya ya sauƙe kana ya maida idanunsa kan zara-zaran eyelashes ɗin ta da suka jika da ruwan hawaye da kuma yanda take ƙifƙiftasu.
Wani irin sanyi da nusuwa ne yaji yana dirar masa tabbatas Ishmah ta musamman ce azuciyarsa da rayuwarsa tana da wani irin matsayi da harshe kansa bai isa ya fade sa ba...

Ishmah kuwa cikin nutsuwa take gyara masa ƙafar bayan ta gama wankewa tasa auduga tare da bandeji ta matse.

Ahankali ya sauƙe nannauyan ajiyar zuciya a lokacin da yaga ta rufe First Aid box ɗin.
Anutse ta ture First aid box ɗin tare da juyawa ta kalli kan dining idanunta suka sauka akan Warmers data shiryasu ne sunan Bappa Kawu da komai da komai da ke kai.
Miƙewa tayi ta ɗauko try ta ajiye agefensa kana ta buɗe fridge dake dining ɗin ta dauko plate data haɗa friut da kuma Fresh  da Swan water sai Cock bayan ta ɗauka ta zauna a gabansa.
Shibkuwa kallon wayarsa yayi dai-dai lokacin kiran Abokinshi Dr Amdaz ɗan Qatar ya shigo wayarsa.
Kansa ya kawar gefe.
Ita kuwa Ishmah hawayenta yaƙi tsayuwa ahankali ta cire ledan data rufe fruits ɗin sai kuma tasa fork ta tura masa Bowl ɗin kusa dashi.
Idanu ya zuba mata batare da yace komai ba ganin haka yasa ta ɗauki glass cup ta zuba masa ruwa ta miƙa masa...

Cikin sanyi ya ɗaga kansa ya kalleta sai kuma ya sunkuyar tare da karɓan cup ɗin ya kai bakinsa shi kansa yasan cewa akwana biyun nan da ruwan ne yake rayuwa dashi a cikinsa sai kuma ɗan fruits da yake sha time to time ahankali ya ajiye cup ɗin bayan yasha kusan rabin ruwan.

Kallonsa tayi bayan ya ajiye cup ɗin tace.
“Taj”.
Idanunsa dake cike taf da tarin damuwa ya dago ya kalleta da ido ta nuna masa Bowl ɗin fruits dake gabansa.
Kansa ya jujjuya mata.

Da sauri ta girgiza masa kai murya cike da sanyi kana hawaye na taruwa tace.
“Na roƙe ka da Allah koma menene matsalar ka, kada ka hora kanka da yunwa, Please dan Allah kaji tausayin zucciyata.
Kaci abinci kada kayi fushi da ƙaddarar da zata iya riskarka a ko wani yanayi a ko wani lokaci Kaci abinci ka samu karfin da zaka yiwa Allah godiya da addu'a sannan ya kawo maka sauyi acikin rayuwarka”.
Jin abinda ta faɗa yasa ya zuba mata idanun batare daya iya cire idanunsa akanta ba yana kallonta.
Ganin haka yasa ta ɗauki fork ta soka  yankekkekken kankana data zuba madara akai ta ɗago.
Idanunsa ya ɗaga ya kalleta sai kuma ya sunkuyar da kansa ahankali cikin rauni tace.

“Karɓi”.
Ta ƙare maganar tana miƙa masa fork ganin yanda tayi maganar da kuma yanda hawaye ke zuba a idanunta  yasa ya karbi fork ɗin yasa abakinsa.

Ahankali ta sauƙe ajiyar zuciya ganin yasa abakinsa shi kuwa Ahankali ya tauna ya hadiye yana ji kamar maganine sai kuma ya sake soko kankanar saboda ganin ta tsareshi da ido, ahaka yaci kusan yanka biyar Na kankanar kana  ya ajiye fork ɗin.
Banana ta ɗauka ta bare masa sannan miƙa mishi.
Amsa yayi tare da fara ci.
Ita kuwa fork ɗin ta ɗauka ta soka shi jikin apple, kana ta miƙa masa kansa ya girgiza ya kalli grapes yanzu yana jin zai iya shan grapes.

Ganin haka ne yasa ta kama saman Nonon grapes ta mika masa ahankali ya amsa kana ya maida kansa ya jingina da jikin kujeran ya cigaba da tsinkar ƴaƴan grapes yana tauna yana hadiya.
Ita kam idanu ta zubawa ƙafarsa tana kallon wani irin tausayinsa na bin magudanan jinin jikinta zuwa zuciyarta tuni lokacin Maghiba ta ƙara to....

*Littafin INDA RAI na kiɗine ki biya ki karanta cikin aminci da salama 1k ne kacal 0661110170 GTBank Aisha Aliyu Garkuwa sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276. Mutanen kasar Niger kuma 1000fc jaka ɗaya kenan rak zaku biya ta wurin Mommy +22790899076 Please Dan Allah da Manzonsa kada ki karanta min littafina in kinsan baki biya ba, in kuma kika biya kika rinƙa turawa wasu ko groups wannan kuma keda Allah*

Acan cikin gida kuwa Garkuwa ce tsaye a kitchen yayin da Aunty Maryam ke gefenta cikin dariya sosai tace.
“Wai nikam dan Allah Garkuwa me haka son kai afili so nake na ture Ishmah in maye gurbinta ajikinki amma kinƙi, kuma fa nima yar ɗakinki ne tunda dai Makkan nan tare mukaje ɗaki ɗaya”.
Murmushi Garkuwa tayi tare da cewa.
“Toh son kan me nayi
Maryam kemafa kadaki manta lokacin aurenki haka Naita dibi-dibi dake yanzu ke kin tsufa gashi har kin bugo Hafiz da Hafiza”.
Maryam na gyara tsayuwar ta tace.
“Ki gani fa daga ji an ɗaura auren Ishmah kiga wasu abubuwa da kike ki dafa wannan ki ajiye ki dafa wancan yanzu wannan me yenene dan Allah in ba son kai ba tunda ni lokacin zabuwa kawai kika dafa min”.
Ƴar dariya Garkuwa tayi tare da sauƙe tukunyar data dafa Zabuwa a ciki wanda yaji hadin magunguna na musamman masu kama jiki sauƙe wa tayi ta juye a Warmer kana ta kalli Maryam tare da cewa.
“Ba wani son kai aciki ita fa Amarya ce ke kuma amarya ce. kuma ita Ishmah abu yanzu a ƙurarran lokacin da son samune in tsumata na wata ɗaya zuwa biyu, to wannan Tajj ɗin yayi mana shigar sauri, dan ma dai Allah yayi kwanaki mun ɗan fara kaɗan akan batun Dr Nafi'u da magana ta fara rawa kuma dole muka bari”.

Maryam na matsar da warmer gefe tayi Murmushi tare da cewa.
“Aikuwa tare dani za'a ci”.
Wara Idanu Garkuwa tayi da faɗin.
“Ki yiwa Allah da Annabi ki bari ita kaɗai zata cinye Kuma yau bazan bar gidan nan ba sai ta cinyesa a Idona yanda Auren nan yazo mana a bazata in ba dage mata akayi ba bazata ciba”.
“Kar ki damu ai Maryam na nan zata nace mata dan Maryam nada naci akan magani babu kamar ita duk da cewa itama batasan maganin amma idan ta nace mata dole sai taci”.
Cewar Aunty Nana dake shigowa yanzu.
Cikin jin daɗi Garkuwa tace.
“TOh Alhamdulillah”. Ta ƙare hamdalar suna
ƙarisabfito falon ta ajiye akan dining tana ajiye wa ta fito tare da kallon Rahama tace.
“Ki miƙo min ruwa mai sanyi a fridge”.
Kai Rahama ta gyada tare da ɗauko mata goran ruwa a fridge dake dining tana kawo mata ta karba tare da buɗe ledan da suka kawo mata ta fito da wani ɗan kwanon China tare da cewa.
“Ina su Aunty Amina fa?”.
Rahama na ɗan danna wayarta tace.
“Sun shiga ɗakin Daddy zasuyi alwala sallan Maghiba ya ƙara to”.
Kai ta gyaɗa tare da faɗin.
“Nima bari nayi sauri na dama lokaci ya ƙara to".
Juyawa tayi ta kalli  Maryam dake gyara zaman da Kulolin data kawo kan Dinnin table.
“Yauwa Maryama gwara  fa ki matson nan dan  abubuwa nake so in bar Miki aiki zan baki na bawa Ishmah magani dan Allah ki nace mata".
Dariya Maryam tayi tace.
“Kada ki damu dama nice dai-dai da ita akan magani ”.
Murmushi Aunty Hauwa tayi tare da cewa.
“Toh Ni dai bari na shiga tunda lokacin sallah ya ƙara to".
Kai ta gyaɗa Garkuwa kana tace.
“Toh nima bari na gama tunda lokaci yayi”.
Ta ƙare maganar tana ɓare sabon kwanan ɗan China wanda ke ɗauke da rubutu mai kyau ajiki wanda aka rubuta _Walaƙad Alaihi muhabbatu_ ba rubutune na tsafi ba ko sammu ba ko wani saɓoba, tissue dake gefenta ta zare kana ta goge rubutun sai kuma ta ɗauki goran ruwan tasa ruwa kaɗan ta wanke kana ta ɗauki murfin kwanan shima ta kaɗe sai kuma ta ɗauki robobin data fitar daga cikin kwanan garuka ne kala biyu da gumbuna suma kala biyu sai kuma peak ta ɗauka ta miƙawa Rahama tace.
“Rahama fasa min wannan”.
Karba Rahama tayi tare da nufar kitchen
Ita kuwa roban farko ta buɗe ta ɗebo garin mallaka cokali ɗaya tasa a ruwan rubutun kana ta sake ɗiban ɗaya garin ilanwaddihi ta zuba aruwan sannan ta ɗebo gumbar ɓelɗamhi ta saka tare da gumbar da ba'a baiwa mai kishiya dai-dai lokacin Rahama ta fito daga kitchen ɗin karban madarar tayi ta juye acikin sannan tasa cokalin data ɗiba aciki ta dama lokacin ɗaya ya damu sai ya zama tamkar damun fura da nono ne wanda kuma ta kai har tsakiyan kwanan saboda yawan garurrukan da gumba nan ga kuma ruwa da aka ɗan wanke rubutun tana gamawa tasa murfin ta rufe tare dasa cokalin asama ta miƙawa Rahama da cewa.

“Ajiye min shi a fridge”.
Aunty Maryam dake gefenta tace.
“Nayi zaton yau zata shanye?".
Kai Garkuwa ta faɗa da cewa.
“Eh ganan wannan zan Miki bayani ga paper nan duk bayanin yanda za'a yi amfani dasu na bari aciki kuma ma ai wasun kam kin sansu”.
Kai ta gyaɗa tare da miƙewa itama Garkuwa mikewa.
Sai kuma duk sukayi dariya jin Maryam na cewa.
“Toh Allah dai yasa ma kar suyi mana riga Mallan masallaci.
Abu kusan awa biyu da rabi bata fitoba, karfa yayi mana ba zata irin na auren tun kafin muyi gyaran ta dawo da laulayi”.
Dariya mai sauti Aunty Nana tayi tare da cewa.
“Kai haba dai ustadz ne fa”.
Cikin sauri Maryam tace.
“Ustazan nanfa sunfi iya salsala”.
Murmushin Garkuwa tayi tare da cewa.
“Yo ai mu bamu da haufi ko yanzu yazo tun yaushe muke gyara tun kan Barrister Kamal fa, mukayi na Bappa Kawu mukayi na Salis nan baya kusa kusa mukayi na Dr Nafi'u.
Kawai dai dama bamuyi na sabbin bane, Amman ai bamu da haufi”.
Kai Aunty Nana ta gyaɗa tare da dariya tace.
“Eh baku da haufi kam baiwar Allah duk sun fece sun barta da ciwon mara in ya tashi yana damunta in nace mata rashin mijine tai ta rantse rantse tana cemin wlh ita kam bashi bane, ita ba namiji a rayuwarta ma, firfa taki yarda kuma wlh shine”.
Sai kuma duk sukayi saurin juyawa kan kofar dakin ganin....

*Littafin INDA RAI na kiɗine ki biya ki karanta cikin aminci da salama 1k ne kacal 0661110170 GTBank Aisha Aliyu Garkuwa sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276. Mutanen kasar Niger kuma 1000fc jaka ɗaya kenan rak zaku biya ta wurin Mommy +22790899076 Please Dan Allah da Manzonsa kada ki karanta min littafina in kinsan baki biya ba, in kuma kika biya kika rinƙa turawa wasu ko groups wannan kuma keda Allah*

*BY*
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 📝🕋💉🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*INDA RAI*
*BOOK 2 PAGE 4*
*AYASHA ALIYU GARKUWA*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

Zira idanunsa kan fuskarta, wani irin sassayan numfashi mai cike da rauni tausayinta gami da danne ƙuncin zuciyarsa yaja, kana ya juya a hankali ya kalli fuskar wayarta.
Status ɗin Hamisu take kallo inda yasa wani hotonta dashi da sukayi a tare tana bashi magani bayan rasuwar Daddy da yayi fama da ciwon kai a saman hoton yayi rubutu da manyan baƙi.
"Munyi rashin uwa na tsawon rayuwarmu amma ta hanamu maraici koda na one second ne, ta maye mana gurmin Daddy tun second ɗaya bayan fitan ran mahaifiyarmu, ta ruggumemu ta hana hawayenmu zuba ƙasa.
Sai kuma yasa emojis na kuka sai hoto na gaba wanda suna Airport ne.
Ak'asan hoton ya rubuta.
Kin yi nesa damu, irin nesan da tasa dole na zubda hawayen maraicin da yau ne ya riskemu. Nasan gida bazai sake min daɗi ba.
Amman ina jin maɗaukakin farin ciki da aurene yayi mana rabuwar bazata, ke ba yaya bace a garemu ke uwace kamar yadda Daddy tace ki zame mana uwa harda su Yah Muhammad, mu kuma mu zame miki bongo abun jingina.
Abba kance yana tausayinki saboda ƙaddarar mtsalar da Allah ya jarabceki dashi.
Sai kuma ya sauƙi sassayan numfashi a hoto na gaba daya taho.
Wanda ita da Taj ɗin ne wanda sukayi lokacin zuwanshi suna Murmushi ya rubuta.
"Ku tamkar watane da zara, haɗin ku haɗin Allah ne, inayi miki fatan Alkhairi Ammi dan daga yau bazan sake kiranki da Aunty Ishmah ba sai Ammi saboda na fahimci matsayin uwa kike a garemu.
Inayi Miki fatan al'khairi a gidanki.

Zuwa yanzu kam shesh-sheƙan kuka mai sanyi ne ya subce mata da ƙarfi.
Shi kuwa Taj a hankali ya gyara zamansa tare da fuskantar ta da kyau, kana ya manna kanshi ajikin gadon ya zamana goshinsa na gab da kunnenta, cikin wata iriyar matasaciyar murya mafi sanyi ya kirata da sabon sunan daya sanya mata.
"Babe!!"

Yayi mata kiran da cikekkiyar muryar dake nuna ruwan tausayawa, ƙauna da kuma jink'ai.
Kana ahankali ya kuma ƙara kiranta.
"Babe!".
Jin yadda muryarshi ke ratsa cikin kunnuwanta ne kuma yasa ta ɗan buɗe idanunta a hankali.
Cikin sanyi ya ɗan zaro harshensa ganin hawayenta na tsiyaya har suna gangarowa kan kunnenta.
A hankali ya manna tongue ɗinsa bisa saman kunnen.
Da sauri ta lumshe idanunta saboda jin ɗumin harshensa na ratsa fatarta wanda hakan yasa sautin muryar ta fara sanyi.
Cikin numfashi mai cike da rauni ya fara magana a hankali.
"Babe I know Make many mistake!.

Wata ƙil kinaga kamar na cutar da keko?.
But trust me. Banyi da nufin cutar da keba.
Ki sani cewa you are the most important person in my life".
Ya ƙare maganar can ƙasan maƙoshinsa tare da sake manna tongue ɗinsa ya lashi sabbin hawayenta dake siyayowa.
Sai kuma ya fesar da sassayan numfashi da yasa ta ja wani dogon numfashi saboda jin kalamansa suna sakar mata da wani irin masifeffen kasala da ƙaƙƙarfan bacci mai cike da tsumin zuci wani irin numfashin ta kuma fesarwa mai sanyi jin yana faɗin.
"And if I am saying so sorry Babe.
Zuciyata bazata iya jurar ganin hawayenki ba.
Saboda nayiwa Abba al'ƙawarin bazan bar wahayenki ya sake zuba ba".
A hankali ta ɗan sauƙe hannun ta dake kan goshinta saboda bacci ya sa gaɓɓanta sun fara sakewa, cikin baccin da ya fara surarta ne take jiyo kalaman nasa tamkar sauƙan sautin sarewa.
"Babe you know what? I lovo You more than I love my self, then ni ko bakya sona nasan zan rayu da soyayyarki".
A hankali ya ɗan kuma sake numfashi kana a hankali ya ɗan kalleta jin tana sakin sassayan ajiyan zuciya.
Murya ya ɗan gyara cikin sanyi da zaƙin muryasar ya fara karanto suratul Mulk saboda duk daren duniya sai ya karanta.
Gyara kwanciyarta tayi lokacin da taji yayi basmala ya fara kawo ayoyin cikin ranta ta fara binshi daga aya ta ɗaya.
Zuwa ta biyar daga nan bata sake sanin me yake yi ba, saboda baccin da yayi nasarar danneta.

Shi kuwa Tajj a hankali ya gyara zamansa tare da ci gaba da karantawa har dai ya kai ƙarshen surar.
Sai kuma ya karanto Ayoyi 10 na forkon Suratul Khaff.
Sassayan numfashi ya fesar tare da haɗe tafukan hannunsa, ya karanto Ikhlas,nasi, palaƙ, sannan ya daura da ayatul-kursy da kuma amanarrasulu, a hankali ya kife tafukan hannunsa kan fuskarta tare da shafa mata kana ya fara yin ƙasa da hannunsa yana shafa mata a dukkan sassan jikinta.

Bayan ya kammala janye hannunsa yayi tare da jan dogon numfashi, kana ya haɗe tafukan hannunsa tare da yiwa kansa addu'a.
Koda ya shafa a hankali ya juya tare da manna bayansa da jikin gadon ya zamana yana fuskantar alƙibla.
Tanƙwashe sawunsa yayi tare da yin gyaran murya gami da basmala ya fara karatun Suratul Al,Baqara...

*Littafin INDA RAI na kud'i ne ki biya ki karanta cikin aminci da salama ba haƙƙin wani a kanku 1k ne kacal 0661110170 Gtbank Aisha Aliyu Garkuwa sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276, mutane Niger kuma 1000fc zaku biya jaka ɗaya kenan rak zaku tura ta wurin Mommy +22790899076. Kun dai ji kun kuma gani da idonku kun kuma sani littafina na

kuɗine in baki biyaba kika karanta ke da Allah, in kin biya kuma kika ta turawa wani group ɗin ko groups wannan ke da Allah*

Acan wurinsu Garkuwa kuwa tafiya mai ɗan yawa kaɗan sukayi.
“Wow”
Aunty Nana dake gefen Garkuwa ta faɗa a daidai lokacin da suka kutsa kansu cikin wani tamfatsetsen gini na alfarma wanda daga saman sa can aka rubuta.
*Al-AHLI AFISHA HOSPITAL*
Still “Wow” shine abinda Adam ya kuma fad’a.
Aunty Amina ko.
“Masha Allah”. Ta faɗi tana mai karewa tamfatsetsen ginin kallo, wanda yake tsaye iya ganinka benaye ne na alfarma wanda akayishi da fasalin wf.
Gaba ɗayansu ido suke bazawa suna kallon tsarin farfarjiyar Asbitin.
Inda daga farkon shiga ƙaton filine ta gefen hagu, wanda ya kasance parking spaces ne da zai iya ɗaukan motoci 30 zuwa da biyar,
Sai kuma gabanshi da akayi wani Raund about ɗin flowers koraye shar masu furanni pink and yellow color sai ɗan ratsin red.
Ya kasance yana gaban faffadan steps ɗin da zai sadaka da cikin asibitin wanda suke da faɗi sosai aƙalla ko mutum hamsin zasu shiga kana hamsin su fito hanyar zata ɗaukesu.
Steps ɗin guda 8 ne, sai gefenshi kadan da akayi wurin shiga wanda ko da gadon nan marasa lfy ko keke.
Sai kuma gefen dama wata hanya ce ke shimfiɗe tsakanin flowers.
Wacce mota biyu zasu iya haɗewa wannan na shiga wannan na fita.

Yah Salam shine abinda Aunty Nana ta furta a saman lips inta dai-dai lokacin da taga sun kusa kai cikin wani gate da aka buɗe musu.
Ganin tsarin wurin da ƙawatuwarsa da flowers da kuma bishiyoyin dabino da yelwar hasken wutane yasata lumshe idanunta tare da shaƙar sassayan iska mai ratsa jiki.

A hankali motocin sukayi parking a gaban wani dantsatsen gida na alfarmar ginin zamani mai nuna ruwan kuɗin da aka binne wurin gina shi.

A hankali suka fara shiga bayan an buɗe musu ƙofar.
Suna kutsa kansu cikin Corridor kusan duk atare suka saki Numfashi gami da lumshe Idanunsu jin wani ni'imantaccen ƙamshi mai masifar daɗin shak’a tare da cire duk kan wata damuwa dake azuciyar ɗan adam.

Babban Corridor ne mai fadi wanda koda mota ce zata iya bi ta wurin,  cike yake da yelwar haske daya wadaci wajen tamkar rana saboda haske, sai wani irin sheƙi da walwali da kasan tiles ɗin keyi dana jikin rabin ginin.
Tafiya kaɗan sukayi suka isa wani kofar dakin dake gefen damansu ɗakin ya kasance ciki da falo ne sai toilet gabansa kadan kuwa shoe rug ne na ajiye takalma awajen samansa kadan wani ɗan table ne wanda bisa alamu idan zaka ajiye key, hula, jaka, da dai sauransu gaba

kadan daga gefen dama step ne haka ajere wanda za'a haura zuwa sama ne gidan.
Da yake sashine na musamman da aka shiryawa Taj.
Babban falone mai girma asama wanda ya wadatu da komai aciki komai na cikin falon Neavy blue and white color ne kama daga Cottons, Carpet, kujeru, masu masifar kyau, daga jikin bango kuwa wani babban plasma tv ne da kuma Ac dake makale daga ɗaya gefen.
Sai kuma dining area, dake tsakiyar ɗakuna biyu wanda aka shirya dinning table mai kujeru shida, sai fridge da ɗan madaidacin show Glass da aka shirya cups, flack's, mugs, plate's, bowls, spoons da dai ababen buƙata, sai gefensu kaɗan da washing hands beby ke maƙale.
Daga gefen hagun dinning area ɗin kuwa,
wani daki ne da yakasance Library na musamman, domin babu irin littafin da babu acikinsa na addini, da kuma na karatunsa na Likitanci, had'i dana Pilot.
Baki ɗaya ɗakin cike yake da kanta, waɗan da, ke cike da littafai iri da kala, an jerasu tare da kimtsasu daki daki ko wanne sashin da abinda ya ƙunsa.
Daga tsakiya kuwa wani table ne dake zagaye da kujeru huɗu, sai AC dake ciki da yelwar haske.
Idan an fito Parlor kuma ta gefen dama wani ɗan madaidacin Corridor ne bisa alamu ɗakinsa ne.
Wani ƙasaitaccen gadone aciki wanda ya amsa sunansa gado na al'farma, yana kuma ke waye da abubuwan more rayuwa komai na ɗakin fari ne tas, kama daga kan gadon, labulaye, carpet had'i da da two cushions dake gefe suna d'auke da d'an k'aramin stool a tsakiyarsu, duk komai fari ne a d'akin sai ɗan ratsin golding color mai ɗan karen sheƙi da ƙyalli.
daga gefen gadon kuwa drawer'n kayansa ne daya cinye fiye da rabin bango sai kuma mirror dake facing gadon da suketa walwalin madubai dake maƙalle a jikinsu.

Tsakanin Libraryn sa da kuma bedroom d'in dining area wanda yake da step uku ana hudun zaka hau, daga gefen dining area akwai wata ƙofa ana buɗe kofar kuwa wani balcony ne wanda kana tsaye daga wajen kana iya hango farfajiyar wajen ta baya wanda ya kasance kamar Garden saboda shuke-shuke dake wajen bisa dukkan alamu wajen shakatawa ne wanda aka tanada saboda ma'aikatan wajen da kuma majinyata da ake bukatar asamar musu nutsuwa da kuma shauƙi da rage radadɗin ciwo da damuwar dake ɗawainiya dasu iya abin da yake cikin falon kenan.

Idan an sauk'o ƙasa kuwa daga cikin Corridor ta gefen hagu wani daki ne ciki da falo ne sai bathroom idan aka cigaba da tafiya cikin Corridor kuwa za'a hango wata babbar ƙofa dake facing shigowa.

Kusan baki d'ayansu atare suke murmurshi kana suna gyad'awa Addawa kai wacce keyi musu maraba lale cikin harshen Amharic wanda yake shine general language na Ethiopia dashi da Oromo.
Fuskarta d'auke da yalwataccen murmushi mai cike da aminci.
Ganin kamar basu fahimtar abunda take cewa ne kuma yasa ta juyawa zuwa harshen Fulatancin Ethiopia kana tana mai kare musu kallo tana son sanin su wayene saboda Tajj yace mata akwai baki na musamman zasu zo a karramusu Akuma

Mutuntasu.
shin wa'anan su waye ne ina Taj ya samosu shin me suke tafe dashi?.
Duk da wannan tunanin bai sa murmushin fiskarta ɗaukewa ba cikin mutuntasu ta cigaba da cewa.
“Bismillah ku ƙara so ga wajen zama”.
Ta ƙare maganar da nazartar fuskokinsu duk ba wacce ta gane a cikinsu.
Su kuwa kai suka gyada suna masu cigaba da kallon tamfatsetsen falon wanda yasha kayan ƙawa na more rayuwa komai na cikin wannan falon Blue Black da golden. kama daga Carpet Cottons da dai sauransu bisa duk kan alamu 3bedrooms ne a Falon daga gefen dama wani bedroom ne da aka kimtsa kana aka ƙawatashi sosai yayi kyau wanda bisa alamu na Ishmah ce daga gefen hagu shima bedroom wanda bisa duk kan alamu Dakin Addawa ce kusa da bakin Kofar shigowa nan ma bedroom ne bisa alamu ba kowa aciki da alamu Addawa, Laylah da kuma Zulaihat duk daki ɗaya suke.

Sai kuma dining area tsakanin dining area kuwa kitchen ne dake ƙawace da kayan ayyuka na zamani da sauƙaƙa ayyukan rayuwar yau da kullum, wanda duk wata ƴa mace zata buƙata daga cikin kitchen ɗin kuwa wata ƙoface da zata sadaka da Balcony iya tsaruwa ginin ya tsaru ta ko ina wajen sai ƙyalƙyali da ɗaukar ido yake bisa duk kan alamu komai na wajen sabone dal dan sai sheƙi da ɗaukar hankali...

Addawa kuwa cikin mutuntawa da sakin fuska ta k’ira sunan.
“Laylah da kuma Zulaihat”.
Da sauri suka amsa kana suka fito Laylah na kallon Garkuwa ta ware idanunta tare da ɗebawa da gudu ta rungumeta tana me cewa.
“Laaaa Aunty Garkuwa kece”.
Rungumeta Garkuwa tayi had’e da cewa.
“A'a Laylah yan mata”.
Cike da farin ciki Laylah ta saki Garkuwa ta rungume aunty Nana tana faɗin.
“Laaaa Aunty Nana ”.
Sai kuma ta maida kallonta ga Adam tare da cewa.
“Uncle Adam”.
Lokaci d’aya kuma ta maida kallonta ga Addawa still tana murmushi tace.
“Addawa su Uncle Adam ne fa”.
Da sauri ta kalli Khadija tace.
“Aunty Khadija ina Aunty Ishmah na!?”.
Murmushi Khadijah tayi tare da cewa.
“Aunty Ishmah tana tare da Uncle Taj”.
Tsalle Laylah tayi kana ta rungume Addawa tare da faɗin.
“Addawa munji daɗin mu Aunty Ishmah tazo”.
Sai kuma ta juya ta kalli Auty dake murmushi tana kallon yarinyar data shiga ranta Laylah kuwa cikin farin ciki tace.
“Aunty Garkuwa kun kawo mana Aunty Ishmah ko duka ko ta dawo wurinmu ko?”.
Kai aunty Amina ta gyaɗa mata tare da cewa.

“Eh sosai ma”.
Laylah kam cikin jin daɗi ta kuma riƙe hannun Addawa tace.
“Munji daɗin mu Addawa kinji an kawo mana Aunty Ishmah”.
Kallonta ta mayar kan Khadijah tace.
“Aunty Khady ina Aunty Rahama baku zo mana da ita ba?”.
Kai Khadijah ta jinjina tare da cewa.
“Ai mun kawo muku Aunty Ishmah ta dawo gidanku da zama, bazamu haɗa muku da Rahama ba Laylah kun rabamu da Aunty Ishmah dai ya isa”.
Cikin jin daɗi ta riƙa ƙyalƙyala dariya had’i da cewa.
“Alhamdulilah munji daɗi kuma in sha Allah sai mun sa Uncle Afif ya ɗauko mana Aunty Rahama ma ko Addawa”.

Fuska ɗauke da Murmushi Addawa tace.
“Aikam munji daɗi tashi ku kawo musu ruwa”.
Ta ƙare maganar tana kallon Zulaihat.
Kai Zulaihat ta gyada kana ta miƙe ta kawo musu ruwa, dasu drinks,snacks,fruits ta jere agabansu.

Kallon Aunty Amina Addawa tayi jin tana cewa.
“Tafiya dai ko yaya tana da wuya”.
Kasancewar da Fulatancin tayi maganar yasa Addawa ta fahimta kasancewar itama Bafulatanan Ethiopia ce cikin mutumtaka tace.
“Sosai ma kam gashi kuma na tsaidaku a falo baku samu kun shiga ba Zulaihat maza-maxa ku dauki kayayyakin su ku shigar musu ”.
Sai kuma ta maida kallon ta kan wanda adai-dai lokacin yake shigowa da jakankuna cikin alamun dan sanin juna tace.
“Bilal ka shigar da jakunkunan ciki kasa wasu ɗakin nan wasu kuma dakin can”.
Sai kuma ta Kalli Aunty Amina tare da cewa.
“Aunty Amina wasu su shiga ɗakin nan wasu su shiga wancan wasu kuma suzo nan”.
Kai Aunty Amina ta girgiza tace.
“A'a ai biyun ma sun ishe mu ai”.
Murmushi tayi tare da faɗin.
“Toh bari in kawowa Adam key”.
Ta faɗa tare da shiga dakinta Jim kaɗan ta fito ta miƙawa Adam key tace.
“Akwai wani ƙofa da yake kallo. Ƙofar dama ka buɗe ka shiga ciki”.
”Toh”.
Ya faɗa kana ya juya ya fita dai-dai lokacin suka miƙe aunty Amina,Goggo Dijah daƙi ɗaya suka shiga Aunty Nana, Garkuwa, Khadijah suma daki ɗaya suka nufa...

Koda suka shiga wanka suka farayi kana suka cac-canza kayansu kasancewar duk sunyi sallah acikin jirgi yasa suka fito falo bayan sun gama komai.
Ganin sun fito yasa addawa sauke ajiyar zuciya tace.
“Yawwa Bismillah ku iso dining tunda kuka zo ba kuci komai ba”.

Kusan baki ɗaya atare suka zauna a dining ɗin kallon Laylah Addawa tayi tare da cewa.
“Ɗauki ki kaiwa Uncle Adam”.
Kai ta gyada tare da ɗaukan Food flask, da kuma plate bowl spoon da aka jera acikin basket, ta nufi dakin Adam tana shiga ta sameshi zaune a Parlour bisa alamu yayi wanka ya shirya cikin Black jallabiya, cikin girmamawa tace .
“Uncle Adam ga abinci ”.
Kai ya gyada kana yace.
“Sannu Laylah”.

Acan gefen su Garkuwa kuwa sosai suka yaba da mutunci da karramawar Addawa bayan sun gama cin abincin ne kuma suka dawo tsakiyar Falon.

Sai alokacin Addawa tace.
“Yawwa yanzu sai mu gaisa ko?”.
Murmushi Goggo Dija tayi tare da cewa.
“Aidai kam sai mu gaisa tun da tun da muka zo bamu gaisa ba mun bige da cin abinci”.

Dariya Addawa tayi tare da faɗin.
“Ai dai kam matafiyi sai da abinci”.
Cikin mutumtaka da girmamawa suka gaisa bayan sun gama gaisawa tace.
“Na sani yau kam kun ɗebo gajiya ku shiga daga ciki ku samu ku huta in Sha Allahu muna nan tare zamu sha hira kam”.
“Toh shikenan”.
Suka faɗa tare da mik’ewa.

Aunty Nana ce ta kalli Aunty Amina tare da cewa.
“Aunty Amina nifa shiru har yanzu fa basu iso ba”.
Ɗan hararanta Garkuwa tayi kana murya kasa kasa tace.
“Ina ruwanki da jiran sai sun iso mata da mijinta tana tare da mijinta kice sai kin jirata taxo?”.
Murmushi tayi kana tace.
“Ai Yakamata dai mu san inda suke kuma gashi har yanzu basu zoba har zamu kwanta kallifa yanzu kusan ƙarfe biyun dare”.
Dariya Aunty Amina tayi mai haɗe da hamma tace.
“Um wannan dai damuwar kune”.
Ta ƙare maganar tana jan hannun Goggo Dijah suka wuce dakinsu...

Khadijah na dariya tace.
“Toh bari na gwada kiran Addah Ishmah ”.
3 missed calls tayi mata amma duk ba'a ɗaga ba.

Adai-dai lokacin kuma Taj ne zaune yana karatu kasancewar yana karatun da ɗan sautine yasa baiji vibrating ɗin da wayar Ishmahn keyi ba duk da yana gefensa.

Aunty Nana kam dariya tayi tare da zama abakin gadon tare da cewa.
“Hmmm ai waɗannan tsofaffin tuzuran sai dai Allah ya taro manasu nifa karfin halin Taj na gani, mutum shiru-shiru fa Ustaz-Ustaz naga mota tasha kwana hanya daban ko ina sukaje suka buya sai Allah watofa gani yake in munzo nan tare ba lallai ne ya samu matarsa kusa da shiba”.
Garkuwa na gyara kwanciyarta akan gadon da yasha shimfida na alfarma tace.
“Koma dai ina suka nufa matarsa ce ba ruwanki”.
Cikin dariya tace.
“Wallahi ji nake kamar in zama ƙuda in liƙu a jikin blanket nasu inga wainar da za'a to”.
Cikin dariya Garkuwa tace.
“Wato ke Bama a ɗakinba har cikin blanket kike son shiga”.
Dariya mai sauti tayi tare da cewa.
“Hmmm ba doleba zan samu ƙarin darasi Ishmah fa da kike ganin halittar soyyayace shiyasa duk wanda ya taɓa koda hiran sone da ita baya yanke alaƙa da ita dan gwanace a iya tattalin miji wani lokaci har Maryam tai ta mata tsiya tana cewa muda muke matan aure ba ma tattalin mazanmu da riritasu kamar yadda takewa Tajjj.
To kuma shima Tajj ɗin naga alamar Tattabarane shi kuma ɗawisu a fagen iya love ke kiga randa aka ɗaura auren mana da suka ƙule BQ sai Magrib suka fito”.
Sai kuma tayi shiru jin yadda Garkuwa keta dariya.
Hira kaɗan suka taɓa kana daga bisani suka kwanta su kayi bacci...

Washe gari da safe Ethiopia
Aminullah ne zaune agaban Ummi yayin da Abpu ke gefe idanunsa alumshe kamar mai bacci saidai ba bacci yake yi ba, bisa dukkan alamu breakfast suke.
Anutse Aminullah ya kalli Ummi tare da cewa.
“Ummi Aunty Ada fa?”.
Ummi na ɗan gyara zamanta tace.
“Aunty Ada na kirata amma naji tana waya da Izzin”.
Numfashi ya sauke kana yace.
“Ummi idan munyi Sa'a fa Allah ya kawo sauki,  baki ga tun randa mutumin nan yazo ya saki Aunty Ada har yau bata sake fita rawan nan ba”.
Cikin jin daɗi da alamun farin ciki tace.
“Nima abinda nake ta tunawa kenan Aminullah in Allah yaso ma sanadin sakin nan za tayi sanyi ta daina abinda take yi, kasan shi saki yanada zafi da kashe jiki da cushe zuciyar mutum koda ko yana son a sakeshin wannan alƙawarin Allah ne domin abinda zai girgiza al'arshin Allah ai ba wani zuciyar dake da kafircin da zai hanashi girgiza sai dai in bashi da ɗigon imani, gashi kuma tace min ta fadi ƙugunta ya bugu sosai”.
Cikin jin daɗi Aminullah yace.
“Allah yasa ta shiryu kenan”.
Ummi na Murmushi tace.
“Ameen ya hayyu ya ƙayyum Aminullah abinda muke ta fama kenan Allah ya shirya mana ita”.
Yana gyara zamansa yace.
“In sha Allahu ai Allah sami'uddu'a ne zai amsa mana addu'o'in mu, in Sha Allah watarana zamuyi farin ciki da rayuwar aunty Ada”.

Abpu da tunda suka fara Magana baice uffan ba ya buɗe idanunsa cikin rauni yace.
“Kayya ina wani shiryuwa awajen Adaya watakil ciwo ne kawai yasa ta lafa watakil kuma wani abu na daban take shiryawa wanda bamu sani ba”.
Ya kai ƙarshen maganar cikin rauni da takaicin halin data jefa rayuwar ta”
Da sauri Ummi tace.
“Kada kace haka in Sha Allahu Adaya zata shiryu kawai mu cigaba dayi mata addu'a ”.
Cikin sauri Aminullah ya karɓi maganar da cewa.
“Sosai ko Abpu addu'ar mu Aunty Ada ke bukata in Sha Allahu zata shiryu kada ka karaya”.
Murmushi mai ciwo yayi tare da cewa.
“Ina fatan haka ina rokon Ubangiji ya nuna min ranan da za'a ce Adaya ta nutsu ta zama kamilalliyar mace mai nutsuwa zuciya da jiki”.
Haka dai suka ci-gaba da tattaunawa.

*Nigeria*

Abbane zaune afalonsa yayin da Yah Muhammad, Yah Abubakar ke gefensa sai kuma Hamisu da yanzu ya shigo gefen Abba ya tsugunna.
Kansa Abba ya shafa tare da cewa.
“Ya dai Hamisu?”.
Kansa ya gyaɗa kana yace.
“Lafiya lau Abba?".
Cikin kaunar su Abba yace.
“Ya kewar Boɗɗi?”.
Cikin sanyi da kuma rauni yace.
“Abba akwai ina kewarta gidan ba daɗi ji nayi kamar na ƙaura".
Cikin sauƙe ajiyar zuciya da kewar ɗiyarsa Abba ya saki nannauyan ajiyar zuciya kana ya kwantar da kan Hamisu kan cinyarsa tare da cewa.
“Toh ina zaka kaura inda yafi nan Hamisu? Ai duk duniya babu inda zaka je inda yafi nan. In Sha Allahu zamu saba ai abin farin cikine ya samu Addarka. Aure tayi fa sunnar ma'aikin Allah abinda muke mata fata tsawon shekaru kai kafi son ta zauna anan tare damu ba tayi Aure bane?”.
Kai ya girgiza kana yace.
“A'a Abba bana fatan haka.
Hakan shine abu mafi a'ala in Sha Allahu zan yi ta addu'a Allah ya bata zaman lafiya acikin rayuwar aunrenta”.
Atare Abba Yah Muhammad,Yah Abubakar suka amsa da Ameen.

*Qatar*.

Baki ɗayansu zaune suke bayan sun gama breakfast tare da kimtsa wa sai Adam ne dabai nan wanda suka fita tare da Bilal.

Murmushi Addawa tayi tare da kallonsu tace.
“Toh nima dai tun juya nake kiran Afif bai ɗauka ba gashi Ni kaina na matsu ya kawo min Ishmah kuma shiru dai har yanzu”.

Dariya Aunty Nana tayi tare da cewa.
“Hmmm ai muma mun kira Ishmah Addawa ba'a ɗauka ba wannan dai sai mu zubawa sarautar Allah ido.
Allah andi inda suka ratsa”.
Dariya Khadijah ta sanya tare da cewa.
“Allah dai yasa ba ƙasan suka bari ba”.
Murmushi Addawa tayi kana tace.
“Ya isa ya bar ƙasar da ita bai kawo min ita mun gaisa ba?,Ko zai bar ƙasar ai sai ya kawota mun gaisa”.
Cikin sauri Goggo Dijah ta ɗan zare idanu tace.
“Toh ma sai ya iya barin ƙasar da ita toh su tafi ina?”.
Zama Addawa ta gyara tace.
“Duk inda tace masa tana son zuwa zai Kaita in dai Tajju ne".
Kai ta jingina tare da faɗin.
“Lallai dai kam”.

Adai-dai lokacin kuwa a hotel ɗin da suka sauƙa Ahankali Ishmah ke ɗan jujjuya Idanunta cikin ɗakin jikinta sanye da bathrobe fari kanta naɗe da towel wanda shima ya kasance fari bisa duk kan alamu yanzu ta fito wanda.
Ahankali ta shaƙi numfashi tare da shaƙan daddaɗan ƙamshin da jikinta ke fitarwa buɗe idanunta tayi kana ta lumshe aranta tace to ina na wurga hand bag ɗina juyawa tayi ta kalli kan gadon kana ta maida idanunta tsakiyar falon still babu, numfashi ta fesar asaman Lips ɗin ta murya araunace tace.
“Toh bari in duba falo ko acan na bari in ɗauko brush in samu inyi, nayi wanka kuma bazan iya brush da wannan brush d’in nasu mai laushi kamar na jariraiba”.
Ahankali ta ɗan tura ƙofar ta leƙa ganin ko Taj na falon.

Jin Parlourn shiru alamun ba kowa sai sanyin Ac dake ratsa ko ina sai kuma wuta dake kunne wanda ya bawa falon wani haske na musamman da yayi masifar kyau yana sheƙi ahankali ta fito saɗaf-saɗaf ta nufi inda ta hango jakarta akan 2sitter tana buɗe hangbag taga Maclean da brush ɗinta da ta saka, ajiyar zuciya ta sauƙe ta kana ta ɓare ledan brush ɗin ta zato brush ɗin tare da matsa Maclean ɗin juyawa tayi zata koma bedroom sai kuma ta tsaya jin kamar motsin mutum agefen hagunta da sauri ta zira idanunta kan labulayen cikin sauri mai haɗe da tsoro ta zare idanunta muryanta na ɗan rawa tace.
“Waye?”.
Shiru ba wanda ya amsa ahankali ta nufi wajen ganin yanda labulayen keta motsi kamar mutum ne a ciki, saɗaf-saɗaf ta isa wajen sai kuma ta tsaya cikin sanyi tace.
“Taj”.
Sai kuma tayi shiru ganin har zuwa lokacin labulayen na motsi ahankali ta sanya hannunta ta ɗaga labulayen da sauri ta saki sanyayyan ajiyar zuciya ganin ƙoface awajen kana iskane ke kaɗa labulen, wanda tayi zaton Taj ne zai gwada tsoronta, ahankali ta riƙe Handle ɗin tare da murdawa ga mamakinta taga ya buɗu cikin sanyayyan sauti tace.
“Wowww Masha Allah”.

Ta kare faɗan Masha Allah ɗin tana ƙarasa fitowa kan ɗan baranda dake zagaye da ƙarafunan silver, a huta isa kusa da ƙarafun, kana tasa hannayenta ta dafa ƙarfen da aka yiwa Farandar garkuwa dashi idanunta ta lumshe tare da tsira wajen daya fi kama da akira sa da forest dan yafi karfin akira da garden saboda subiruni ne da kuma tsirran da suke bakin kogi wanda akanshi akayi Hotel ɗin duk inda ta ƙyalla idanunta kore ne shar da wani iska mai masidar daɗi dake busawa wanda ke sanya nishadi..
Wani irin shauƙi da farin ciki na musamman take ji wanda yake ratsa sassan jikinta da zuciyarta lumshe idanunta tayi tare da sanya brush ɗin abakinta batare data fara gogawa ba.

Dai-dai lokacin kuma Taj ya buɗe kofar falon ya shigo bayansu kuwa home Deleviry daya kawo musu breakfast ne suna shiga ya nuna masa kan dining ɗin falon alamar ya ajiye abincin akai wanda abinci da sukayi order ne yana ajiye wa ya juya ya fita.
Taj kuwa har ya nufi bedroom ya hango alamar Kofar abuɗe yake ahankali ya nufi Kofar.

 Yana isa yasa hannunsa ahankali ya ɗan ɗaga labulayen.

Idanunsa ya sauƙa akan Ishmah data juya baya tana kollon forest ta ɗan Dafa jikin karafunan kana ta ɗan jingina kadan da jikin ginin sam bata ji motsinsa ko alamarsa ba.

Ahankali ya ƙara sa shiga dai-dai bayanta ya tsaya Anutse ya sanya hannunsa ya zagaye dai-dai kan ƙugunta.

Cikin sauri da tsoro ta ɗago kanta ta kallesa ta gefe wanda ya bawa bayanta damar mannuwa da ƙirjinsa a hankali ɗaya ta saki sanyayyan ajiyar zuciya ganin shine dan da farko ta tsorata.

Kanshi ya ɗan zuro ta gefen fuskarta tare da ɗan manna sajenshi da gefen fuskarta ta murya can ƙasan maƙoshinsa a hankali yace.
“Afwan na baki tsoro ko”.

Sassayan numfashi ta fesar tare da ɗan lumshe idanunta tana mai jin yadda ni'imtaccen sanyi ke ratsata ga kuma ƙamshin jikinsa.

Taj kuwa hankali ya murza hannayensa tare da murza ƙugunta ya juyo da ita  suna fuskantar juna har lau kuma hannunta na kan Brush ɗinta.
Ahankali ya sanya hannunsa dai-dai haɓarta na dama, gefen fuskantar ya ɗan shafa tare da ɗan sayatsunsa biyu yana ɗan shafa sajenta tare da ɗan kwantar dashi, sassayan numfashi suka fesar a tare, sai kuma duk suka ɗan tsaida idanunsu cikin na juna.
A hankali ya ɗan kamo kunnenta kaɗan ya shafa zuwa ƙasan habarta cikin wani irin yanayi ya tsira mata idanu yana mai sakin sanyayyan numfashi.
Itama Ishmah idanu ta tsira masa tana mai jin wani abu mai masifar nauyi yana fita daga cikin ƙwayar idanunsa zuwa nata.
Cikin wani irin yanayi Taj ya saki nannauyan ajiyar zuciya, sai kuma yasa hannunsa na dama ya

zaro brush ɗin daga bakinta.
Ido ta ɗan lumshe kana ta buɗe.
Shi kuwa ɗan murmushi gefen baki yayi tare da sanya broch ɗin cikin bakinsa.
Ɗan wara idanunta tayi kana muryanta can kasan maƙoshi mai cike da shauƙi da kuma sanyi ta fesar da numfashi laɓɓanta ta motsa tare da cewa.
“Brush ɗina kuma kasa abakinka?”.
Idanunsa ya tsayar akanta batare da yace komai ba yana dan motsa hannunsa kamar yana goga Brush ɗin murmushi tayi cikin mmkin lamuransa, shi kuma cikin jin sanyi a rai ya ɗaga mata girarsa ɗaya tare da zaro Brush ɗin daga bakinsa.
Ahankali ya motsa Lips ɗin sa alamar ya ɗan tsosti zaƙin brush ɗin da kuma garɗin yawunta.

Cikin sakin sanyayyan Murmushi mai haɗe da wani irin shauƙi na musamman ta fesar da iska mai sanyi tace.
“Ka bani tsoro”.
Fuskarta ya shafa yana mai jin wani irin yanayi na musamman atare dashi yace.
“Farar kura ga tsoro ga ban tsoro”.
Ya ƙare maganar yana haɗe yawunsa daya haɗe da zaƙin makilin da garɗin yawunta.
Sai kuma yasa hannunsa na dama ya tallaɓe fuskantar ido ta tsira mishi shima tsira mata nasa yayi, da sauri ta lumshe nata saboda ganin ya haɗe bakinsu wuri ɗaya.
“Yah Salam wai ni kam  me lips ɗina sukayiwa  Tajj”.
Tayi mgnar zuci sabida jin yadda yakeyiwa lips inta wani irin fitinenne lasa kamar ya samu lollypop”.
Sai kuma tayi saurin zamewa daga gareshi tare da juyawa tana kallon Forest ɗin still fuskarta na ɗauke da Murmushi.
Sake matsar da ita jikin ƙarafunan yayi   kana yasanya hannunsa ya shafa lafeffen cikinta cikin sanyi sauti yace.
“Jiya ba kiyi Lunch ba gashi yanzu har kusan ƙarfe goma bakiyi breakfasts ba, muje Kiyi in baki abinci, kada Ulcer ta illata min ke”.
Cikin lumshe idanu da yanda hannunsa ke yawo asaman cikinta ta saki sanyayyan numfashi tare da faɗin.
“Toh”.
Kana suka fito falon ƙofar yaja ya rufe.
Ishmah kuwa kai tsaye bedroom ta wuce tana shiga ta wuce bathroom tayi brush tana fitowa ta ganshi tsaye.
Cikin lumshe idanu tace.
“Ya dai?”.
Da hannu ya nuna mata durowa dake cikin dakin yace.
“Ga kaya acikin nan ki saka”.
“Toh”.
Tace dama aranta tana tunanin wani kaya zata saka.
Shi kuwa Taj juyawa yayi ya fita kana ita kuma ta buɗe durowar ɗan wara idanunta tayi tare da faɗin.
”Wow Masha Allah”.

Ganin kayan dake shaƙe ajiki an shiryasu gwanin ban sha'awa wanda bisa duk kan alamu dogayen rigunane masu masifar kyau da sheƙi.
Sai kuma wanduna masu kamar Palazo da top wanda suma suke shirye gefe ɗaya sai kuma takalma wanda mafi akasarin su Snickers ne da hill masu shegen tsini.
Murmushi tayi aranta tace lalle ma Taj zan iya tafiya da wannan takalmin ne ahankali ta zaro wata tattausar abaya mai laushi ƙiran samfurin Qatar Abayas Maroon color ta ɗaura gefen gado sai kuma taja drawer ƙasa nan kuma Undoies ne kama daga Brassier, Pant, Skin tied, Boxer na mata, da dai sauransu ahankali ta zaro Brassier cikin mamaki ta wara manyan Idanunta tare da jujjuyawa asaman Lips ɗin ta tace.
“Ya akayi Taj yasan Size ɗin Brassier na?”.
Ta ƙare maganar cikin matsanancin mamaki ganin gaba ɗaya Brassier size ɗin ta ya sayo sai kuma ta janyo Pant cikin sauri ta rufe fiskarta ganin su manya-manyan aranta tace ya akayi Taj yasan har size ɗin Pant ɗina ahankali ta zaro Pant da Brassier duka farare ta ajiye kana ta ɗauki Skin tied ta sanya ta kimtsa kanta tare da komawa cikin Weldrop ta dauki turaruka masu daɗin ƙamshi kana ta fito.

Akan dining ta same sa already yayi serving abinci.
Ganinta yasa ya mike tare da jan hannunta ya zaunar da ita akujeran dake facing dinsa kafin shima ya koma ya zauna.
Yana zama ya miƙa mata fork ɗin abincin.
Ajiyar zuciya ta sauke kana ta karɓa ganin acikin abinci akwai cheaps yasa ta sauke numfashi tasan ko bata iya cin saura ba zata iya cin cheaps ganin ya zuba mata idanu yasa ta lumshe Idanunta cikin langwaɓar da kai mai sanyi gami da rauni tace.
“Toh kaima Kaci mana”.
Cikin sanyi yace.
“Nafi bukatar naga ke kinci shine babban matsalata inga kin daina zubda hawaye sannan kina cin abinci shine abinda zai iya samin farin ciki arayuwata”.
Numfashi ta fesar muryanta cike da sanyi da kuma rauni tace.
“Toh yanzu ina yin hawayene?”.
A hankali ya ɗan daura rafin hannunshi kan sajensa yana ɗan shafawa tare da cewa.
“Ko ba kiyi yanzu ba kinyi daren jiya kuma har yanzu ga idanuki akumbure alamun yau da safe ma kafin kishiga wanka kinyi”.
Ya ida maganar yana kallon yanda Idanunta sukayi luhu-luhu dasu .
Shiru tayi batare da tace komai ba.
Muryar can kasan maƙoshi yace.
“Kinyi ko?”.
Kanta ta girgiza alamar batayi ba,
langwaɓar da kai yayi tare da cewa.
“Kinyi mana faɗa min gaskiya?”.
Idanunta ta lumshe tare da buɗewa tace.
“Toh ai ɗazune da nayi waya da Hamisu gaba ɗaya yasa Naji nayi kewan gida yana cewa gidan mu ba daɗi ”.
Murmushi yayi kana yace.

“Ina ga zan hanaki yin waya da Hamisu ”.
Da sauri tace.
“Kayi haƙuri”.

Cikin ɗan murmushi da langwaɓar da kai yace.
“Toh ai yana samun ke kuka.
Ni kuma bana son abinda zai saki kuka ”.
Baki ta ɗan tura cikin shagwaɓa da rauni tace.
“Toh Kaci abinci mana”.
Kai ya girgiza mata alamun bazaici ba.
Cikin kwaɓe fuska tare da ɗan ture plate ɗin gabanshi tace.
“Nima bana son cin sannan kuma nima Taj”.
Sai kuma tayi shiru Idanu ya tsira mata yace.
“Kema me?”.
Kallonsa tayi sai kuma ta sunkuyar da kai.
Ahankali ya sake motsa labɓansa yace.
“Kuma me ki faɗa min”.
Batare data kallesa ba tace.
“Kuma mai ya hanaka bacci da daddare?”.
Kansa ya sunkuyar cikin rauni da sanyi yace.
“Bana jin bacci.
Bacci ya ƙauracewa idanu na Ma'eeshah na rasa yanda akayi bacci ya ƙini bansan ya za'a yi in samu inyi bacci ba”.
Cikin sauƙe numfashi da tarin tausayinsa tace.
“Baka da lafiya ne?”.
Kai ya girgiza mata zazzafan Ajiyar zuciya ta sauke tare da cewa.
“Ka faɗa min mana”.
Araunane yace.
“Nima ban sani ba Ma'eeshah”.
“Toh Ni dai Kaci abinci”.
Ta ida maganar tana miƙa masa fork kusan tare suka ci abinci.

Jim kaɗan da gama cin abincin su,
su kaji ana knowking miƙewa yayi ya buɗe kofar ganin Dr Amdaz ne yasashi ɗan sakin fuska tare da mishi sannu da zuwa.
Cikin alamun sabo da shaƙuwa da alamun yawan magana Dr Amdaz yace.
“Barka da safiya Dr”.
Anutse Taj ya amsa tare da bashi hanya.
Sai kuma ya maida kallonsa kan Ishmah tare da cewa.
“Ma'eeshah tashi ki shiga ciki”.
Kai ta gyada tare da mikewa Akuma dai-dai lokacin Dr Amdaz ke cewa.
“Barka da safiya Amarya”.
“Barka dai Dr”.

Ta faɗa tare da shiga bedroom...

Dr Amdaz kuwa kallon Taj yayi kana yace.
“Dr naxo da duk Doctors ɗin fa ”.
Kai ya jinjina tare da faɗin.
“Ba matsala ka shigo dasu ai zama zamuyi dasu gaba ɗaya ne za muyi meeting ɗin”.

Fita yayi jim kadan ya sake shigowa mutum tara na biye dashi shida daga ciki maza ne sai mata uku. shine cikon na goma suna shiga suka zauna a Falon.
Dr Amdaz kuwa gefe sa ya zauna tare da cewa.
“Wa'annan sune manyan Doctors ɗin mu ko wanne da fanni daya karanta akwai Brain Dr, Skin Dr, Eyes Dr, Teeth Dr, heart Dr, ko wanne problems muna da Dr'nsa da kuma magungunansu maganinsa.
Kai Taj ya jinjina cikin gamsuwa yace.
“Masha Allah”.
Dr Amdaz kuwa zamansa ya gyara tare da faɗin.
“Dama nace yau kayi zama da Dictors gobe kuma Norse's.
Sai Jibi kuma in Allah ya kaimu kayi zama da Cleaners da sai sauransu”.
Cikin gamsuwa Taj ya jinjina kansa kana yace
“Eh hakan ne yayi abi komai step by step”
Daga nan suka Cigaba da tautauna sauran abubuwa daga bisani ya ɗauki key ɗin office da muhallin ko wani Dr ya basu tare da tsaida ranakun zuwansu da lokaci da kuma dakarun su daya kasance mai gwaɓi, ya ƙara da faɗin satin firko da zasu fara aiki komai kyautane zasuyi duk nauyin ciwo da maganin da zaici.
Sosai sukaji daɗin haka mussaman da suka kasance duk musulmaine sai biyu daga cikine ɗaya ba India ne da addinin hindu ɗaya kuma ahlul kitab ne, wanda da kyar Amdaz yasashi ɗaukarsu sabodo kwarewar su da kuma nuna mishi ai zasuyi fatan su kasance tare dasu su zama sanadin musuluntarsu.
Cike da jin daɗi sukayi godiya kana suka ci gaba da tattaunawa da yadda zasu tallata asbitin..

Acan gidan Addawa kuwa da yammaci suna zaune Garkuwa ce da Aunty Nana suka kalli Addawa jin tana cewa.
Zulaihat tashiga kitchen tayi musu girki.
Murmushi garkuwa tayi tare da cewa.
“Addawa bari mu shiga mu taya ta girkin ai abin ya mata yawa ita kaɗai take ta fama”.
Addawa na gyara zama tace.
“Zata iya ai Zulaihat nada ƙoƙarin”
Zulaihat na gab da shiga kitchen tace.
“Allah Aunty Ku huta”.
Khadija na miƙewa tace.
“A muje dai na tayaki”.
Aranta tace gwara dai muje mu ga abinda za'a mana Kada ayi mana abincin Larabawa ko na Amharic wanda ba lallai mu iya ciba.

Daga nan suka shiga kitchen kana su kuma suka ci-gaba da hiransu.

Aunty Nana dake ƙoƙarin kunna gas tace.
“Wai ni har yanzu ba wanda yayi waya da Ishmah?,”.
Khadijah na ɗauraye tukunyar tace.
“Wai ke me matsalar ki da sai kinyi magana da ita na rasa mene matsalar ki yanzu fa da da ba ɗaya bane da in kina tunanin cewa Ƙanwar mijinkine tana zaune agida yanzu fa matar Aurece kuma gurin mijinta take”.
Adai-dai lokacin kiran Ishmah ya shigo wayar Aunty Nana murmushi tayi tace.
“Ƴar halak kinƙi ambato”.
Ta kai karshen maganar tana amsa kiran tana ɗauka tace.
“Ohhh Ikon Allah yanzu dan Allah dan Annabi Ishmah ina kika shiga tunda muka zo ba amo ba labarinki.
Kinje kin rungumi mijinki kunyi shiru wannan abu har ina daga ke har Taj ɗin kun bani kunya".
Cikin sanyi Ishmah tace.
“Wallahi nikam ba ruwana dan ko yatsana bai riƙe ba har da cewa wai na rungumi miji ance Miki ni irinki ne!?”.
Dariya Aunty Nana tayi tare da faɗin.
“Ai dake irina ne da tare zamu zauna kawai sai naga mutum ya canza hanya da ban toh yanzu ina kuke?”.
Cikin sauƙe numfashi ta faɗa mata sunan hotel ɗin da suke.
Aunty Nana na dariya ta juya ta kalli Garkuwa tare da cewa.
“Kin gani ko Garkuwa wai fa a Hotel suka sauka yanzu yaushe zaki dawo?”.
Ahankali Ishmah ta girgiza kai tare da faɗin.
“ Nima ban sani ba Aunty Nana anma anjima idan ya shigo zan baki ki tambayeshi”.
Dariya Garkuwa ta sanya kana tace.
“Madallah kinyi min naganinta”.
Kana ta karbi wayar suka ci-gaba da hira...

Aranar dai haka Taj ya yini tattaunawa da Likitocinsa koda suka gama ranar ma haka ya kwana kamar jiya baiyi bacci ba Ishmah kam bacci take shi kuma yana zaune bakin gadon yana karatu idan ya ɗan gaji da zaman yayi nafila haka nan zuciyarsa ta gaza amsar hukuncin Yah Abana ji yake yi ya rabashi da dukkan farin cikinsa a hankali ya ɗan juyo ya kalli Ishmah da ta ɗanyi juyi tare da matsowa gab da bakin gadon murya cike da bacci tace
“Tajj kayi bacci”. Sai kuma ta ƙare maganar tare da kife kanta alamun cikin bacci tayi mgnar kuma baccin ya kuma danneta, sassayan numfashi ya fesar tare da gyara zamansa ganin fuskantar a kusa dashi a matsayin matar sa kaɗai ne ke sawa yaji zuciyarsa ta ɗan samu sassaucin tarin damuwarsa da ta kauda dukkan shauƙin jiki da zuciyarsa gami da ruhinsa....

Washe gari da safe Ethiopia.
Meymer ce zaune gaban Momynta.
Cikin tsuke fuska Momyn Meymer tace.
“Toh Meymer kin dai yi abinda kike so”.

Cikin matsanancin kuka da zubda hawaye tace.
“Momy me nayi?,dan Allah ki daina cewa nayi abinda nake so”.
Cikin takaici tace.
“Meymey kin sani na sani kinyi abinda kike so Afif ya sake ki ko?”.
Kai ta gyada cikin gamsuwa da jin daɗi tace.
“Eh”.
Cikin rashin walwala tace.
“Shawar da zan baki ki fara Istigfari kafin Sakayya yazo ko Ubangiji zai kawo Miki Sakayyan da sauƙi”.
Da sauri tace.
“Wallahi Allah Momy ba abinda nayi mishi Momy abinda ya aikata fa aka faɗa banyi masa ƙazafi ba”.
Cikin tarin takaici Momy tace.
“Ni dai ban nemi ƙarin bayani ba, abinda zan faɗa Miki ki kama kanki ki riƙe kanki da Dr Zakariyya duk abinda zakuyi sai ki bari sai kin gama Iddah kafin ku fara maganar Aure”.
Cikin sauri tace.
“Momy nifa babu Iddah akaina tunda mu kayi Aure da Yah Afif ko hannuna bai taɓa riƙe wa ba”.
Wani kallon takaici Momy ta watsa mata kana tace.
“Ni dai ban nemi wani bayani ba kawai kiyi zaman Iddah kafin kuyi aure da Dr Zakariyya dan nasan shine aranki”.
Ta ƙare maganar tana mai jin takaicin rabuwar Auren Afif da ƴarta...

Acan gidansu Adaya kuwa Ummi ce da Aminullah tsaye a falo bisa alamu aike ta yiwa Aminullah yanzu ya kawo mata cikin mamaki ta buɗe ido ganin Adaya ta fito tana tafe cikin rausayawa bisa duk kan alamu zata tafi Reharzal ne cikin tarin takaici da bakin ciki ya kalli Ummi itama Ummi kallonsa tayi .
Cikin jujjuya kafada da jijjiga ƙirji tace
“Toh Ummi na tafi ”.
Cikin tarin takaici da Mamaki tace
“Ina zakije Adaya?”.
Ɗan wara idanunta tayi tare da faɗin.
“Ummi kin manta kwana biyun nan ƙuguna da yake ciwone yasa ban samu na naje Reharzal ba yanzu fa wata biyu ne fa kacal ya rage mu tafi India gasar rawa Ummi ki tayamu da addu'a”.
Cikin tashin hankali Ummi tace.
“Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un dama har yanzu Adaya wannan gasar rawar yana ranki”.
“Eh mana Ummi ”.
Ta faɗa tare da ficewa a falon.
Cikin kunci da tarin damuwa Aminullah yace.
“Badan ciwo ba daɗi ba da nace ciwon daya. dami Aunty Adaya ya dawwama ajikinta har Abada saboda ta nutsu ta daina abinda takeyi”.
Cikin sanyin jiki da karaya da lamarin Adaya Ummi ta zauna kan kujerar tare da dafe kanta da hannunta duka biyu.

Adaya kam tuni ta fita tana isa hall ɗin da suke Reharzal ɗin duk suka miƙe tsaye saboda jin an saki wani irin....
*Kunsha typing errors dan banyi editing wannan page ɗin ba*

*BY*
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 📝🕋💉🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*INDA RAI*

*BOOK 2 PAGE 3*
*AYASHA ALIYU GARKUWA*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*Lockpage*

Ido suka zuba mata cike da farin ciki Aunty Nana ta juyo ta kalli Garkuwa dake murmushi sai kuma ta kalli Ishmah dake raɓa gefenta, kai a sunkuye tana tafiya ne cike da sanyin jiki da kaɗuwa da dukan ba zata da kalmar aurenta ya saki mata, gami da raunin da ganin Taj a cikin yanayin da yasa har yanzu hawayenta basu tsagaita zubar da sukeyi ba.
Cikin sanyi Aunty Nana ta ɗan jujjuya kai, tare da ɗan juyawa ta nufi hanyar fita saboda haka nan taji rauni yana diro mata.

Ita kuwa Ishmah tana shiga bisa gadonta ta faɗa tare da sakin sassayan kukan da yaƙi dannuwa.

Da sauri Garkuwa ta biyo bayanta.
A gefen ta ta zauna tare da kamo hannunta ta tada ita zaune, cikin sanyi da tausasa zuciya tace.
"Haba dai Ishmah, wannan shine irin godiyar da zakiyiwa Allah? Hakan bai cancanci nagartaciyar mace irinki ba, ki sani fa ɗan adam baya tsallake ƙaddararsa, kuma duk managarcin musulmin da ya cika mumuni na gaske, amsar ƙaddara yakeyi a duk san da tazo mishi, a kuma duk yanayin da yazo mishi."
Sai kuma ta ƙare maganar tare dasa hannunta ta jawota tsaye.
"Shiga kiyi al'wala kizo kiyi salla, ki godewa Allah da ni'imar da yayi Miki, na mallaka Miki miji mafi daraja da tsada a cikin mazaje, miji irin wanda ko wanne uba yakewa ɗiyarsa fata da

addu'ar sumu.
Ishmah ki sani fa cewa Allah yayi Miki ni'imar mafi ƙololuwar ɗaukaka, ni'imar samun mallakar Sheykh Afif Muhammad Taj a matsayin mijin aurenki, Kin fini sanin waye Taj domin kece mace mafi kusanci dashi a duniya, harma da mahaifiyarsa tunda yanzu zaki rayu a ƙarƙashin inuwar aurenshi, zaki zame mishi sutura, zai zame miki sutura, kana garkuwanki"

Wasu irin tafassasun hawayene masu tafe da tsananin tsoron Allah da girgiza da girman ikonsa da ƙudurarsa, wai yau itace Aisha Ishmah ake kira a matsayin matar Taj ya Salam.
Shine kaɗai abinda ta iya cewa.
Dai-dai lokacin kuma Aunty Amina wacce take ƙanwa ga Daddy, ta ɗan juyo ta kallesu lokacin da ta fito daga bathroom bisa alamu al'wala tayi.
A hankali ta matso kusa dasu tare da tallafe habar Ishmah tana faɗin.
"Mu yau duk faɗin family d'in mu, cike muke da tsananin farin ciki da bazai misaltu ba, saboda haka dan Allah kada ki raunata mana zuciya shiga kiyo al'wala".
Kai ta jinjina tare da juyawa ta nufi Bathroom ɗin.
Bayan tayi al'walan ta fitone itama Garkuwa ta shiga tayi.

Bayan sun idar da sallan isha'i zaune suke a tsakiyar Parlour kowa da abinda ke gabanshi.

Cikin kulawa Garkuwa ta ƙara turo mata plate ɗin da ta zuba mata dungulen zabuwar.
"Dan Allah ki cinyeta, dan so nake inga kin cinyeta kafin Oga yazo, dan yace yau da kansa zai-zo ɗaukata dan yana son yayi wa Abba murnar auren Boɗɗinsa".
A hankali ta ɗan kalli plate ɗin wanda ta ci kusan rabin zabuwar, fork ɗin hannunta tasa, tare da ɗan sabulo tattausaar tsokar da magunguna suka sa tayi baƙi, ido ta rufe lokacin da ta kai tsokar cikin bakinta.
"Ai nima yau bazan tafi ba, sai ta cinyeshi".
Cewar Aunty Hauwa.
Fuska ta ƙwaɓe cike da rauni tace.
"Cikina ya cika fa".
Kai Aunty Amina ta gyaɗa tare da cewa.
"Ba matsala Garkuwa bata damun tasha, anjima kan mu tafi zata ƙarasa zabuwar".
Ta ƙare maganar tana kai cup ɗin ruwa bakinta.

Aunty Maryam da yanzu ta shigo ne tace.
"Ai kada ku damu a barmin wannan aikin, ni daɗi nake ji inga na tisa mutun a gaba yasha magani".
Cikin sanyi da ya gaza barin ruhi da jinkinta tasa hannunta ta amshi kwanon Ƙasaitacciyar mace da yake ɗauke da damun.
Lumshe idanunta tayi domin sosai damun yayi mata daɗi a bakinta sai dai, ina cikinta ya cika rabi tasha kana ta ajiyeshi.
Tana hamdala domin tun safe bataci komai ba.

Ƙarfe tara dai-dai duk ummomin ta suka tafi, bayan sun jaddada wa Garkuwa ta bata ta cinye

sauran.

Ƙarfe goma dai-dai, Oga ne, zaune da Abba a falonshi tare kuma da Taj.

Sosai sukayi hira daga bisani.
Sheykh ya kira Bobbuga rumbun Abboi ɗinsa ta fito su tafi.

A hankali ta sauƙe numfashi tare da cewa.
"Yauwa yanzu dai hankali ya kwanta tunda kin ƙarasa kazar, kin shanye damun kuma".
Cikin sanyi Ishmah ta ɗan shafa cikinta da bazakace a ciki zabuwar nan da damun nan sunka samu muhallin zamaba.
Sai kuma ta ɗan kwaɓe fuska jin Garkuwa na cewa  Maryam.
"Akwai kuma haɗin jan Nama dama na dafa mata, yana cikin fridge da safe ki ɗumashi sai ki bata ta cinye, garukan nan kuma dasu tsumi, sau uku zata rinƙa sha safe da yamma, da rana".
Da sauri tace.
"Toh wannan kam sune zasu zama abincina ko yaya, zasuyi min yawafa Aunty Garkuwa".
Murmushin tayi tare da ɗaukar mayafinta tana yafawa tace.
"Ai haka nakeso suyi miki yawan, Sheykh Afif ya banbance tsakanin aya da tsakuwa."
Tana gyara mayafin jikin ta, ta fara binta a baya ganin ta nufi hanyar fita tana faɗin.
"Toh Maryam na barku, da aiki.
In sha Allah zuwa jibi kuma zan turo mata dahuwar zuciyar farin rago."
Suna fita Maryam tace.
"Kada ki damu, mun gode sosai a gaida gida".

A hankali suka iso harabar  gidan.
Tsaye suka samu Oga da  Taj.
A hankali suka ƙaraso kusa adasu dai-dai lokacin da Sheiykh  ke cewa.
"Wannan ba matsala in sha Allah, zanyiwa Capting Sadik sale mgna akan visa ɗin, masu rakiyar tunda nasan na ango da amarya kam can ne zasuji daku".
Cikin sanyi Taj ɗin ya bashi hannun tare da cewa.
"Amman dai za'a bamu aron Garkuwa ko, tayi mana rakiya".
Da sauri duk suka kalleshi jin yana faɗin.
"Kai kuyi haƙuri bazan iyaba".
Cikin sanyi Taj ɗin yace.
"Haƙuri zakayi".
Yana ɗan murmushi yace, .
"To yanzu dai bari muji ta bakin Sadik ɗin muji ko zaku samu visa ɗin, duk yadda mukayi dashi zakaji ni".
Ya ƙare maganar tare da bawa Taj ɗin hannunsa sai kuma ya ɗan juyo ya kalli Ishmah dake gaidashi yace.
"Barka dai amarya, Allah ya sanya alkhairi yabada zaman lafiya".

A tare Taj da Garkuwa suka amsa, ita kuwa Ishmah ƙasa tayi da kanta tare da ɗan kaɗa kanta

jin Garkuwa dake shiga motar nace mata.
“To sai da safe, zamuyi waya”.

“Allah ya bamu alkhairi”.
Amin suka amsa kana yaja motar suka tafi.

A hankali ta ɗan juyo ta kalleshi, da sauri tayi ƙasa da kanta ganin shima ɗin ita yake kallo.
Cikin sanyi murya tace.
“Ya ƙafarka?”.
A hankali ya ɗan matso kusa da ita, murya can ƙasan maƙoshinsa yace.
“Alhamdulillah”.
Ya faɗa tare da ɗan ƙara matsowa jikinta.
Sai kuma ya ɗan jujjuya kanshi yana ƙarewa harabar gidan kallo ba kowa.
Hannunshi yasa ya jawota jikinsa sassauƙan rugguma yayi mata tare da ɗan manna lips inshi kan goshinta ya dire mata sassayan kiss murya can ƙasan maƙoshinsa yace.
“Ki yafewa Tajj ɗinki Ma'eesha”.
Cikin sanyi ta ɗan lumshe idanunta kana ta buɗesu a hankali. Sai kuma ta ɗanyi saurin matsawa baya, saboda hango Yah Muhammad.
A hankali ta nufi cikin gida.
Shi kuwa Taj BQ ɗin ya wuce shida Yah Muhammad.

Washe gari da safe, cike suke a Parlour Daddy.
Cikin sanyi Ishmah ta kalli Yah Rabi'u ɗan Bappa Bello dake zaune ba tare da ya fara cin abinci ba.

“Yah Rabi'u kaci abinci mana”.
Kanshi ya ɗan jujjuya tare da cewa.
“Ina azumi ai”.
Da sauri Rahama tace.
“Kai Yah Rabi'u dan Allah ka karyashi muna haɗe kowa nacin kai kuma ka wani ce kana azumin”.
Cikin mutuntaka da nagarta yace.
“Azumi mukeyi dani da Yah Abubakar wanda mukayiwa Allah al'ƙawarin duk randa Ishmah tayi aure, zamuyi azumi uku uku domin gode mishi”.
Cike da tarin mamaki ta kalleshi.
A ranta tace.
A kaina, shin dama ashe har haka rashin aurena ke ciwa yan uwa tuwo a kwarya.
A fili kuwa sunkuyar da kanta tayi, yayinda wasu siraran hawayen ke zubo ma.
Cikin sanyi kuma duk suka kalli Adam daya saki wata doguwar ajiyar zuciya murya cike da rauni yace.
“Ni saboda aurenta nake azumi uku cikin ko wanne wata, sai  gashi yanzu kuma da auren yazo, ji nakeyi tamkar ace an fasa saboda, bana son tayi nesa damu, domin itace ta meye mana gurbin Daddy a gidan.

Ita muke gani muji sanyi itace ta danne maraicinmu, mukan shiga ɗakinta muyi tamkar yadda mukeyi a ɗakin Daddy".
Da sauri Yah Abubakar ya ɗan dafa hannunsa dake kusa da nasa tare da girgiza mishi kai.
Sai kuma duk suka kalli Hamisu wanda ya miƙe tsaye tare da ficewa yana zubda hawayen tunowa da Mahaifiyarsun da kuma nesa da yayarsu zatayi dasu.
Da sauri kuma duk suka kalli Rahma yar auta data saki shesh-sheƙan kuka murya na rawa take cewa.
"Yanzu zamu ƙara fuskantar maraici, ni bazan ma zauna a gidan nan ba in ta tafi".
Da sauri Yah Muhammad ya jawo hannunta tare da cewa.
"Zo nan auta, ba gamu ba, duk abinda kikeso zamuyi miki".

Ita kam Ishmah tuni take zubda hawaye masu zafi.
Sosai take jin rashin mahafiyarsu ya sabunta garesu.
Yah Rabi'u ne ya gyara zamansa cike da hikimar Addini ya fara yi musu nasiha mai ratsa jiki wacce tasa gaba ɗaya suka fara samun nitsuwa.

Ethiopia
Cikin sanyi Abpu ya koma ya kishingiɗa jikin kujerar dake bayanshi.
Tare da fesar da zazzafan numfashi cikin alamun rashin ƙoshin Ify yace.
"Zuwa yanzu dai dole in cire batun auren Adaya a raina.
Wata ƙil itace Allah ya bani Zakka a cikin yayana.
Allah yaji ya gani nayi iya iyawata shine shaidata, kamar yadda shine mai shiryawa,
To ina fatan ya shirya min ita fiye da bada tarbiyata in tana da rabon shirya,
In kuma bata da rabon shirya ina roƙon Allah ya yafe min kada ya kamani da zunubanta".
Ya ƙare maganar murya cike da rauni.
Yah Ma'aruf dake gefene ya ɗanyi saurin motsawa kusa dashi.
Aminullah kuwa ƙaninta hawayene suka tsinko mishi.
Ummi kuwa murya a sarƙafe tace.
"In sha Allah zata shirya, tunda kace Allah.
Ta dire mgnar tana nazari yau kwana uku kenan Adaya bata fita ko tsakar gidaba tun randa wanda akace mijinta ne yazo ya saketa.
Yah Ma'aruf ɗinne yaci gaba da tausa sa Abpun.
Mamanshi kuwa k'waffa tayi ƙasan lips  tare da juyawa ta fice Allah ya sani lamarin Adaya ya fara damunta, dan yana damun mijinsu kuma itama duk inda taje sai ace ƴarsu cikin takaici tace.
"Shegiyar yarinya mai kama da ifiritu minaljinni, ta buwaye mu ai ta nuna mu, Allah ya shirya."

A dai-dai lokacin a can Parlour Abba kuwa.
Sheykh Tajuh Usman Bauchi ne tare da Babban ɗansa Sheykh Tijjani Usman Bauchi.
Sai Uncle Bello.
Da kuma Taj dake tsakiyarsu.
Bisa dukkan alamu magana mai mahimmanci suke tattaunawa

Bayan sun gama duk tattaunawar tasu, sun tsaida matsayar tafiya da masuyin rakiyar kai amaryar.

Sai ƙarfe goma su Sheykh Tajuh Usman Bauchi, suka fita tare da tawagar zakiransu, suka kama hanyar Bauchi, bayan ya ƙara kebewa da Taj ɗin.

Cikin sauƙe numfashi Uncle Bello ya kalli Abba da kuma sauran yaran nasu kana yace.
“To Alhamdulillah, abu yazo mana a lokacin da bamuyi zaton zai-zo mana a hakanba.
Sai kuma ya ɗan kalli Yah Muhammad tare da cewa.
“Masu zuwa rakiyar nanfa, bazasu wuce 6 ba, ni in a son samu nane ma mutum biyu kacal”.
Kai Yah Muhammad ya jinjina tare da cewa.
“Toh gsky nima hakan naso, toh shi ɗin ne yake nunin da aje ɗin saboda wai hankalin Ishmah zaifi kwanciya, kuma Abba ma zaifi samun nitsuwa in ya san inda Boɗɗinsa take”.
Murmushi ya ɗanyi kana yace.
“To ka kira Goggo Dijan ku. ƙanwarsu Abba kenan. da takwararta Khadijah ƙanwar Ishmah kenan mai Binta.
A gefen mu su zasuje, sai kuma ummarku ɗaya.
Sai kuma matarka ko matar Abubakar, sai kuma uwar ɗakinta Garkuwa.
Biyar kenan ko?”.
Da sauri Yah Abubakar yace.
“Eh”.
Yana gyara zamansa yace.
“To sai ita Ishmah da mijin nata, bakwai sun fito ba.”
Cikin sanyi Taj ɗin yace.
“Eh yanzu mukayi waya da Sheiykh yace, min yayi magana da wani ƙaninsa cewa, za'a samu Visa, sai dai na mutum takwas za'a samu kuma ranar Laraba jirgin zai tashi.”
Cikin sauke numfashi Yah Abubakar yace.
“To sai asa Adam cikon na bakwai ɗin, kar suje ba namiji ko ɗan aike zai musu, kuma Aunty Nana taje, In sha Allah daga baya zanje da Maryam kam”.
Cikin gamsuwa Abba yace.
“To Allah ya sanya alkhairi aje Ify a dawo Ify.
Khadijah ma da Dija sun cemin sun taso suna hanya ma”.
Shiru sukayi jin Yah Muhammad na cewa.
“Toh Amman Uncle Bello ko dai Ummace zataje madadin Nana”.
Da sauri Uncle Bello yace.
“Wannan tunda muka dawo Umrah take fama da mura, gashi matar Rabi'u nada tsohon ciki. Baza muso a barta ita ɗaya a gida ba babba ba”.
Cikin gamsuwa yace.
“To Allah ya sauƙeta Ify”.
Amin suka amsa sai kuma yace.
“To sai kaje ka amso E passport ɗinsu duk masu zuwan dan ayi duk abinda ya dace”.
Daga nan dai suka gama tsara komai.

A Parlour Daddey kuwa cikin murmushi Yah Muhammad yake kallon E passport ɗin Ishmah tare da cewa.
“Masha Allah saura wata uku yayi expire, da yanzu sai munyi sungular sabunta shi, Kinga yanzu an huta mijinki yayi sungular in kunje.”
Ba tare da ta fahimci mgnar saba, ta juyo tana kallon Aunty Maryam dake miƙo mata bowl ɗin data zuba mata dahuwar jan naman.
Amsa tayi tare da cewa.
“Amman sai anjima yanzu bana jin yunwa”.
Cikin kulawa Yah Muhammad yace.
“Toh me kikaci ɗazumafa ina ganinki ba abinda kikaci”.
Cikin sanyi tace.
“Ji nake ina ƙoshe”.
Kai ya jujjuya mata tare da cewa.
“A'a Goggani kada kiyi haka”.
Da yake yakan kirata da goggini a wasu lokutan yadda Khairat ɗinsa ke kiran Ishmah kafin ta gama iya magana.
Kujera ya nuna mata tare da cewa.
“Zauna kici, ke baki ga kin zama yar lelenmu ba”.
Kai ta ɗan sumkuyar tare da cewa.
“Toh”.
Daga nan ya fita yana faɗin bari inje in amshi na Aunty Amina da Garkuwa.
Cikin sauri Aunty Nana tace.
“Abban Ikiram ya yarda zata je?”.
Kai ya jinjina tare da cewa.
“Eh Amman fa saida Abba da Sheykh Tajuh da Tajj ɗin sukaje har wurinsa tukun ya yarda”.

Adam kuwa da bashi da E Passport Abubakar yasashi a gaba sukaje ayi mishi.

Hakan kuwa akayi.
Cikin kwana biyu aka gama komai, to abune na kuɗi da kuma sa bakin manya, shiyasa tuni komai ya kankama ya haɗu.
Aunty Maryam kuwa da Garkuwa wani irin shiri da tsumi na musamman sukeyiwa Ishmah da har yau mgnar kalmar auren nan bai haɗata da kowaba.
Har gobe jin kalmar take a baƙuwa a cikin kunnuwanta.

Taj kuwa tamkar ma gudunsa takeyi, ko sun kasance wuri ɗaya ma kuma zama take tamkar ba itace surutacciyar abokiyarsa nan mai tsananin shaƙuwa da shiba sai dai tana kula da ƙafarsa duk dai har yanzu yana ɗan ɗingisa ta.

A tsakanin kwana kin kuma ya amsa gayyatar sauk’an karatun wasu ɗalibai a jihar Bauchi a ƙaramar hukumar Azare.

Ita kuwa Ishmah gani take Taj ɗin tamkar ba Taj ɗinta bane, kamar wani ne da ban aka ajiye

mata.
Saboda tsananin nauyin shi da takeji wanda yasa ko sunanshi nauyin faɗi yake mata.
(girma da darajar aure kenan.)

Khadijah da Goggo Dijan kuwa da Aunty Maryam tuni suketa shirya komai na tafiya.

Ethiopia
Yau talata Ummi ce zaune tare da tsurawa Adaya idanu tana kallon yadda take tahowa wurinta cikin sanyi da lallaɓa takun ƙafar tamkar ba Adayarta data sani a bayaba wacce ko tafiya take sai ta rausaya ba.
Numfashi mai nauyi ta fesar dai-dai lokacin da Adaya ta zauna gefentan a hankali tace.
"Adaya nafa ce Miki, na san akwai abinda kike ɓoye min, ki faɗa min menene matsalar ki?".
Cikin sauri da karsashi tace.
"Ummi ba abinda ke damuna fa! Kawai zazzabin da nayine, kuma na gaya miki faɗuwar da nayi a BQ lokacin da zan fita ne, ƙuguna ya bugu shiyasa nake tafiya a hankali dan har yanzu yana min ciwo, shiyasa ma ko fita rihazal banayi".
Cikin rashin gamsuwa Ummi tace.
"Toh Allah ya sauwaƙa".

Gidansu TAJJ.

Ummey ce zaune gaban Addawa cikin sanyi tare da tsiyayar da hawaye masu zafi
Murya na rawa cike da rauni tace.

"Ko ina yayi min zafi a duniya ji nakeyi, bani da wani sauran farin ciki tunda Malam ya nesantani da Afif ya cika zuciyata da duniyata da baƙin ciki mara yankewa.
Nayi niyar zanyi mishi mgnar Afif in yaso ta zama sanadin aurena, in rabu dashi inje in kansance tare da ɗana, in killace shi in cire mishi ƙuncin rashin mahaifin nasa.
Amman kin hanani kana kin ƙara min wuta a kan ranar da malam ya sani".
Cikin sanyi Addawa ta ƙara matsowa kusa da ita.
Sassayan numfashi ta fesar tare dasa hannunta ta sharce mata hawayenta da wani ke korar wani cikin hikima da hangen nesa na manyan mutane tace.
"Eh ko yanzu zan ƙara jaddada Miki ban amince ki kira masa sunan Taj a gabansa kamar yadda yace ba".
Har suna haɗa baki ita da Halima sukace.
"Toh saboda me?".

"Saboda yace in kin kira masa sunansa a gabansa ko kinyi alaƙa dashi a kan aurenki".
Da sauri tace.
"Toh me zanyi da auren Malam me ya rage min dashi".
Tana maida hawayenta dake tsatstsafowa tace.
"Nasan idan har kikayi mgnar Afif a gabansa tabbas zai sakekin, sakinki kuma shine abinda zaifi yiwa Afif ciwo fiye da komai, yace min bazai taɓa yafewa kansaba in har ya zama sanadin

rabuwar auren iyayensa.
Sannan kuma ai in kikayi abinda zaku rabu da Malam kin yiwa magauta abinda suke so, shike nan sunyi nasarar korar ɗanki. Kema sun fidda ke gidan Zakiya nayin aure shike nan baki da ko tsuntsu a gidan
Zai kuma tabbata cewa Afif ya aikata laifin kenan?!".
Da sauri Ummeeyshi ta saki shesh-sheƙan kuka.
Dafa kafaɗarta Addawa tayi tare da cewa.
"To in dai bakya son haka ya tabbata, to kiyi haƙuri kada ki sake mishi mgnar Afif, kuma daga ke har su Maryam kada kuyi alaƙa dashi, saboda kada Allah ya isan mahaifinsu ya hau kansu".
Cikin kuka Halima tace.
"Yanzu shike nan an rabamu da ɗan uwanmu an maraitar dashi duk da yawan danginsa!".
Cikin ƙarfin hali Addawa tace.
"Tajuddeen bazai maraitaba, zan kasance tare dashi, kamar yadda na gaya muku dani da Laylah, da  Zulaihat yau da dare zamu tafi Qatar zamuje can.
Yace min shima zuwa dare baƙi zasu isa in rigasu isa in marabcesu, sai dai bansan wasu baƙin bane, kuma bansan ina yake ba.
Dan haka ki kwantar da hankalinki zanje in kasance dashi zan bashi dukkan kulawar da kikega in kuna tare zaki bashi.
Wani sassayan kuka Ummeeyshi ta kuma sakewa tana faɗin.
Yanzu ko a waya kenan ya haramta inyi mgn da ɗana".
Da sauri Addawa tace.
"Kwarai ma kuwa, don kiyaye igiyar aurenki, ki zauna a nan mu jira ranar da gsky zatayi halinta domin ai INDA RAI to tabbas da Rabo.
Ki zauna a gaban idonki gsky zatayi halinta kiga yadda kwayar idanun magautansa zasuyi."

Nigeria.
Yau Laraba tun safe suke gama shirin su, duk masu tafiyar sun haɗu.
Garkuwa, Aunty Amina, Aunty Nana, Khadijah, Adam Goggo Dija.
Kasan cewar ƙarfe tara jirginsu zai tashi daga Adamawa to Lagos.

Ƙarfe biyu dai-dai kuma zasu tashi daga Logos Nigeria to Doho Qatar.

Cikin sanyin da tunda gari ya waye ta tashi dashi, da ji take da ganin abin kamar wasa ko almara koko mafarkin da zata farka ta ganshi a sawarware.
Rauninta yayi ruɓanya da kaso 90 bisa ɗarine, a lokacin da taga anata fidda dukkan kayayyakinsu durƙushe take a gaban Abbanta da kuma Uncle Bello sai Yayunta.
Wani irin sassayan kuka take yi mai tsuma zuciyar duk mai imani.
Sai kuma kawai ta rarrafa a hankali ta ɗaura kanta bisa cinyar Hajia kakarta wacce tun safe tazo don yin sallama dasu.
Sunkuyar da kai Abba yayi domin shima kansa hawayen ke zubar masa.
Da sauri Rahama tazo ta raɓa jikinta jin tana cewa.
"Yanzu in na tafi waye zai zauna dasu Rahama, waye zaike hanasu kewa da maraicin Daddy,

Waye zai rinƙa hana Hamisu kuka in ya tuno Daddynmu".

Wani irin azabebben numfashi Taj ya fesar a hankali, tare da rumtse idanunsa ji yake yi kukanta na ƙona mishi ƙahon zuciyarsa tamkar zata narke.
Uncle Bello ne ya ɗanyi ƙarfin halin farayi mata faɗa mai haɗe da nasiha nasiha.
"Toh Shatu YAR FULANI. Kin mance cewa Duk wanda baya yarda da ƙaddara MI WASMITI shine kalmar da zata yi abota da harshensa.
Ki tuna fa cewa NAMIJI BAYA KAƊAN.
Ai duk sonki da su Hamisu iyakar na BANDIRAWO ne baki kai Allah daya haliccesu sonsuba.
kuma dai TAUSAYAWA JUNA da kuke bazai hanaki yin aure ki raya sunnar Manzon Allah ba.
Tunda da baku isa ku kauda RUBUTACCAN AL'AMARI ba.
Mutuwa kuwa ai RIGAR KOWA ce, Mamana ya zamuyi Allahn da ya bamu ita shi ya ɗauke mana ita, kuma ya fimu sonta.
To ma wai zakiyi butulci da HUKUNCIN ALLAH ne Mamana?
Kin sani cewa Babu Maraya sai rago ko, to ai ko NAKASA MA BA KASAWA BACE, bare kuma ga
Ga yayunku da mahaifinku wanda yake GARKUWA a gareku.
Kuma TUBALIN jin daɗi rayuwarku.
Kada ki mance cewa Allah yayi miki SAKAYYAH nefa da maɗaukakin aure a bisa haƙurinki da kikayi tsawon shekaru kina riƙe da kanki
Dan haka ki share hawayenki ai INDA RAI to ai ana tare duk inda kike a faɗin duniyar nan."
Ina ta kasa tsaida hawayenta saboda jin murya Khalid wanda Hamisu ya ɗaukosu dan suzo suyi sallama da ita wani irin sassayan kuka yaron yakeyi harda Shesh-sheƙan kuka.
A hankali Taj ya jawoshi jikinsa cikin son yaron tare da jin tausayinsu zai ɗauke musu uwarsu ya nesantasu da ita.
Wani irin tausayin Minat dake gefe tana sharar kwallane ya rufeshi.
Ji yake yi shi da yake babba ma daga shi sai Allah ne kaɗai suka san irin ƙunci da ciwon da yakeji na rabuwa da iyayensa da yayi, inaga su yara.
Cikin sanyi yace.
"Zo nan my Daughter".
Ya ƙare maganar yana jawo hannunta a hankali ta matso gareshi sai kuma ya jawo Mahamud da yayi ƙasa da kanshi cikin sanyi yace.
"Kada kuyi kuka, kuyi mana addu'a, kai My boy kana gama Secondary School zaka dawo wurinmu kaci gaba da Karatu.
Kema My Daughter zaki dawo kuyi karatu tare da Laylah ɗinki ko.
Kai kuma Mahmoud ai kama kusa tafiya Mexico kayi karatu a can ko?".
Cikin jin daɗi duk sukace masa.
"Yess Uncle Taj".
Yana sharewa Khalid hawaye yace.
"To kuje ku rarrashi Amminku kuce tayi haƙuri".
Kusan a tare suka koma gabanta da sauri ta ruggume su.
Sai kuma tayi murmushi mai haɗe da hawaye jin Khalid na cewa.
"Ammi ki dena kuka, nima ina gama Secondary School zan taho Qatar mu zama larabawa".

Kanshi Abba ya shafa tare da cewa.
“Yauwa Khalid haka nake son ji”.
Da sauri duk suka ɗaga hannayensu jin Uncle Bello na cewa.
“To muyi musu Addu'a.”
Nan fa yayi ta kwararo musu addu'o'i.
Bayan sun shafa ne, kuma Ishmah ta sake sakin wani kukan.
A hankali Abba ya miƙe tsaye tare dasa hannunsa ya kamota ya tsaida ita cikin kuka tace.
“Abba wa zai zauna da Rahama da Hamisu”.
Da sauri ta sauƙe nannauyan numfashi jin Hajiabna cewa.
“Ki kwantar da hankalinki Ni zan zauna dasu, sai Abbanku yayi aure zan koma gida”.
Cikin jin ɗan sanyi a ranta ta ruggume Hajia.
Yah Muhammad ne ya ɗan sharce hawayen da suka zubo mai gami da cewa.
“'Lokacin tashin ku ya kusa fa”.
Aunty Amina ce ta kamo hannunta suka fito ganin alamun bazata saki Hajia ba.
Cikin sanyi da tsokana Maryam ta sharce hawayenta tare da cewa.
“Fisabilillahi ke ba yarinya ba duk kiyi ta samu kuka da shogwabarki ki karya mana zuƙata.”
Ruggume Maryam ɗin tayi tare da cewa.
“Aunty Maryam zanyi missing naku ga amanar su Rahama”.
Sai kuma ta sake Maryam ta ruggume Hamisu.
Murmushin ƙarfin hali yayi tare da kamo hannunta suka nufi motar Abba buɗe mata yayi ta shiga kana ya sunkuyo a hankali ya raɗa mata wata kalma.
Kawai sai gani akayi tana Murmushin tare da dukan kanshi.

Daga nan duk saura suka shiga motocin akaja aka tafin.
Suna zuwa Airport ba dadewa suka tashi, suka yi Lagos.

Suna shiga cikin jirgi a jere cike da nitsuwa wayace maƙale a kunnensa bisa alamu da Addawa yake mgna.
“Mu yanzu zamu tashi!”.
Tana gyara zamanta bisa ɗaya daga cikin hamshaƙan kujerar tace.
“Mufa tun sha biyu muka isa”.
Kai ya ɗan jinjina tare da cewa.
“Eh ai ba nisa Ethiopia to Qatar 3 Hours and 18 minutes ne!”.
Tana lumshe ido alamun bacci tace.
“Kuma zaku iso kafin la'asar ko?”.
Suna haurawa saman first class, ya ɗan girgiza  kai tamkar yana gabanta kana a hankali yace.
“Nanfa Nigeria to Qatar 8 Hours and 55 minutes ne, kin ga tafiya ce mai nisa sosai”.
Ya ƙare maganar tare da zama bisa kujerar dake gab da window, a hankali Ishmah kuwa data lumshe idanunta hawayen da suke ciki suka zubo, Saboda jin irin nisancin da zatayi da ƙasarta da yaranta mahaifinta Yayunta da kuma ƙannenta hakan yasa kukanta ya sabunta,
Tana mai zubda hawayen ta zauna.
Yayinda Garkuwa kuwa da Aunty Amina suke gefen daman su.
Sai Khadijah da Goggo Dijan dake bayansu.

Adam da Aunty Nana kuwa na can baya.

Shi kuwa Taj a hankali ya ɗan gyaɗa kansa tare da cewa.
"Uhmmmm". Saboda jin Addawa na cewa.
"Kace inyi baccina sai tsakiyar dare zaku iso, ni da nufina zan jira isowarku ai".
Ƙosawa da surutunta ne ya sashi katse kiran tare da kashe wayar saboda sanin dokokin su na cikin jirgi.

Ƙarfe biyu dai-dai jirginsu ya ɗaga zuwa Qatar.

Wani irin kukane mai sassayan sauti ya kubcewa Ishmah lokacin da taji jirginsu ya rabu da ƙasarta ta haihuwa.
Lallai wanda baiji tsoron Allah ba ya wahala.
Cikin kwanaki biyar rayuwarta ta sauya salon ƙaddararta ya juye yazo mata a baibai, ko kusa ko zato ko tsammani fita ko cikin Jimeta batayi ba sai gashi wai ƙasar zata bari Bama ƙasar ba Africa baki ɗaya.
Dama ace Ethiopia ne da tasan ko ba komai yankin nahiyarta ne Africa."

Shi kuwa Taj a hankali ya lumshe idanunsa, tare da fara tariyo shekarun baya, yana mai tunowa haɗuwarta dashi da halin da ta shiga, tuno da wannan ne ya sashi ɗan gyara zamansa tare da ɗan matsowa kusa da ita.

Dai-dai lokacin kuma tayi saurin rumtse idanunta da ƙarfi saboda jin hanjin cikinta sun fara walle-walle irin dai yadda taji a shiganta jirgi na forko a rayuwarta.
Murya cike da rauni tace.
"Innalillah".
Da sauri yasa hannunsa ya kamo nata ganin ta yunƙura bisa alamu so take ta kafa goshinta a jikin set ɗin da yake gaban nata.
Da ƙarfi ya ɗan matse hannun nata cikin nashi tare da sarƙafe yatsunsu wuri ɗaya.
Sassayan numfashi ya fesar tare da ɗan jawota gefenshi, dai-dai lokacin kuma jirgin ya ɗanyi marisar ɗaukar asalin hanyarsa.
Cikin tsananin tsoron ta raɓa jikinsa gefen kafaɗarsa ta manna kanta bisa damtsenshi tare da rumtse idanunta da ƙarfi.
Shi kuwa Taj cikin fesar da sassayan iska ya ƙara matse hannunnata tare dasa hannunshi ɗaya ya gyarawa kanta zama, cikin sanyi ya lumshe idanunsa tare da ɗan sunkuyar da kanshi kaɗan lips inshi ya manna bisa goshinta tare da liƙa mata wani amintaccen kiss mai sauk'ar da nitsuwa.
Ajiyar zuciya mai nauyi taja kana ta sauƙe tare da direshi da ƙarfi, saboda wani irin sanyi da taushin lips inshi da ya ratsa mata goshi.
Shi kuwa Taj a hankali ya ɗan ƙara matsowa kusa da ita, sai kuma ya ɗan sunkuyo ya leƙa fuskar ta ganin hawaye na zubowa ne yasashi sa yatsunsa biyu ya sharce mata hawayenta, sai kuma ya ɗan ƙara sunkuyowa sosai ya kai bakinshi dab da kunnen ta.
Sassayan numfashi ya shaƙa tare da motsa lips inshi a hankali murya cike da raɗa yace.

“Shima iri ɗaya ko Ma'eeshah!”.

Sai kuma ya ɗan cije gefen lip inshi na ƙasa yana mai ƙara yarda cewa haɗinsu daga Allah ne, shiyasa komai nasu yake zuwa iri ɗaya, jin hawayenta na ɗisa bisa cinyarsa ne yasashi ci gaba da cewa.
“Allah ne ya ke kusanta ƙaddarorinmu da kamantasu, kin rasa Daddy a lokacin ban alaƙan ta kamanceceniyar ƙaddararmu ba, sai gashi ni ƙaddara ta rabani da Ummey na, wanda gwara ke mutuwace ta rabaku”.
Haka nan taji hawayenta sun tsananta domin tunda yazo basuyi wani zaman kirkiba jin abinda yake faɗane kuma yasata fahimtar cewa ya shiga cikin jarraba mai tsanani.
Shi kuwa Taj a hankali ya motsa lips inshi tare daci gaba da faɗin.
“Akasi kuma yasa mutumin da yafi kowa sona a duniya ya nesanta kanshi dani, ya barrantani da yaransa yace, ya barwa duniya ni, kinga gwara ke zaman aurene sunnar Manzon Allah ne yasa na rabaki da Abba, Ma'eeshah dani dake bamu da banbanci, nima tamkar maraya nake, bani da kowa duniya sai ke da Addawa da Laylah, Ma'eesha kece kaɗai sauran hope d’ina, in bake a kusa dani ba amfanin rayuwata gwara kawai in mutu in hut”.
Shiru yayi ba tare da ya ƙarasa mgnar ba jin yadda take jijjiga mishi kai.

Aunty Amina ce ta ɗanyi murmushi tare da nunawa Garkuwa inda suke da idanu.
Itama Garkuwa murmushin tayi tare da cire idonta.

Khadijah kuwa tuni tayi baccinta mai daɗi.
Adam kuwa kurui yayi da idanu yana kallon yadda suke keta hazo da gajumare, suna fesa gudu.

Ita kuwa Ishmah a hankali ta fara jin bacci saboda.
Yadda yake ɗan jijjiga ƙafafunshi a hankali hankali wanda wannan halittarce in dai yana zaune sai yayi ta haɗa guiwowinshi yana ɗan rabawa.

Fahimtar tayi bacci ne kuma yasashi gyara mata jingina.
Kana shi kuma ya faɗa duniyar nazarin rayuwar da zai fuskanta.
“Zan rayu dake tamkar abokiyar da kika kasance min Ma'eeshah bazan taɓa kusantar ki a matsayin matar aurena ba, har sai ran da naga sona a matsayin mijin aure ba aboki ba a cikin kwayar idanunki, kuma harshenki ya furta min, dole in fara sauya matsayin soyayya ta a zuciyarki kafin sauya matsayin abota zuwa miji”.

A haka sukayi ta keta hazo har karfe huɗu.
A hankali ta ɗan yunƙura zaune.
Sai kuma ta ɗan kalleshi jin yana cewa.
“Je kiyi al'wala kizo muyi sallan la'asar, ki gayawa su Adam ma duk suyi al'wala suyi niya suyi sallah.
Kai ta jinjina kana ta miƙe tare da nufar wurinda taga yana nuna mata.

Bayan ta fitone duk suka sabunta al'wala bandashi dan yasan al'walarsa na nan.

Koda suka idar da sallan, hannunshi ya ɗago tare da jera musu addu'a.

Daga nan suka ci gaba da tafiya.
Hakama sukayi Magrib da isha.
Koda aka kawo musu ɗan abin taɓawa kowa yaci abinda aka bashi, amma ita babu yadda baiyi da itaba tak'i ci shima kuma baici ba.

Ƙarfe takwas ne ta ɗanyi hamma tare da ɗan lumshe idanunta kana a hankali tace.
“Mun kusa isa? Saura awa nawa?”.
Yana ɗan jawo hannunta yace.
“Saura mana 2 Hours and 35 minutes, bacci kikeji ko?”.
Ya ƙare maganar cike da kulawa, kai ta gyaɗa mishi, ganin haka ne yasa ya jawota jikinsa tare da cewa.
“Zo kiyi baccinki”.
Da sauri Goggo Dijan tayi sauri cire idonta daga kansu.

Ita kuwa yana jawota ya manna kanta a damtsen hannunshi lokaci d’aya bacci yayi awon gaba da ita.

Ƙarfe 9 da minti 35 dai-dai jirginsu yayi landing a Qatar Airways tower.

Bayan duk sun shiga motocin.
A hankali ya kamo hannun Ishmah tare da nufar ɗaya daga cikin motar suna shiga.
Akaja motar tare da bin bayan sauran.

Tafiya mai tsawo sukayi.
Yayinda gaba ɗayansu suka ware idanunsu suna kallon tsari da shaharar ƙasar Qatar da da ta wuce tunanin mai tunani.
Cikin buɗe ido Adam ya kalli Khadijah tare da cewa.
“Yah Sallam Anty Khadi Kinga duniyar da Allah ya kawo mu”.
Kai ta jinjina tare da cewa.
“Ai ni nama rasa abin faɗa, wannan abu kamar aljanna!”.

Garkuwa kuwa a motar da suke sassayan numfashi ta fesar tare da baza ido tana ƙarewa Qatar kallo tare da ƙudurtawa a ranta in sha Allah sai tayi littafin a Qatar.
Su Garkuwa ɗiɗɗiri sai baza na mujiya ake ana kallon kauyenci to ba fulatanar daji a tsakiyar birni Doha.

Aunty Amina kuwa cikin sanyi tace.
“Allah ɗaya gari bambam”.

A motarsu Ishmah kuwa a hankali ta kalleshi cikin sanyi tace.
“Ya naga sunyi can mu munyi nan”.
Cikin kulawa yace.
“Su gida zasu wuce!”.
Cike da gajiya tace.
“To mufa?”.
Yana ɗan matsota yace.
“Zaki gani”.
Dai-dai lokacin kuma taga driver ya ɗan karya kwana ya fuskanci wani ƙaton gada daya yake gicciye a tsakiyar tekun dake zagaye da ƙasar, da sauri ta rumtse idanunta saboda iya ganinta ruwane a kwance bila haddin.

Tafiya mai tsawo sukayi kana taji an buɗe musu Gate.
Yah Salam shine abinda tace dai-dai lokacin da idanunta suka sauƙa kan wani Mashahurin Hotel Rixos Gulf Hotel Doha, wani irin hotel ne na alfarmar kai da gani ma kasan bana yara bane.

Wanda ke jan motar ne ya fito, tare da ɗaukar trollybag d’in Ishmah, kana suka fito suka bishi a baya.

Sassayan numfashi mai nauyi ta fesar a hankali da ta kutsa kanta cikin Parlour.
Ya ilahi ya mujibat da'awati, sune kalaman da ta faɗa saboda wani irin ni'imtaccen ƙanshin gami da sanyi mai kashe jiki da zuciyar ɗan Adam.

Jujjuya kwayar idanunta tayi tana ƙarewa Parlorn kallo a saman lips inta tace.
“Wannan a duniya ne haka? Ya Allah ka bamu aljanna”.
Sai kuma ta ɗan kalleshi jin ya kamo hannunta tare da amsar trolly bag din.
Shi kuwa driver’n juyawa yayi ya fita.
A hankali suke takawa har suka shiga cikin bedroom ɗin, a hankali ya sauƙe numfashi kana yace.
“Shiga kiyi wonka, kafin a kawo miki abinci!”.
Yess tana son yin wanka Amman jin ni'imomin cikin ɗakin yasa taji wani irin sassayan bacci na diro mata.
Shi kuwa Taj drawer’n dake kafe daga dungu har dungu ya ɗan buɗe mata side ɗaya tare da cewa.
“Ga sleeping dress a nan in kin fito.
Ya ƙare maganar tare da sa hannunsa ya zaro wata tattausan jallabiya Black blue mai sheƙi, kana ya fita Parlour.

Bayan tayi wanka ta fitone kuma ta kimtsa kanta cikin wasu soft sleeping dress na companyn Gucci riga da wondo ne masu kyau da shek’i had’i da ɗan kaurin da zasu kareta daga tsananin sanyin AC’n dake d’akin, rigar pink and white color ce, sai kuma white headband me kyau da

tasa a kanta tare da tubke gashin kanta, idanunta ta d'an lumshe alokacin da ta d'au d'aya daga cikin unisex perfumes d'in da ta gani akan tsararren dressing mirror d'in dake d'akin, turaren me suna Symphony na companyn Louis Vuitton ta fesa ajikinta, sosai kuwa kamshin yayi mata dadi.

Cike da gajiya ta zauna a bakin gadon,
Da sauri kuma ta lumshe idanunta saboda jin kamar anayi mata lilone sunkuyar da kanta tayi tana shunshunan kanta da kanta saboda jin yadda take baza ni'imtaccen ƙamshi.

Lokaci d'aya kuma sai ta kalli wayarta jin alamun an turo mata saƙo a WhatsApp.
"tana buɗewa kuwa taga Hamisu ne, sai kuma ta ɗan kalli saman profile picture d'inshi ganin alamun yasa abu a status ɗinsa.
A hankali ta danna kanshi.
Cikin wani sanyi mai cike da gajiya kasala, ta zame ta kwanta a bakin gadon tana fuskantar ƙofar shiga.
Wasu irin zafafan hawaye ne suka fara silalo mata.
Dai-dai lokacin kuma Taj ɗin ya shigo sanye da jallabiya sai faman baza fitinannen ƙamshi mai kashe jiki da zuciya yake.

Ido ya ɗan zuba mata ganin alamun bata ma san ya shigo ba, da fari yayi zaton tayi bacci ne, sai da ya ɗan matso kusa kuma yaga idanunta na zubda hawaye.
Cikin sanyi ya fara takawa yana matsowa bakin gadon.
Tare da yawo da kwayar idanunsa akan dukka sassan jikinta.
Ahankali ya zauna a ƙasan gadon dai-dai inda kanta yake, cikin nutsuwa ya daidai ta fuskarsa da tata fuskar.
Kana asanyaye cikin wani irin fitinannen yanayi mai hana zuciya sukuni ya kusan to da fuskarsa tare da zira....

********************** ? **************************
********** Ai Hausa Novels ****************
************************? **********************

DOWNLOAD More complete Hausa Novels, Education Books, Adventure, Drama, Mystery, Religion, Fiction, Non-Fiction, Romance, Meimor, True Life Stories & Others from our blog.

Visit > https://www.aihausanovels.com.ng

Ka tura mana sako ta adireshinmu na email, domin tuntubarmu ko turo mana hausa novel ko kuma post.

Email > aihausabooks@gmail.com

******* FOLLOW US ******

Facebook: Ai Hausa Novels

Twitter: Ai Hausa Novels

Telegram Channel: https://t.me/Aihausanovels

WhatsApp Number: 08138873799

Haka kuma domin shiga kowanne daga cikinsu za ku iya ziyartar shafin ku yi search na AI HAUSA NOVELS, hatta facebook group dinmu ma za ku samu.

********************** ? *************************
*************** Ai Hausa Novels ****************
********************** ? *************************

By
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 📝🕋💉🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*INDA RAI*
*AYASHA ALIYU GARKUWA*
*BOOK 2 PAGE 7*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

“Bazan iya zama a gaban ka ba, kana suffanta min kanka da waɗanan mugaye, ƙazaman, lalatattun, halayyar da nasan ba naka bane, kuma bazaka aikata ba, Wallahi tallahi bazan taɓa yarda da kaiba koda zaka kwana dubu kana faɗa min waɗanan kalaman ne.
Please dan Allah Tajj kace min wasa kake min, kace min ƙarya Addawa tayi min, kasan na sani cewa kai maitsarki ne kuma tsarkakken da zuciyata tasashi a sahun masu cikar imani kuma nagartataccen da bani da haufi kan nagartarka Please dan Allah kada ka faɗa min kalaman da zasu fasa min zuciyata”.
Taƙere mgnr cikin Muryar kuka tare ysyyarfa hannu ɗaya, ɗaya kuma na bisa ƙirjinta.
Shi kuwa Tajj da sauri ya tashi tsaye tare dasa hannunsa ya kamo hannunta da take ta yarfawa tamkar wacce ta ƙone.

Wani irin nannauyan numfashi ya fesar mai zafi tare da sakin ƙaƙƙarfan ajiyan zuciya dake nuni da kaso 50 na cikin dari na damuwar dake nuƙurƙusar rayuwarsa ya bar zuciyarsa.

Addawa kuwa tun sanda yacewa Ishmah yayiwa Laylah fyaɗe ta shigo da sallamar da basu jitaba bare su amsa mata, gefensu ta tsaya a duk da basu gantaba.
Shi kuwa Taj cikin sanyi ya jawota jikinsa tare da yi mata amintaccen ruƙuma murya can ƙasan maƙoshinsa yace.
“Babe haka akace wai ni nayiwa Laylah fyaɗe, kuma har Ummeey na da Yah Abana sunyi fushi dani”.
Cikin jujjuya mishi kai da zubda hawaye tace.
“Karya ne Tajj wlh ƙazafi akayi maka! Ban yarda ba, baka aikata hakaba waye ce kai kayiwa Laylah...”.
Sau kuma ta gaza ƙarasa kalmar.
Shi kuwa cikin sanyi kamar a narke mgnar ta fito.
“Meymey ce tacewa Yah Abana ni nayiwa Laylah fyaɗe, kuma Laylah ta tabbatar gashi tsorona takeji”.
Da sauri ta ɗan janye jinkinta daga gareshi tare da jujjuya kanta tana faɗin.
“Allah ya isana ban yafe mataba, tayi ma ƙazafi mafi muni, ta rabaka da mutani mafi soyuwa a gareka, tayi maka illar da har abada zuciyata bazan taɓa iya yafe mata ba”.
Sassayan numfashi Addawa ta fesar domin itama da fari taji tsoron ƙarshen kalaman Ishmah kar tace bazata zauna da Tajuddeen ɗin ba”.
Ita kuwa Ishmah a hankali ta zame ƙasa ta zauna, wanda haka yasa shima ya zame ya zauna. Suna fuskantar juna, guiwowinta na manne da guiwowinsa cikin sanyi da alamun ta fara dawowa gayyacinta,  tunda yace mata ance ne bawai shi da kansa bane yake jaddada mata cewa yayi fyaɗen ba.
Murya a sanyaye tace.
“Allah ya isana bazan taɓa yafewa duk wanda yayi maka wannan ƙazafinba, Saboda an sawa Al-AHLI AFISHA tabo mai wuyar mancewa, zan ƙare ragowar rayuwata dayi maka addu'o'in neman sakkayar duk wanda yayima ƙazafin nan, da yi mishi addu'o'in tonon asirinsa da rashin samun duk kwanciyar hankali a cikin burinsa kai harda addu'o'in ganin azab...”
A hankali ta lumshe idanunta hawaye masu zafi na kwaranyo mata saboda jin yasa tattausan tafin hannunsa ya rufe mata bakinta.
“A'a Babey banda addu'o'in azaba domin Bama fatan ko wanne musulmi ya faɗa cikin azabar Allah”.
A tare suka kalli Addawa jin tana cewa.
“Alhamdulillah Ishmah kin kasance yadda muka zata, kin ƙarfafa yaƙini da Amincin Tajuddeen a kanki, ko duniya duk zasu gaza fahimtarsa ke zaki fahimceshi.”
Shi ma Taj  a hankali yace.
“Mar'atussaliha”.
Da sauri Addawa ta miƙe ta fita.

Ita kuwa Ishmah cikin sanyi tace.
“Tajj wannan ƙazafin ne yasa duk rayuwarka ta ƙuntata?”.

Kanshi kawai yake jijjiga mata dan baya jin zai iya mata cikekken bayanin a yanzu saboda yafi son sai ƴan uwanta sun tafi baya kuma jin zai iya faɗa mata hukuncin Yah Abana na cewa in ya sake yiwa Ummeeyshi mgn ko suka haɗu a kan auren iyayen nasa.

Shigowar Addawa da trayn abincin da ta shirya musune yasasu ɗan gyara zama a plate ɗaya ta zuba musu tare, da ajiye musu spoon guda biyu kana ta tace.
“Bismillah kuci abinci shine abinda zai sama min nutsuwa, bari inje in kawo muku tea.”

Jim kaɗan da fitan ta dawo ga mamakinta ko taɓa spoon ɗin basuyi ba koda ta matsa suci abincin tea ɗin suka amsa suka sha.
Suna gama sha ana kiran sallan azahar, wanda haka yasa shi Taj yin al'wala ya fita tare da Adam da Bilal da yanzu suka shigo.

Bayan sunyi sallan azahar, a ɗakin Ishmah inda nan Aunty Amina da Goggo Dijan suke, ta nufa. Zaune ta samesu da jakukkunansu a gabansu suna shiryawa, cikin sanyi tace.
“Ayyah Aunty Amina me kuke sauri haka tunda ance goben ma sai gab da Magrib jirginku zai tashi”.
Aunty Nana da yanzu take shigowa ne tace.
“Yo ni da zan samu ma mu tashi yau ai da yafi min”.
Sai kuma tayi ƙasa da murya tacewa Garkuwa dake bayanta.
“Saboda nayi kewar mijina”.
Ɗan dungure kanta tayi tare dayin ƙasa da kai suna dariya.
Nan dai suka shiga sukayi ta hira, sai da aka kira sallan la'asar kana suka tashi sukayi salla.

Bayan an idar da  salla Khadija ne ta kalli Aunty Nana da Garkuwa tare da cewa.
“Bari mu shiga kitchen nida Zulaihat me zamu dafa mana?”.
Da sauri Aunty Nana tace.
“Kuyi mana fried rice tun jiya naso muyi shi”.
Kai Khadijah ta gyaɗa kana ta fita, a Parlour ta samu Laylah da Zulaihat.
“Mu shiga kitchen ko!”.
Tace musu tare da wucewa kitchen ɗin suna biye da ita a baya.

Bayan fitan Khadija da kaɗan Addawa ta shigo gefen Ishmah ta ɗan zauna tare da kallon yadda ta zauna tsakiyar yan uwanta tana tayi musu magiyar bata gaji da suba.
“Hmmm to yanzu dai tashi kije ki ɗan samawa Tajuddeen,abinda zai ɗanci”.
Cikin kulawa da son ɓoyewa ƴann uwanta damuwarta da sirranta matsalar mijinta da ƙaddararsa tace.
“Ya dawo ne?”.
Addawa na miƙewa tsaye tace.
“Eh yanzu ya shigo ya haura sama”.
Ta ƙare maganar tana fita

Ita kuwa Ishmah juyowa tayi ta kalli Garkuwa jin tana cewa.
"Muje to kiyi wani ɗan abin".
Miƙewa tayi tare da bin bayanta ganin tuni tayi waje.

Cikin kulawa ta ɗan kalli Ishmah tare da ɗaga marfin fridge dake kitchen kana tace.
"To me zakiyi mishi".
Tana ɗan kallon Khadija dake gyara fruits tace.
"Abu mai ɗan sauƙi dai, dan yau tunda gari ya waye ba abinda yaci".
Kai Garkuwa ta jinjina tare da buɗe fridge numfashi mai sanyi ta fesar tare da ɗan juyowa ta kalli Ishmah tana faɗin.
"Ya matsalar rashin bacci akwaita har yanzu?".
Da sauri Ishmah ta gyaɗa mata kai.
Kai ta jinjina tare da dacewa.
"To in sha Allah yau zaiyi bacci, zo ki haɗa mishi giyar fulani".
Zare ido Khadijah tayi tare da cewa.
"Ya Salam giya kuma?".
Da sauri tace.
"Eh ta Fulani ba, kuma halattacciya ba haramtacciyaba".
Ta ƙare maganar da fito  da wani roba mai ɗan girma wanda ke cike da kindirmo, sai kuma ta kalli Ishmah tare da cewa.
"Ɗauko blanda can".
Juyawa tayi ta ɗauko tare da ɗauraye cikinsa kana ta ajiyeshi.
Ita kuwa Garkuwa cup tasa ta ɗiba cikinsa uku tasa a bulandan kana ta kalli Khadijah tare da cewa, bani Ripe bananas guda huɗu!.
Ke kuma Ishmah ɗauki coconut ɗin nan ki goge bayanshi".
To sukace baki daya.
Ita kuwa juyawa tayi ta ɗan ɗauki, robar  vanillah Essenes cikin marfin ta ɗan saka a ciki kana ta ɓara Ripe bananas guda huɗu ta saka a ciki, sannan ta haɗa rabin coconut ɗin nan da Ishmah ta goge bayanshi sai kuma tasa sugar tea spoon shida dai-dai misali, kana ta watsa ice a ciki, sannan ta rufe tare dayin blanding inshi dai yadda takeso.
Sai kuma ta kalli Ishmah tare da cewa, kawo Bowl guda biyu masu ɗan girma, ki sasu a tray da kuma table spoon biyu".
Kai ta jinjina mata tare da ɗaukar Bowl ɗin da yafi ɗaukar hankalinta, ita kuwa meda robar nonon tayi kana ta ɗauko na samansa da ta ajiye a gefe wanda furane a ciki.
Kwaya shida ta ɗauki tare da marmasasu cikin nonon kana ta ɗan ƙara yin blanding enshi kaɗan.

Sai kuma ta kalli Ishmah tare da cewa.
"Goge min sauran coconut ɗin".
To tace kana ta fara gogeshi sir-sir.

Ita kuma Garkuwa Ice ɗin ta kuma ɗaukowa ta watsa kusan guda takwas takwas a cikin bowl ɗin kana ta juye damun akai kusan cikasu tayi.

Dai-dai lokacin kuma Ishmah ta miƙo mata coconut ɗin data gogeshi.
Amsa tayi ta watsa akai sai kuma ta ɗan tsinki Grapes kusan guda goma jere guda biyar-biyar tayi kan damun, tare dasa ƴan marafensu ta rufe, kana ta ɗan ƙara gyara killace tsabtar komai na saman trayn sannan ta miƙa mata.
“Gashi ki kai kusha”.
Tana ɗan lasan lip inta na sama tace.
“Hmmm harda ni?”.
Kai ta jinjina mata tare da cewa.
“Yanada amfani jikinki ai”.
Kai ta jinjina kana ta fita.
Ita kuwa Garkuwa sauran ta juyo a Bowl ɗaya, kana tasa guntun a cup Khadija ta miƙa ita kuma ta kaiwa Addawa na hannunta.

A hankali ta gyara zamanta tare da ɗan ƙara matsowa gaba kujerar Dinnin table ɗin.
Spoon ɗin tasa mishi cikin bowl ɗin tare da ɗan motsa ice ɗin da tuni ya narke saura kaɗan-kaɗan cikin sanyin murya da tausasawa tace.
“Dan Allah kayi haƙuri kasha, wannan koda bakaci abinciba, wannan dai ka sha”.
Kai ya ɗan gyaɗa mata tare da amsar spoon ɗin ya ɗan motsa shi ya ɗebo rabin spoon tare da Grapes ɗaya da diddingin coconut ɗin, a hankali ya matso gaban kujerar.
Lumshe idanunsa yayi lokacin da yaji garɗin nono da ɗanɗanon banana ga kuma garɗin coconut da na grape, sai ɗan zaƙi da sanyi daya fito mishi dai-dai yadda yake buƙata.
Cika spoon ɗin yayi a karo na biyu yasa a bakinsa.
“Masha Allah, Babe so sweet”.
Ya faɗa a hankali.
Sai kuma ya tura mata daya Bowl ɗin gabanta cikin sanyi yace.
“Sha, kiji yayi daɗi sosai”.
Tana ɗan lumshe idanunta ta jawoshi tare da fara sha.

Tas ya shanye nasa, sai kuma ya kalleta ganin ta ɗan ture Bowl ɗin gabanta gefe kaɗan alamun ta ƙoshi.
“Ki ƙarasashi Babe”.
Yace cike da taushin lafazi.
Ɗan miƙa tayi tare da cewa.
“Cikina ya cika”.

Sassayan numfashi ya fesar tare da cewa.
“Annabi yace, al'barkar abinci shine na ƙasan kwano fa”.
A hankali ta turo mushi bowl ɗin tare da juya idanunta kana tace.
“Ayyah to ka ƙarasa mana, ni ɗazuma nasha fruits bayan fitanka”.
Kai ya gyaɗa tare da jawo bowl ɗin, fes ya shanye rogowar nata.
Tana Murmushin jin dadi tare da tattaresu tace.
“Taj me zan dafa maka kaci da dare?”.
Ta ƙare maganar tare dasa hannunta kan Tissue box ɗin dake gefen hannunta Tissue ɗin ta

zaro tare ɗan ƙara matsowa gaba, a hankali tayi mishi alamar ya matso da kanshi.
Ɗan matso da kansa yayi sai kuma ya ɗan lumshe idanunsa saboda jin ta ɗaura Tissue ɗin kan lips inshi tana goge lips ɗinshi.
Sassayan numfashi ya fesar yana maijin cikinsa yayi haniƙan a hankali yace.
"No kada ki wahal da kanki, ba inda wani abin zai kuma shiga cikina a dai yau".
Ya ƙare maganar tare da ƙara matsowa da kyau, jujjuya ƙwayar idanunta tayi saboda ganin yayi mata alamun ta matso.
Kai ya jinjjina mata alamun eh matso.

A hankali ta kuma matsowar da ta basu cikekken kusanci.
Cikin sauri ta lumshe idanunta saboda jin ya manne tongue ɗinsa gefen lip inta na sama wanda nono ya ɗan taɓa kaɗan.
Hmmmmmmmmm suka ja numfashi tare.
Sai kuma ya haɗe tafin hannunsu yana mai ɗan lasan lip ɗinta.
Sai kuma tayi ɗan sauri janye kanta jin yana ƙoƙarin haɗe lips ɗintu baki ɗaya.
Cikin sanyi ta miƙe tsaye tace.
"Zanyi maka ɗan abu mai sauƙi dai kaci".
Ta ƙare maganar tana fita.
Shi kuwa a hankali ya kife kanshi bisa table ɗin tare da yin pillow da hannunsa yana mai lumshe idanunsa.

Bayan sallan isha'i zaune suke suna cin abinci.
Kai Goggo Dijan ta ɗan juya tare da kallon Ishmah dake zaune ba komai a gabanta.
"Ya dai Boɗɗin Abba, kici abinci mana".
A hankali ta buɗe baki murya a narke tace.
"Cikina kamar zai fashe, ji nake kamar ma iska ake ɗura min ƙoshin na ƙaruwa".
Aunty Amina ce ta ɗanyi murmushi tare da cewa.
"Ai dama haka damu yake".
Addawa ce ta amshi zancen da cewa.
"Wlh kuwa nima ji nake kamar ƙoshin ake ƙara min".
Cikin sanyi Ishmah ta
Miƙewa tsaye tare da cewa.
"Ga ɗan karen kasalar mayataccen bacci, bari inje inyi wanka ko zan samu baccin ya watse idona ya watstsake dan wlh yau dai so nake muyi kwanan zaune musha hira".
Aunty Nana ce ta ɗanyi ƙasa da murya cikin raɗa tace.
"Ke dai faɗi gsky kwanan zaunen kashe arna da oga ba, ba kwanan zaunen hira da muba, in kin haura sama ai ko motsinki bazamu kuma jiba".
Hararanta tayi da idanunta dake cike da bacci daga nan ta wuce bedroom ɗin dasu Garkuwa suke dan taga nan akwatunanta suke.

Tana shiga ta wuce bathroom dan yin wanka.

Su kuwa a Parlour suna gama cin abinci, Khadijah da Zulaihat suka tattare Wurin kana Zulaihat

tayi wanke-wanke tare da kimtsa komai na kitchen ɗin.
Kusan duk a Parlour suka zauna.

Juyowa Garkuwa tayi tare da kallon Laylah dake kwance gefen Khadijah tayi pillow da cinyarta.
“Jekice Ishmah tazo ta kaiwa Uncle Taj dinner ɗinsa kar ta mance dashi”.
To Laylah tace tare da miƙewa da sauri ta nufi ɗakin.

Tsaye ta samu Ishmah cikin tattausan sleeping dress royal blue da ratsin white da akayisu da zanen heart, sleeping dress ne da zasu tafi da AC weather.
Riga da wando ne, wondon iyakarsa ƙasan guiwa ne kaɗan wanda yake da roba daya kama wurin sai kuma samansa da roba mai ɗan faɗi da ya lafe ya manne kan cikinta da ƙugunta, hakan yabawa mazaunanta damar sakewa sar-sar ciki, rigar kuma mai gajeren hannuce, sai hula, wanda itama ƙasanta keda ɗan roba.
Lumshe idan Laylah tayi tare da cewa.
“Kai my Aunty kinyi kyau, ƙamshin turarenki daɗi”.
Murmushin ta ɗanyi tare da jawo after dress ɗin da ta ciro Black blue ta ɗaura kan kaya, sai kuma ta ɗan sa hula, kana ta juyo ta kalli Laylah dake cewa.
“Aunty Garkuwa tace kizo ki kaiwa Uncle Taj dinner ɗinsa”.
Ɗan sunkuyowa tayi tare da riƙo kafaɗun Laylah cikin sanyi tace.
“Laylah ina son mu zauna muyi hira, zakiyi hira dani ko?”.
Da sauri ta gyaɗa kai tare da cewa.
“Eh sosai ma Aunty Ishmah”.
Murmushin mai haɗe da jin bacci tayi kana ta ɗan sumbaci goshin Laylah kana tace.
“Duk abinda na tambayeki
 zaki gaya min gsky ko?”.
Da sauri ta kuma cewa.
“Eh”.
Sai kuma duk suka kalli Khadijah data shigo tana faɗin.
“Adda wai kije ki kaiwa Uncle Taj dinner, Aunty Amina tace kada a turo ɗan aike na uku fa”.
Cikin sanyi sauti tace.
“Uhmm wlh bacci nakeji”.
Sai kuma ta shafa kan Laylah tare da cewa.
“Yanzu dai jeki Sai gobe zamuyi hirar.”
Da sauri ta juya ta fita.

Ita kuwa Ishmah kamo hannun Khadija tayi suka zauna bakin gado cikin tsananin so da shaƙuwa na ƴan uwa cikin uwa da uba tace.
“Khadija ban gaya miki batun Hamisu da Rahama zasu dawo nan bako”.
Da sauri Khadijah tace.
“Adda Hamisu kuma harda Rahama, ai sunyi yawa karfa muyi rashin pulaku mu ɗaurawa bawan Allah abinda ba haƙƙinsa ba”.
Da sauri tace.
“A haba shi da kansafa ya faɗi haka, kuma ai zai iya ne”.

Cikin sanyi tace.
“Adda da kunya fa”.
Ɗan hararanta tayi tare da cewa.
“Ya dai keda nake zaton zaki tayani shawo kan Abba ya yarda, sai kuma inga ke  ɗinma  kina shirin ƙi”.
Da sauri tace.
“A'a wlh ba haka bane Adda, Amman dai naso a barmin Rahama ai mu koma Gombe da ita, ta fara GSU ai zaifi”.
Da sauri tace.
“To ko in kin ɗauki Rahama ni kuma zaku bani Maamah ko tazo mu zauna tare in haɗa da Laylah kinga na samu yan biyun da nake so”.
Cikin son juna tace.
“Toh Adda am, ai Maamah kam ɗiyarki ce nasan Abbansu bazai hanaba”.
Cikin yin hamma tace.
“Kina dai yimin daɗin baki”.
Dariya sukayi baki ɗaya jin Aunty Amina na cewa.
“To ga yar aike ta uku kam na shigo, Goggnku tace, duk wanda aka aika ya shigo kamar an aiki bawa garinsu, dan haka maza tashi kije ki kaiwa mijinki abinci”.
Ta ƙare maganar da miƙa mata basket ɗin data shigo dashi, wanda aka shirya komai a cikinsa.
Amsa tayi tare da juyawa ta fita.

Tana fita suma suka fito nan suka ci gaba da hirarsu.

A hankali ta ajiye basket ɗin akan Dinnin table ɗin,
Sai kuma ta dawo tsakiyar Parlour tare da ɗan tsayawa ido ta zuba wa wayarsa daketa Vibration.
Dr Abbas ta gani tana kai hannunta kiran na katsewa,
Sai kuma kiran Arfah ya shigo.
Hakanne yasa ta ɗauki wayar tare da nufar bedroom ɗinsa.

A hankali ta tura ƙofar bakinta ɗauke da sallama.

Hummmmmm taja wani irin kasalallen numfashi mai gauraye da nataccen bacci.
A karo na biyu ta kuma jan numfashi saboda wani irin ni'imtaccen ƙanshin da sanyin da yasa baccinta gangarowa duk ya taho cikin idanunta.
A hankali ta buɗe idanunta tare da zubasu a kanshi, zaune yake a bakin gadon, system nashi na bisa cinyarsa da alamun abu yake sonyi Amman masifeffen baccin da yakejin ya hanashi ganin komai.
A hankali ya ɗago kanshi tare da zuba mata ido cikin sanyi suka kuma lunshe idan a tare.

Cikin sanyi murya ta sakeyin sallama.
Murya can ƙasan maƙoshinsa ya amsa mata sallamar tare da yafitota da hannunsa alamun tazo.

A hankali ta fara yin taku tana maijin sanyin tayis ɗin na ratsa tafin sawunta duk da safar da ta saka.

A hankali yasa hannunsa ya amshi wayar da take miƙa mishi, sai kuma ya nuna mata gefenshi tare da motsa lips inshi a hankali yace.
“Zauna”.

A hankali ta ɗan zauna gefenshi tare da ɗan yin gajeriyar miƙa, shi kuwa system ɗin ya rufe, ya ajiyeshi kan bedside drower.
Sai kuma ya ɗaura wayarsa saman system ɗin nasa.
A hankali ya ɗan ƙara matsowa gefentan murya can ƙasan maƙoshinsa yace.
“Babe bacci”. Yayi mgnar yana mai lumshe idanunsa tare da ɗan maida hannunsa duka biyu ta baya  zuciyarsa na amintar da ruhinsa kasancewar Ishmah a gafenshi, a ƙasa ɗaya gari ɗaya gida ɗaya a ɗakin aurensu na Sunnan a matsayin ma'aurata.
Lumshe idanunsa yayi tare da fesar da sassayan numfashi, saboda nazarin zuciyarsa daya fayyacemishi yayi rashi da samu duk a cikin wata ɗaya, ya rasa iyayensa Allah ya samar masa Ishmah ya mallaka mishi ita, domin itace sanyin idaniyarsa mai sama mishi sauƙi da raɗaɗin zazzafar ƙaddarar data ritsa dashi Allah ya sani itace kaɗai zata iya tausasssa zuciyarsa a faɗin duniya shiyasa ya mallaka mishi ita cikin sauƙi.

Cikin kasalar da furar ta sakar musu tace.
“Nima baccin nakeji”.
A hankali ya ɗan juyo ya kalleta.
Cikin sanyi ya ɗan miƙe ganin idonta a lumshe,  hannunsa yasa ya ɗan tattare jallabiyar jikinsa tare da murza robar boxer ɗinsa yayi ƙasa dashi.
Numfashi mai sanyi ya fesar lokacin da yayi ƙasa da Boxers ɗin nasa, saboda jin cinyoyinsa da Taj ɗinsa sun sake yadda yake muradi.
A hankali ya sunkuyo tare da zareshi duka.
 Yana ɗagawo da Boxers ɗin a hannunsa tana buɗe idanunta, da sauri tayi ƙasa da kanta tare da maida idanunta ta lumshe shi kuwa Taj a hankali ya ida nade shi tare da cilla shi bisa kujerar dake gefensu.

Sai kuma ya zauna bakin gadon tare da hawar da sawunsa duka.
“Kinyi al'wala?”. Ya tambaya cikin murya kasala da bacci, kanta ta gyaɗa mishi.
Ganin haka ne yasa ya ɗan matsa gefe can kana ya jawo hannun ta, murya can ƙasan zuciyarsa yake faɗin.
“Zomu kwanta tare ko zan samu inyi bacci kamar jiya”.
Ya ƙare mgnar tare da tattare blanket ɗin kan gadon, da hannunsa ɗaya yayinda ɗaya hannun kuma ke jawota, kusa dashi.

Yana gyara mata pillow yace.
“Bismillah kwanta”.
Cikin sanyi da jin wani fitinenne kasalar bacci, ta ɗan kwanta tare da fuskantar alƙibla haka yasa

ta bashi baya.
Nannauyan numfashi ta fesar, tana mai nazarto kasantuwarsu ma'aurata yana ƙara sa tsikar jikinta tashi.
A hankali ya warware naɗin da yayiwa blanket ɗin har zuwa saman ƙirjinsu,
Sai kuma ya gyara zamansa cike da kasala yayiwa kansa addu'a ya shafa, kana ya sake yin addu'a ya tofa a hannunsa.
A hankali ya juyo ya fuskanceta.
Hannunshi yasa ya jawo hannunta ya juyata rigingine.
Uhhhhmmmm shine sautin da suka saki a tare, lokacin da ya kife tafukan hannunsa kan lallausar fatar fuskantar,
A hankali ya fara yin ƙasa da hannunsa yana shafa mata addu'a ta ko wani sasan jikinta.
Shmmmmmm ya furta a hankali lokacin da ya dire hannunsa kan fatan wuyanta.
Sai kuma ya lumshe idanunsa a hankali a dai-dai lokacin da ya dire hannunsa ƙan ƙirjinta.

Da sauri ta rumtse idanunta da ɗan kare ƙarfi, saboda wani irin yam-yam da tsikar jikinta ya fara zubawa.
Shi kuwa Taj a hankali yaja wani kulafataccen numfashi, duk da kuma damuwar data Addanbi zuciya da ruhinsa bai hanasa jin wani baƙon yanayin ba, sai dai ƙarfin damuwar tayi nasarar tauye ta'azzarar mayatarsa ya duƙufar da kuzarinsa kaso 60 cikin ɗarin.
A hankali ya shafe mata dukkan jikinta, sai kuma duk suka sauƙe ajiyan zuciya a dai-dai lokacin daya konta gefentan gab da ita, har tana jin ɗumin numfashinsa.

Nigeria
A dai-dai lokacin kuma Dr ne kwance bisa kujerar a fili yake faɗin.
“Wannan Ustas ɗin ya watsa min shiri na, ya hargitse min duk maitar kwaɗayi na, nason jin irin ɗanɗanon ni'imar dake jikin Ishmah, wacce na tabbar zatayi min zaƙi fiye da duk matan da na sani”.
Sai kuma yaja dogon tsaki tare da miƙewa tsaye kayansa da dukiyar aurensa da Abba yasa Yah Abubakar ya dawo mishi dashi ya kalla cike da mamakin ganin tsinkensa basu taɓa ba. A fili yake faɗin.
“Duk da dai hakan ya zama sanadin kareni da yin dakon zunubin cutar da ita wurin raɓa mata HIV, Allah ne ya kareta, Afif ya zame mata Garkuwa Yah Allah ka bani dai-dai dani mai irin ciwona mu rufawa juna asiri.

Ethiopia.
Kwance take tayi lip ta rufe jikinta daga sama har ƙasa, wayartace a hannunta hotonshi dake fuskar wayar tata ta zubawa idanu babu ko kiftawa cikin murya mai cike da yanayin muradi tace.
“Kai wannan na mijine, cikekken namijin duniya, duk inda Namiji yake ya kai namijin da ko wacce mace take fatan mallakar irinsa Ya Allah kasa in samu na Habibina ma haka yake”.
Sai kuma ta fesar da numfashi tare da juyawa ta kwanta a kife cike da begen makusanci a gareta Allah ya sani ita macece mai muradi.

Doha Qatar.
a hankali ya ɗan yunƙuro kanta saboda jin yadda take sauƙe numfashi alamun bacci ya fara nasarar yin awon gaba da ita, kanshi ya ɗan ɗago matso da lips inshi yayi dai-dai kunnenta cikin raɗa yace.
“Babe! Babe!!”.
Sai kuma ya ɗan ƙara matsota cikin sanyi ya kuma kiranta yana mai ɗan ɗaura ƙafarsa ɗaya kan cinyoyinta.
“Hmmmmmm”. Tayi sauti alamun ta amsa.
“Babe zan rage Miki kayan nan sunyi miki yawa a jiki”.
Ya ƙare maganar yana zame mata hannunta cikin after dress ɗin.
“Hmmmmm”.
Ta sake faɗi Murmushin gefen baki yayi domin ganin yadda duk jikinta ya sake.
A hankali ya zare mata ɗaya hannun ma.
Ya zamana tana kwance ne kawai a samansa.
Komawa yayi ya kwanta tare da jawota jikinsa ya ɗaurata kan cikinsa ya manne kanta bisa ƙirjinsa.
Sai kuma yasa hannunsa ɗaya ya tattare after dress ɗin ya cilla shi can bisa kujera, blanket ɗin ya jawo ya rufe musu jiki, kana ya ɗaura tafukan hannunsa bisa bayanta yana ɗan shafawa a hankali yanayin sama da ƙasa dasu tare da ɗan mammatse wuyanta kamar maiyi mata tausa.

A hankali yaji idanunsa na lumshe,
ƙamshin jikinta ya kuma shaƙa a karo na barkatai tuni bacci yayi awon gaba dasu manne da juna.

Ethiopia
Washe gari da safe misalin ƙarfe tara.
Yah Aryan ne, zaune a Parlour Ummu Aryan ɗin, bisa alamu waya yakeyi da ɗansa Arfah cikin takaici yace.
“Wai ni Arfah anya kuwa ko ni ubanda da na haifeka kana sona kamar yadda kake son Afif wannan wanne irin nacin tsiyane da jarabar mayata shi yana can yana harkokinsa da karuwansa yama mance daku, kai ka buwayeni”.
Cikin takaici Arfah yace.
“Wlh Uncle Taj ba mazinaci bane, Dad ka daina faɗan haka”.
Cikin tsawa yace.
“To ubana yanzu dai saura ka rufeni da duka kawai ko. Maza gimtse wayar wlh in ka sake min mgnar Afif cin ubanka zanyi hegen yaron mai nacin jaraba”.
Jin haka ne yasa Arfah katse kiran kana yayiwa Imaran bayanin yadda sukayi da mahaifinsa ya ɗaura da cewa.
“Nifa gani nake kamar Abba na baya son Uncle Taj”.
Da sauri Imran yace.
“A'a Arfah kada ka faɗi haka, ya zaiyi ya ƙi ɗan uwansa yanzu bari in sake gwada kiran Uncle Taj ɗin”.
Ya ƙare maganar da kiran Taj ɗin, a hankali ya juyo ya kalli Arfah cikin sanyi yace.

“Layinsa baya shiga bari sai anjima in sake gwadawa”.
ranar dai haka sukayi ta gwadawa Amman bata shiga.

Qatar
Ƙarfe Goma dai-dai jirginsu Aunty Amina, Goggo Dija, Aunty Nana, Garkuwa, Khadija, Adam.
Ya ɗaha daga Doha Qatar zuwa Abujan Nigeria.
Sai da suka ga tashinsu kafin, Taj da Ishmah suka fito Airport ɗin suka nufi gida.

Bayan sun dawo gida
Kwaɓe ta tsuke tare da tura baki, ɗan gajeren murmushin yayi tare  da cewa.
“Afwan laifin me nayi ne wai?”.
Ya ƙare maganar yana ɗan zamewa ƙasa ya zauna gabanta bisa kujerar.
Murya can ƙasan cikin dishewa alamun tayi kukan tafiyarsu ta ɗan kalleshi kana tace.
“Shike nanfa sun tafi sun barni ni ɗaya, yanzu bani da kowa a ƙasar nan”.
Da sauri yace.
“Babe ba gani ba, Taj ɗinki fa, bakiji me Abba yaceba”.
Cikin sanyi tace.
“Naji”.
Miƙewa tsaye yayi tare da cewa.
To taso muje mu kwanta ki samu ladana Inyi bacci Kinga sai naji ɗimin jikinki nake iya bacci”.
Cikin ƙasa da murya tace.
“To Amman banda cire kaya”.
Hancinta ya ɗan lakace tare da cewa.
“Jiyama ke da kanki kikace in cire miki, da izininki na cire Miki ai kuma ai ba kaya na cireba”.
Ya ƙare maganar da jan hannunta suka nufi Bedroom.

Alhamdulillah washe gari ranar Monday aka buɗe Al-AHLI AFISHA HOSPITAL, Ify duk Doctors and Nurse's da cliners sun fara aikinsu babu kama hannun yaro buɗe asibitin kuwa yazo da gagarumin nasarar da tasa duk Qatar aka san da asinitin saboda  wata balarabiyar da aka cirewa yara tagwaye biyar reras uku maza biyu mata, kuma duk suna Ify.

Acan Nigeria ma Alhamdulillah sun isa Ify ko wacce ta koma gidanta sai Khadija da Goggo Dijan ne da suke ɗan ƙara huce gajia kafin su koma Gombe.

Bayan kwana uku, wanda ya kama yau kwanansu goma kenan da zuwa Qatar.

A Parlour suke shi da Ishmah da Addawa yayinda Zulaihat da Laylah suka fita suna can baya suna lilo.

Ido Addawa ta ɗan zuba mishi saboda ganin yadda ya zauna yayi tagumi da hannun biyu.
“Zuwa yanzu dai ya kamata ace, ka bar duk wannan damuwar tunda Ishmah dai tayi maka

kekkyawar fahimta."
Nannauyan numfashi ya sauƙe tare da cewa.
"Ya za'ayi hankali na ya kwanta bayan kuma ance Laylah nada ciki, kinga tana cikin matsala an cuceta anyi mata fyaɗa da ƙanan shekarunta, sannan ance tana da ciki".
Cikin kaɗuwa da tsoro Ishmah ta ɗan zaro idanunta waje tare da cewa.
"Innalillahi ciki kuma Addawa, to wai wanne mara imanin ne yayi mata fyaɗen nan kuma ace harma da ciki?".
Cikin sanyi Addawa tace.
"Abinda kenan har yau bamu ganoba, mun kasa gano ko binciko wanda yayi mata fyaɗen har ya narka mata ciki".
Cikin tausayawa da ƙunan rai hawaye na cikowa Ishmah tace.
"Ba komai wlh na rantse da Allah in sha Allah sai na binciko wanda yayi mata cikin nan kuma sai an gano shi ya amshi hukuncinsa in sha Allah zan yi bicike kan lamarin".
Ta ƙare maganar da yaƙini.
Addawa kuwa bayanin duk yadda abubuwan suka faru ta labartawa Ishmah sai dai bata faɗi mata sharaɗin Malam na cewa muddin Taj ya bari ya haɗu da wani dangi nasa ko yayi mu'amala da ahlinsa ba, a bakin auren Ummeeysa.
Tadai gaya mata yace ya ciresa a yaransa baya kuma bukatar sake ganinsa ya kuma ce ya raba sunansa da nasa kasake tayi tana jin Addawa cike da nazari da zurfin tunani a hankali tace.
"Tajj anya kuwa ka gwada Laylah da kanka? Anyama akwai wannan mgnar, nifa gani nake nakircine kawai da iya tsara gadar zaren kai kuma ka rubta ciki kuma ka rasa mai tayake warwarewa".
Cikin sanyi yace.
"Ma'eesha kiga yadda Laylah ta sauyafa duk alamun ciki bayyana gareta".
Cikin nazari tace.
"Hmmm Tajj kamar ba likitaba kawai sun haɗa ma zafi kan zafine da fushin Yah Abana shiyasa baka iya tuna komai ba.
Amman in sha Allah zan nazarci lamarin".
Kiran salla Magrib da shigowar su Laylah ne yasa suka watse taron nasu.

Misalin ƙarfe tara na dare.
Zaune take a bakin gadonta yayinda Laylah ke gabanta cikin nitsuwa da kuma son kwantar da hankalin Laylah da son gane abinda ke ɓoye tace.
"Laylah tashi in aikeki wurin Uncle Taj."
Da sauri ta zazzaro idanu tuni jikimta ya fara rawa murya a firgice tace.
"Afwan Aunty Ishmah ina tsoro, ni bazan jeba".
Cikin tsareta da ido tace.
"To Laylah me kike tsoro wai? Uncle Taj ɗinkin nefa, me zai Miki?".
Cikin rawan murya da jiki ta ƙara matsowa jikin Ishmah cike da tsoro tace.
"Ni dai ina tsoronsa tunda yake cemin zai yankani in ban bari yayi min cikiba".
Ya Salam shine abinda Ishmah ta faɗa cike da ɗimuwa da mamaki gami da firgici tace.
"Laylah Uncle Taj ɗin naki ne yake cewa zai yankaki in baki bari yayi miki cikiba, cike da gskya

da gskya tace.
“Wallahi shine tunda mukaje Nigeria muka dawo, duk randa ya dawo Ethiopia a ɗakina yake kwana kuma sai yace in nayi ihu zai kasheni kuma in bari yayi min ciki, wai kuma kar in gayawa Aunty Meymey”.
Far-far jikin Ishmah ke rawa da tsuma, da sauri tasa hannunta duka biyu ta riƙe kanta saboda zafi da raɗaɗin kalaman Laylah yasa kan nata fara sarawa da ƙarfi, sai kuma ta buɗe bakinta da ta samu numfashi ya dai-dai saboda jin numfashinta na cizga.
“Yah Salam wannan makircine aka ƙullawa Tajj aka ɓatashi a gaban ƴar da yakeji shi ya haifa” .
Ta ƙare maganar zuci tana mai rumtse idanunta saboda jiri data fara gani.
Ita kuwa Laylah cikin Tsananin kukan rauni da ruɗu taci gaba da cewa.
“Har bindiga yake nuna min, yace min in cire kayana”.
Da sauri Ishmah ta riƙo hannun Laylah cikin son gano gskyr da takejin tsoron in ya tabbata cewa anyiwa Laylah fyaɗe nan tabbas zuciyarta zata buga domin tasan har abada yarinyar bazata yarda ba shi bane.
Murya na karkarwa tace.
“So sorry Laylah, kiyi haƙuri daina kuka, gaya min gsky tsakanin ki da Allah Uncle Taj ɗin ne, yake miki haka kin ganshi da kyau da haske lokacin da yake shiga?”.
Cikin shesh-sheƙan kuka ta fara gyara murya cikin gskyar lamarin da fahimtar yarintarta tace.
“Eh ko na kashe wutama, yana shiga yake kunna wuta, ya cire kayansa yace nima na tuɓe, kuma ya kwanta kan g...”
Da sauri tayi shiru ba tare da ta ƙarasa mgnar ba, saboda jin  Yadda Ishmah ta saki wani irin.....

*Littafin INDA RAI na kuɗine ki biya ki karanta cikin aminci da salama 1k ne rak 0661110170 GTBank Aisha Aliyu Garkuwa, sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276 mutanen Niger kuma 1000fc ne jaka ɗaya kenan rak zaku biya ta wurin Mommy +22790899076 idan kika karanta min littafina baki biyaba wannan ke da Allah*

By
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 📝🕋💉🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*INDA RAI*
*BOOK 2 PAGE 6*
*AYASHA ALIYU GARKUWA*

*Bononza! Bononza!! Bononza!!! Kayan Mata na musamman. Kuɗi nake nema wuri janjau yaseen saboda inada abin yi dasu!!! Yoh ace min turo account no  ma kaɗai yana sani farin ciki, inaga kuma inga alerts na zubowa kamar ruwan sama, toh wannan shine sirrin rashin raina

Customers ɗina, ina yinku ina ganin girman yardar da kuke min saboda wasu ko mgna bata taɓa haɗani da suba sai kawai su turi dubban juɗaɗensu kafin ma suzo suce min ga abinda suke, wlh hakan kan sani jin in mutuntasu sabida ai yardace ta kawo haka, yinku ina sonku domin kuna sani farin ciki. Shiyasa nake sake muku Garaɓasaa kamar bansan cewa komai na rayuwa ƙara tsada yake ba. Kuɗi nake so da zafi zafinsu, Ku zo ku sayi kayana.Yauwa kina ji ko ni ba bashi ko maula ko alfarmarku nake nemaba!!. A'a talla nake muku ku bani kuɗi niko in baku kaya ɗa'a.🤝😘🤣*
*Da ɗumi-ɗuminsa Set ɗin mgnin infection 8k kunga garaɓasa har 2k half 4k Dadiharmadiga 4k maliƙi 5k ragi har na 2k robar Ƙasaitacciyar mace 5k ragi har 2k botikin gumbar 9k a 8k ƙananan robobiin garuka gumbunan da tsumi na 3-3k duk a 2,500 kunga ragin dari biyar biyar ai ba wasaba, haɗin kazar 20k a 17k na 15k 13k garin babambaɗe 4k al'ajabu 4k idan kuma kayanki ya kai na 50k zuwa sama in dai arewa kike to Free Delivery ne sis. In kuma na 40k 35k 30k 25k ne kuwa gareku Kanawa, Gombawa, Josawa, Jigawa, Bauchi, Taraba, duk Free Delivery ne kuma! In kuma kayanki ya kai na 60k 70k 80k 90k zuwa 100k kinada tukuicin ɗan haɗin humra da kulacca da turaren wutan ga kuma free delivery. Nace ba tsaya mana kiji, inafa araha kam Amman ina hana bashi, kuma wannan Garaɓasar daga yanzu ne yau ɗin nan laraba 24-01-2024, zuwa 01-2-2024 cib Garaɓasar zata sauƙa so ko kada ki karanta tallan bayan nan kizo kice ai naga kince kaza da kaza da Free Delivery da sauƙin farashi, ɗaya ga watan biyu na shekara dubu biyu da ashirin da huɗu na gotawa koda one minute ne to fa garaɓasa ta fece. In a shirye kike ga account no. 0005388578 Jaiz bank Aisha Aliyu Garkuwa sai ki hankaɗo min shaidar biyanki ta Whatsapp number na 08069423567. Maliƙi da ddhmdg abin 12k Amman a 10k Garaɓasar ma ai tayi yawa gaky, 10k fa wannan kayan alkhairi Please dan Allah in kinsan baki shirya sayaba, kada kizo ki ɓata mana lokacinmu ki hutar da kanki nima ki hutar dani.*

Ya ƙare maganar da narke kwayar idanunsa cikin nata, wanda hakan yasa jikinta yin wani irin fitinenne macewar da har yasa muryarta narkewa can ƙasan maƙoshinta tace.
"Tun yanzu?".
Yana mai zira mata wasu fitinanuna lamura ta cikin gajiyayyun idanunsa ya motsa lips inshi a hankali yace.
"Eh muje".
Ya ƙare maganar tare da juyawa ya kalli su Addawa da Goggo Dija da Aunty Nana dake cewa.
"Maza tashi ku tafi".
Ɗan rusunar da kansa yayi tare dayi musu sallama kana ya nufi hanyar fita.

Ita kuwa Ishmah ƙara matsowa tayi a jikin Aunty Amina tayi tare da yin rau-rau da ido sabida jin Aunty Amina na cewa.
"In sha Allah Jibi da dare dai zamu tafi, in Allah ya yarda sai kizo gobe mu wuni!".
Cikin sanyi tace.
"Dan Allah ku bari mu ƙara sati".
Ɗan ture kanta Aunty Nana tayi tare da cewa.
"Tafi daga nan, da muke nan ɗinma tunda muka zo, bamu ga idonki ba sai yanzu, ke gaki yar

miji dadi, muma da mazanmu, dan haka  baza mu zama ƴan amshi shata ba”.
Dariya sukayi baki ɗayansu.
Garkuwa kuwa hannun Ishmah taja tare da cewa.
“Zo muje daga ciki”.
Da sauri ta miƙe sai kuma ta kalli Goggo Dijan dake cewa.
“Kada dai ki mance mijinki na jiranki a waje”.
Da sauri Aunty Nana tace.
“Laa dama kinyi shiru Goggo ai bazata manceba”.
Khadijah ne ta ɗan harari Aunty Nana tare da cewa.
“Uwar sa ido ba”.
Sai kuma duk suka kalli Addawa ganin ta miƙe tsaye tare da cewa.
“Ai gwara ta bada himma ta kular min da jikana ta sama mishi farin ciki, in tayi mana haka mu ta gama mana komai na rayuwar duniya”.
Cikin gamsuwa da hafimtar kalaman Addawa Garkuwa taja hannunta suka nufi ɗakin.

A bakin gado suka zauna cikin kulawa da fahimtarwa ta tsare Ishmah da ido cikin yin ƙasa da murya tace.
“Da alama dai kin gaza kwantar da hankalinki bare ki kwantarwa mijinki nashi hankalin”.
Ajiyan zuciya mai nauyi Ishmah ta fesar tare da gyara zamanta kana a hankali tace.
“Na rasa me yake damun Taj, sam ba haka yakeba, na fahimci yana cikin tsananin damuwar da ko bacci baya iyayi fa my Aunty”.
Ta ƙare maganar cike da damuwar hakan.
Tsuke fuska Garkuwa tayi tare da cewa.
“To ai duk laifinki ne Ishmah, ace kina mace macen ma data san zaman duniya da haƙƙin miji, ace ki kasa kwantar masa da hankali da sama masa nutsuwa zuciya, har damuwa ta hanashi bacci kina kuma tare da shi a muhalli ɗaya anya kuma Ishmah baki zama lusarar maceba.
Kin kuwa san tabbas ya ɗaukekine ya tafi Hotel dake dan ku samu hutun jiki dana zuƙatane, keda kanki kika cemin yana cikin damuwa mai tsanani fa,
Kin kuwa ga kenan ya nemi kusanci da kene domin yana zato da yaƙinin kece farin cikinsa, kece zaki sawa zuciyarsa nitsuwa da tausarsa ki kwantar mishi da hankali ki cire masa damuwar dake tare dashi, Amman ace haka ya gagara kina tare dashi wuri ɗaya, ɗaki ɗaya, kai gado ɗaya ƙarshenta ma pillow ɗaya, cikin blanket ɗaya, Amman ki kisa zama ƙasaitacciyar macen da zata sa mijinta bacci wlh Allah kin bani kunya Ishmah.”
Cikin sauke numfashi tace.
“A'a my Aunty wlh tunda mukaje iyakarsa a ƙasa bakin gado, ko gefen bai taɓa zamaba.”
Sai kuma ta ɗan lumshe idanunta kana ta buɗesu ta zubasu kan Garkuwa dake yi mata kallon mamaki a hankali tace.
“A zaunefa yake kwana yana karatu, wani lokacin ma kuka ne yake fizge muryarsa.”
Cike da takaici Garkuwa tace.
“Innalillahi Ishmah dan Allah ke bakya jin tausayinsa, kinfi kowa sanin Taj kin dai ga zahiri damuwa tare dashi wai ke wacce iriyar mace ce?”.
A sanyaye tace.
“Ni nayi zaton yana damuwa ne da auren bazata da yayi min, dan akan haka yaketa bani

haƙuri, yana jaddada min shi masoyine a gareni".
Sai kuma sukayi saurin kallon bakin ƙofar jin sallamar Addawa.
A tare suka amsa mata, jin sun amsa mata ne, yada ta shigo fuska ɗauke da Murmushi, a gefen Ishmah ta zauna ya zama sun sata a tsaki cikin sanyi tace.
"Ishmah wurinki nazo".
Tana ɗan juyowa tace.
"Toh Addawa gani".
A hankali ta ɗan sauke numfashi kana ta kalli Garkuwa tare da cewa.
"Aysha, ƴar ɗakin kin nan fa tana bukatar tunasarwa".
Da sauri Garkuwa tace.
"Sosai ma kuwa Addawa".
Kai ta jinjina cikin hikima ta fara mgna.
"Kallo ɗaya nayiwa Tajuddeen na fahimci cewa har yanzu yana cikin damuwar data samu baro Ethiopia zuwa nan Qatar, damuwar da take sirri a gareshi, ya kuma roƙeni da in sirranta masa shi, da banyi mishi wannan al'ƙawarin ba, da zan baku dukkan labarin abinda ya faru, wanda nakeda yaƙinin in kinjin zaki ruɓanya kulawarki gareshi, zaki tausashi zuciyarsa ki sama mishi farin ciki koda kaso 30 cikin 100 daya rasa, to dan Allah ki taimaka kiyi azama da hikima sashi bacci, domin zuciyarsa da kwakwalwarsa su samu su huta da azaban damuwar dake cikinsu".
Wani irin fitinenne rauni tausayin Taj ɗinne ya rinƙa narke zuciyarta wanda har ya tsinko mata hawaye.
Garkuwa ko kai take jinjinawa cike da tausayi, sai kuma suka kalli Addawa ganin ta riƙo hannun Ishmah tare da cewa.
"Ya nemi kusanci da kene da yaƙinin duk duniya kece kaɗai farin cikinsa, burin zuciyasa, kuma sanyin idaniyarsa, na fahimci cewa yana jinki a jiki da zuciyarsa da yarda ko kowa zai juya mishi baya a duniya ke zaki fuskanceshi.
Please Ishmah dan Allah ki kular min da Tajuddeen ki ɗebe mishi kewa ki sashi farin ciki, ki mantar dashi abinda ya faru dashi kwanaki goma sha biyu da suka shuɗe, ki kusantar dashi da bacci dan zuciyarsa ta huta sannan ki kula da cikinsa kada yunwa ta lahantashi".
Cikin sanyi murya cike da aminci tace.
"In sha Allah".
Sai kuma ta ɗan kalli Garkuwa dake cewa.
"Kin dai ji ko, dan Allah ki watsar da raunin kin nan, na koke-koken kin bar Hamisu ƙaton gardi, ki ruggumi mijinki ki faranta mishi rai sai kema Allah ya faranta miki".
Sai kuma tayi ɗan kasake tana jin Garkuwa na bata dabarun samawa miji bacci da dai sauransu, yayinda Addawa ta ɗaura da nata.
Kusan 30 minute sukayi suna ƙarfafa mata guiwa.
"Yauwa tashi kije yana jiranki, dama na kirashi nace ya bani 30 minute zaki fito."
Cewar Addawa tana miƙe tsaye tare da kamo hannunta.
Ita kuwa Garkuwa cikin juya harshe zuwa hausar da tasan Addawa bataji tace.
"Ya batun kayan ɗa'a da kullaccar sirri da shu'umar humra in baki sune".
Cikin yarda da kai tace.
"Ai kullacca da humra akwaisu a hand bag na, kaya kuma barsu, in sha Allah gobe zamu bar hotel ɗin zamu dawo gida, dan zanfi samu nitsuwar nesantashi da yunwa da kusantashi da

bacci”.
Kai Garkuwa ta jinjina cike da gamsuwa.
Daga nan suka fito ta sallami su Aunty Amina kana ta wuce ta fita.

Su kuma suka zauna a Parlour sukaci gaba da hira.

A Corridor ɗin sukayi kiciɓis da Adam da Bilal, hannu Adam ya bata sukayi musabaha kamar yadda mafiya akasarin lokuta haka suke gaisawa, sai kuma ta amsa gaisuwar da Bilal keyi mata, cikin murmushi tayi tare da cewa.
“Wai ya naga ka zama wani ƙaramin ba Ethiopia ne kam”.
Cikin ɗaga kai Adam yace.
“Aha wani ba Ethiopiaye ko! Ba Balarabe ba, ba kullum tsiya kukemin kuce duk cikin mahaifiyarmu nine baƙi ba, ina gaya muku ni kalata mai tsadace tamafi ta larabar kyau tunda kin yarda nayi kalar Ethiopia yawa”.
Tana Murmushin tace.
“Yaban kai dai...”
Da sauri ya amshi mgnar tare da cewa.
“Ilimi ba”.
Kusan a tare suka juyo suna biye da ita a baya. Bilal ke cewa.
“Yauwa dama Uncle Taj yace ki fito ku tafi”.

A bakin motar suka tsaya, sai kuma suka ɗan fara jujjuya kai, can gefen motar suka hangeshi zaune bisa kujerun silver dake jere a wurin.
Bilal ne ya buɗe mata marfin motar, Adam kuwa wurin Taj ɗin ya nufa jim kaɗan suka dawo tare.

Baya ya shiga gefentan, kana driver'nsa dake can bakin gate wurin mai gadi ya taso da sauri yazo ya shiga, kana yaja suna tafi.

A hankali ya ɗan juyo ya kalleta dai-dai lokacin da suka fita harabar gidan, cikin kulawa da tasayawa tace.
“Kanka na ciwo ko”. Tayi mgnar tana kallon yadda idanunsa sukayi da kuma yadda jijiyoyin kansa suka ɗan tashi, kai ya ɗan jujjuya mata alamar a'a.
Sai kuma ya ɗan kalli wayarsa dake ringing.
“Ka ɗauka mana”.
Ta faɗa tare da gyara zamanta.

Sallamar da Dr Abbas yayi masa ne ya amsa cikin sanyi da rashin bacci ya sakar masa da cushewar zuciya gami da tunani dan har wani juyawa yakejin kansa nayi.
“Afif wai me nake ji ne?”.
Cewar Dr Abbas yayi tambayar cike da damuwa.
“A ina ɗin!”.
Taj ɗin ya amsa mishi tamyarsa da tambaya.

Murya cike da ruɗani yace.
“Dazu da Yamma Yah Aryan da Kabir suka zo da Malam, sun cire komai na sunanka sun meye gurɓinshi da sunan Kabeer TAJMUH CONSOLATION HOSPITAL ma sun maida shi ARKABMUH CONSOLATION HOSPITAL sun haɗe sunan Aryan Kabeer dana Malam, sannan sun soke sunanka a komai, kai kuma nayi maka text message ba amsa meke faruwa, harfa da cireka a matsayin Dr asibitin an meye sunan Kabeer a gurbinka shida yaushe ma ya gama karatunsa”.
Yana ɗan lumshe idanunsa yace.
“Eh na sani, ba matsala ai”.
Da sauri Dr Abbas yace.
“Zurfin ciki ko? Wai ni kake cewa ba matsala, bayan duk abinda ya faru Yah Aryan ya gaya min! Sannan kuma naga kabar ƙasar ka koma Qatar harma da ɗiban ma'akata sama da mutum 100.”
Shiru Ishmah tayi domin tana iya jiyo duk abinda Dr Abbas ke faɗa can ƙasa.
“Eh na bar wannan asibitin ne, na dawo nan Qatar zan kula da sabon Asbitin dake wurin”.
Da sauri Dr Abbas yace.
“Ok nima zan bar musu aikinsu na nan, zan dawo Qatar ɗin mu kula da wannan”.
Da sauri Taj yace.
“Please Abbas kada muyi haka da kai, ka zauna ka taya Kabeer kula da nan”.
Tsaki mai tsawo Dr Abbas yaja tare da cewa.
“Anƙi zaman, ai kai kasan dama dan kai nake aiki a nan, Dr Farida ma tuni tayi ajiye musu aikinsu.
Nima kuma na rubuta takardar barin aiki nama tura musu.
Kuma ina nan tafe Qatar”.
Ya ƙare maganar tare da katse kiran.
Kanshi ya ɗan jingina jikin kujerar motar a kuma dai-dai lokacin suka shiga cikin hotel ɗin.

A hankali suka kutsa kai cikin Parlour,
Numfashi mai sanyi ta fesar tare da lumshe idanunta saboda sanyin wurin yafi na cikin gari ta fahimci cewa suma watannin sanyinsu da zafi da damuna kamar namu ne, dan yanzu kusan ƙarshen damune dan yau ne 12 September.
Ido ta ɗan zuba mishi ganin ya zauna bisa kujera tare da sa hannunshi duka biyu ya riƙe ƙansa.
Bedroom ta wuce, tana shiga ta faɗa bathroom broch ta farayi kana tayi wanka  tare da al'walan bacci.

Tana fitowa ta tsane jikinta da baby towel, sannan ta murza kullaccar sirri tare da ɗan shafa shu'umar humra.
Wasu tattausan riga da wondo na bacci maroon color ta ɗauka wondon bai sauƙan mata har ƙasa sosai ba, da kaɗan ya wuce guiwa, rigar kuma mai gajeren hannunce, tayi cib da jikinta sai hular kayan da ta naɗe gashinta ta cusa a ciki.

Dai-dai lokacin kuma ya shigo.
Ba tare da yace mata ko ƙalaba ya wuce bathroom.

Ita kuwa a hankali ta zauna bakin gado tare da haɗe tafin hannunta tayi addu'o'in kwanciya bacci, ta shafa kana ta miƙe ta fita Parlour.
Jin wayarta na tsuwa ganin Maryam ce yasata amsawa da sauri.
“Amarsu ta ango duk kin mance damu kin ruggume miji, su da sukaje rakiyarma gudunsu kukayi bare mu da muke nan ko”.
Dariya tayi tare da cewa.
“Sherrin Aunty Nana nefa”.
Itama Maryam dariya tayi tare da cewa.
“Toh a dai ragewa arnan Qatar dangi kaɗan kada a ƙarardasu a mako ɗaya”.
Tana lumshe idanunta tace.
“Toh ai dama Qatar ba ƙasar zamansu bane, gwara kawai mu kashesu duka a mako ɗaya mu samu ladan jihadi”.
Cikin ƙelkel Maryam ta fashe da dariya mai sauti har Saida Yan Abubakar yace.
“Ke Ify kuwa”.
Ganin haka ne yasa ta fito Parlour.

Bayan sun gama wayarne kuma tayi saurin juyowa ta kalli wayarsa dake ringing.
*Arfah* ta gani a fuskar wayar.
Haka yasa ta ɗauka tare da nufar bedroom ɗin.
Wani irin ni'imtaccen ƙanshin ne ya bugi hancinta da zuciyarta har yasata lunshe idanunta, kana a hankali ta buɗesu a kansa.
Tsaye yake cikin wata tattausar jallabiyarsa Morning sky mai masifar sheƙi da sulɓi, sai baza ƙamshi yake tamkar fure, ido suka zubawa juna tamkar yau suka fara ganin juna.

A hankali ya ɗan fara taka ƙafarsa yana tahowa gabanta.
Wani nannauyan numfashi ta kuma fesarwa tare da fara kallonshi daga saman rumfar sawunshi tanayin sama da idanunta a hankali.
Shi kuwa Taj tafiyar yake cikin sakewa da jin daɗi da yake ji a duk lokacin da ya kasance daga shi sai jallabi ko giltan baccinsa da yake ɗaurawa, Allah ya sani shi baya iya kwana da wani abu a jikinsa, jallabiyar ma da yake sawa dan itane, tunda ya kai shekaru takwas daya koma gidan Addawa kasancewar dakinsa shi kaɗai  yake kwana da giltan, giltan ɗan wani tattausan fellen yadukane masu masifar taushi wasu daga ciki kuma masu sulɓi so su yake ɗaurawa yayi bacci dan bayi son takura Taj ɗinai.
Tafiyar da yake yi ne kuma ya bashi  damar motsawa da bayyana kansa sosai a cikin jallabiyar wanda ganin haka ne yasa Ishmah saurin rumtse idanunta tare da kauda kanta.
Sai kuma ta miƙa mishi wayar jin kiran ya kuma shigowa.

Yana amsar wayar ta wuce ta gefenshi a bakin gadon ta zauna tare da jawo pillow ta kwanta.

Shi kuwa kashe wayar yayi baki ɗaya, kana ya dawo ya zauna a ƙasa bisa Carpet ɗin a hankali ya jingina bayanshi da jikin gadon sai kuma ya ɗan juyo ya kalleta murya a sanyaye yace.
“Babey Kiyi addu'a ko”.

Kai ta jinjina mishi tare da buɗe hannunta ta fara addu'an.

Shi kuwa Taj a hankali ya ɗan gyara zamansa tare da fara karatu cikin sassayan muryar da yasata lumshe idanunta.

Ethiopia Yah Hafiz ne riƙe da waya murya cike da rauni tausayi ido na tsatstsapo da wahaye ya ɗanyi gyaran murya tare da kiran ɗan nasa da suke waya dashi.
“Imran! Imran!!”.
Ina Imran ya kasa amsawa sai kuka shesh-sheƙan kuka da yakeyi.
“Imran”. Ya sake kiransa a karo na uku.
Murya na rawa yace.
“Na'am Abba”.
Cike da lallashi yace.
“Imran kayi shiru ka dena kukan ya isa haka, zai sa maka ciwon kai, ina Arfah?”.
Cikin kuka Imran ya fara magana cike da rauni.
“Abba ko yanzu nayi ta kiran Uncle Taj baya ɗagawa, nayi mishi text ba amsa yau kusan kwana takwas kenan dani da Arfah duk muna kiranshi ba amsa yanzuma Arfah ya kirashi Amman sai kashe katse kiran fa yayi.”
A sanyaye Yah Hafiz yace
“Ai bazai ɗagaba Imran saboda, Malam yace bai yafe mishi ya sake mu'amala da kowaba a cikin family'nsa kuma muma ɗin yace mana baiyafe mana muyi mu'amala da shi daba”.
Da sauri yace.
“Wallahi mu dai bai isa ya rabamu da Uncle Taj ba, ku da ya haifa kuke ganin zakuyi mishi biyayyar ya raba zumuncin ku da ɗan uwanku mai sonku mai tausayinku, mai son ƴaƴanku tamkar yadda kuke sonmu koma fiye da haka, in kunga zaku iya kuyi masa biyayya, Amman wlh tallahi nida Arfah da ƴan uwanmu mata da sukayi aure muddin mazansu basu hanasuba, zamuyi zumunci da Uncle Taj, domin shine kaɗai Uncle namu da yake tamkar uba, amini, malami, kuma jigon mu, ni dasu duk Allah ya isar Malam bazata yi mana komaiba, Ni matsala ta shi Uncle Taj wanne hali yake ciki? A ina yake? Dasu waye yake rayuwa? Su waye zasu zame mishi madadinku, duk da nasan duk duniya babu masu zame mishi madadin Ummeeyshi da Yah Abanansa”.
Yanayin mgnar ne cikin kuka da hawaye kasheɓar.
Yayinda Arfah ma dake zaune a gefensa yake kuka mai raunataccen sauti.
Ji sukeyi Mexico City tayi musu ɗaci da duhu saboda nesantasu da wanda yayi sanadin zuwansu ƙasar.
A hankali Yah Hafiz ɗin yace.
“Imran kamar tuhumata kakeyi kan na gaza ƙarfafa zumunci na da Afif ne, shin ka mance yadda Afif yake a rai nane,
Imran ko a hospital na wuni jinina ya hau, ya kake son inyi in har kai ɗan da na haifa kana tuhumata na gaza gyara komai.
Ina shiga damuwa in na tuna ba wanda yasan inda Taj yake, naje gidan Addawa kusan sau huɗu Amman itama cemin take bata san inda yakeba, kwana kusan shida kuma in najema bana samunta, gashi Malam yace bai yaffe muyi mgnar Shiba”.

Cikin kuka Arfah ya amshi wayar tare da cewa.
“Big Uncle dole duk mu zargeku akan nesanta Uncle Taj damu da kanku”.
Sai kuma kawai ya fashe da kuka.
Cikin rarrashi Yah Hafiz ɗin yace.
“Kuyi haƙuri kunga kwanaki ne suka rage muku, ku zaku fara jarrabawa, kada kusa damuwar haka a ranku! In sha Allah komai zai dai-dai”.
Haka dai yayi ta kwantar musu da hankalinsu.

Qatar a hankali ta ɗanyi miƙa saboda baccin da ya fara surarta, na yadda ta lumshe idanunta tana jin sautin muryarsa na ratsa kunnuwanta na kusan tsawon 28 mutane.
Sai kuma dukkan kalaman Addawa da Garkuwa suka fara dawo mata.
A hankali ta miƙe zaune, tare da zura sawunta ƙasa kusa dashi.

Buɗe idanunsa dake cike da gajiya, bacci, damuwa, da hawayen ƙuncin zuciya.
Dai-dai lokacin kuma ta zame ta zauna kusa dashi, har kafadarta na ɗan taɓa kafaɗarsa, ɗan gajeren hamma tayi tare da yin mgna a hankali.
“Please Taj kayi bacci, ka bar karatun nan haka ga idanunka fa suna cike da bacci”.
A hankali ya ɗan miƙe tsawunshi tare da sa hannunsa ya jawota jikinsa kan cinyarsa ya ɗaura kanta zuwa kafaɗunta.
Sai kuma yasa hannunsa na dama yana shafa rabin sumar kanta da hular ya zame, a hankali yaci gaba da karatun domin so yake ya kai ƙarshen Suratul Yaseen. Alamun saura masa izufi 15 ya sauƙe Qura'an ɗin a kwanaki uku da ya faro daga Baqara.

Numfashi mai sanyi ya fesar lokacin da ya dire ayar ƙarshen surar.
Iska mai sanyi ya ɗan hura mata cikin kunnenta jin tana mgna ƙasa-ƙasa.
“Kiyi bacci kada kanki yayi ciwo”.
Yayi mgnar yana shaƙan sassayan ƙamshin kullaccar sirri da shu'umar humra dake cikinta, wanda yasashi lumshe idansa.
A hankali ta juya ta ɗan mirgina kanshi tare fuskantarsa, sai kuma ta ƙara lafewa jikinsa murya a tusashe tace.
“In dai bakayi bacci ba. Nima bazanyi baccinba”.
Ta faɗa cikin narkekkiyar murya da tasashi ƙara sunkuyowa a kanta bisa kafaɗarta ya ɗan kife kansa tare da sakin nannauyan numfashi.

Ita kuwa Ishmah cikin sanyi ta gyara kwanciyarta a jikin nasa, tare da sa hannunta ɗaya bisa cinyoyin nasa tayi pillow dashi ɗaya hannun kuma a hankali ta ɗan yi sama dashi kaɗan kan kan ƙeyarsa ta kife tafin hannunta sai kuma ta ɗan zora babbar yatsarsa cikin kwarmin ƙeyarsa inda wani irin tattausan gashi mai sulɓi dake kwance lip-pli a wurin a hankali ta ɗan murza yatsar.
Wani irin lumshe idanunsa yayi tare da fesar da sassayan numfashi.
Mutsu-mutsun da sukeyi ne, yasa tattausar jallabiyarsa fara tattarawa kasancewarta mai tsulɓi
Gyara zamansa yayi ya ɗaura ƙafarsa ɗaya bisa ɗaya, hakan yasa tayi tudu sosai  tudun da ya bashi damar gyara kifa ƙirjinsa da kansa bisa kafaɗarta ya cusa kansa tsakanin wuyanta da

kanta, tare da manna hancinsa dai-dai ƙasan kunnenta da yake zuba ƙamshi kulaccar sirri cikin sanyin murya da kamar raɗa-raɗa ya fara karanto suratul Mulk dan ɗabbagar sunan da ɗibi'arsa na karantarta surar duk daren duniya, domin itama surace maiyin ceto ranar gobe kiyama.

A hankali take shaƙan ƙamshi turarensa tare da da gyara hannunta na hagu kan cinyarsa ta tallabe fuskantar ɗaya hannun kuma tana murza ƙeyarsa a hankali wanda tuni hakan yana sako mishi wani irin amintaccen sanyin da lunshin ido.
A hankali ta lumshe idanunta, yayinda shima ya lunshe idanunsa tare daci gaba da karatun yana mai jin ɗumin jikinta da ƙamshimta suna fizgo mayataccen baccin dake damunsa.
Cikin 6 minutes bacci yayi awon gaba dasu, wanda zuwa lokacin tuni ƙarfe biyu ta gota.

Ƙarfe biyar dai-dai ya fara buɗe ifanunsa a hankali, tare dayin addu'ar tashi daga bacci, da sauri ya sake rufe idanunta saboda ganin yadda ta jawo jallabiyarsa ta tattareta ta yi filon gefen fuskantar dashi, a hankali yake sauƙe numfashi dake nunin da ya samu sassaucin azabar rashin baccin, dai-dai lokacin kuma ta buɗe idanunta tare da yunƙurawa alamun zata taso, still tana riƙe da jallabiyar tasa wanda hakan yasa gaba ɗaya cinyoyinsa bayyana a fili zura idanunta tayi bisa tattausar farar tatarsa da gargasa ke kwance lip-pli a kanta tamkar anayi masu bayin ruwa, so take ta lunshe idanunta Amman ta gaza, saboda kyaun surar cinyarsa.

Shi kuwa Taj cikin sanyi yace.
“Yah Salam Babey mun makara fa”.
Ya ƙare maganar da sa hannunsa ya tattaro gashin ta ya meda mata shi gefen wuyanta, wanda hakan ya bawa fatar wuyanta dama bayya, kusan a tare suka Lumshe idansu lokacin dayayi kissing ɗin wuyanta.
Jan numfashi tayi tare da miƙewa zaune, ta haɗe sawunta tare da kife kanta bisa guiwowinta.

Shi kuwa Taj a hankali ya miƙe tare da nufar Bathroom, wanka yayi kamar yadda ya saba kana yayi al'walan, yana fita itama ta shiga.

Yadda yayin haka tayi, tana fitowa ya miƙe ya nufi Parlour tare da cewa.
“In kin gama kizo muyi jam'i muyi salla ko!”.
To tace tare da nufar drower.

Wani kayan ta jawo riga da wondo ne, sai dai rigar  chort sleeve shirt ce, fara ƙal mai ɗan wuya, sai wondon kuma brawn collar ne mai ratsin fari sai doguwar abayar kalan wondon mai igiyoyi biyu.
Sai kuma ɗan gyale fari.

A hankali ta kimtsa kanta cikin kayan.
Masha Allah, tace lokacin da ta tsaya gaban mirror tana rolling gyalen a kanta, domin sosai kayan suka zauna ɗas a jikinta kai kace, dan ƙirar jikinta aka haliccesu, igiyoyin rigar taja ta ɗan ɗaure daga tsakiya wanda hakan ya bawa ƙirjinta damar bayyana, kana tayi rolling kanta ta

fidda fuskantar  fasalin 0 turaren ta fesa.

A hankali ta fito Parlour, kan sallayan dake can shimfiɗe a gefen sukayi salla bayan sun idar ne ta ɗan juyo ta kalleshi.
“Barka da safiya”.
Ta faɗi tare da kallon fuskarsa, cikin jin sassauci da raraɗin damuwarsa yace.
“Babey kin tashi lfy”.
Sai kuma ya ɗanyi ɗan guntun Murmushin gefen baki yace.
“Wuyanki na ciwo ko?”.
Kai ta jujjuya mishi alamar a'a.
A hankali yace.
“Kin samu lada, kin sani nayi bacci har na tsawon awa uku, kusan mako biyu kenan baccina baya wuce 30 minutes nake farkawa shima sai in ina karatune nake samun ya ɗan fizgeni, shiyasa nake kwana a zaune, Amman yau nayi mai yawa Allah yayi Miki albarka”.
A hankali tace.
“Amin ya Allah”. Sai kuma ta ɗan kalleshi jin yana cewa.
“Miyi du'a Azkar, sai muje Restaurant muyi breakfast”.
Kwaɓe fuska tayi cikin sanyi tace.
“Taj mu koma gida”.
A hankali yace.
“Kin gaji da zaman nan ne!”.
Cikin sanyi tace.
“A'a kaga gobe su Aunty Nana zasu, koma ina son ɗan zama tare dasu”.
Yana ɗan gyara zamansa yace.
“to Saida yamma ko!”.
Da sauri tace.
“No ai in mun kai 12:00 AM
sai ka ƙara biyan kuɗin yau, ni mu tafi yanzu kaji ko dan allah.”
A hankali ya gyaɗa mata kai tare da cewa.
“Hmmm ai dama na kuɗin two weeks na biya. Amman zamu tafi tunda hakan kikeso”.
Daga nan sukayi addu'o'in su.

Ƙarfe goma dai-dai ta samesu a cikin gidan.
Bayan ya gaida dasu Aunty Amina da duk suke Dinning area.
Ya wuce ɗakin Addawa.

Ita kuwa Addawa da kanta ta haɗa musu breakfasts ta miƙawa Ishmah tray.

A bisa kujera ta sameshi zaune, yayinda Laylah ke zaune can gefen gado ta takure jinkinta daketa karkarwa tamkar wacce taga dodo.
Shi kuwa Taj ido kawai ya zuba mata cike da ƙuna da ƙuncin zuciya yana ɗaya daga cikin abinda yasa yakejin kamar zai raba musu gida da Addawa ta riƙe Laylah saboda yadda Laylah ta kasa sakewa dashi a fili yake ganin tsananin tsoronsa a kwayar idanunta wanda hakan ke

sashi jin ya tsani kansa da kansa.

Ajiye Tray Ishmah tayi a gabansa tare dasa hannunta ta jawo Laylah da jikinta ke karkarwa tamkar mazari, a hankali tace.
“Ya dai Laylah me ya sameki? Ya kike firgice haka?”.
Sai kuma ta juyo ta kalli Taj ɗin daya taune gefen lip inshi na ƙasa kana ya zura idanunsa wuri ɗaya.
Cikin mamaki tace.
“Taj wai me ke damun Laylah ne, me take tsoro haka?”.
Cikin sanyi ya miƙe tsaye tare da zura hannunshi cikin aljihunsa suit inshi a hankali ya juya ya nufi hanyar fita tare da cewa.
“Ni take tsoro”.
Ya ƙare maganar tare da ficewa, side ɗinsa ya wuce kai tsaye.

Yana fita Addawa kuma na shiga dai-dai lokacin da take cewa Laylah.
“Laylah wai Uncle Taj ɗinki kike tsoro? Me yayi Miki?”.
Cikin sanyi Addawa ta zauna gefensu tare da yin ƙasa da murya tace.
“Eh shi take tsoro Ishmah!”.
Da sauri tace.
“Saboda me?”.
Tana mai ɗan taune lips inta duka biyu tace.
“Tun sanda maganar cewa Taj yayi mata fyaɗe ta fit.”
Da sauri Addawa tayi shiru ganin Ishmah ta sa hannunta duka biyu ta toshe kunnuwanta kana ta miƙe tsaye tana mai girgiza kai tare da jujjuya idanunta da sukayi jazir gaba ɗaya jikinta rawa ya farayi tamkar mazari.
Ita kuwa Addawa sai yanzu ma ta tuna da kashedin Taj da yayi mata na kada ta gayawa Ishmah komai shi da kansa zaiyi mata bayanin.

Sai kuma tabi Ishmah da idanu ganin ta fita.

Sauri-sauri gudu-gudu ta nufi Corridor ɗin, steps ɗin hawa saman ta fara takawa da sassarfa har Lau hannunta na toshe da kunnenta kamar tsoron buɗe kunnuwanta ma takeyi.

Gaba ɗaya idanunta basa iya gani, shiyasa ta gaza hango shi inda yake Dinnin area yake zauna bisa kujerar tare da kife kansa a kan Table ɗin.

Cikin rikitaciyar murya da alamun tsananin girgiza gami da son hafimtar abinda taji ta fara kiran sunansa murya a hargitse.
“Tajj! Tajj!! Tajjjj! Ina kake”..
Ta ƙare maganar muryarta na rawa hawaye na zubo mata.
Cikin sanyi ya miƙe tsauye yayinda zuciyarsa ke duka tara-tara farga da kiɗimar kaddai Addawa ta gaya mata cewa yayiwa Laylah fyaɗe harma tana da ciki ne suka diro mishi in one second.
A sabule ya taho gareta, murya a daskare yace.

“Gani”.
Da sauri ta juyo ta inda taji muryarsa hannunta tasa ta kamo hannunsa kana ta jawoshi zuwa tsakiyar Parlour sake hannunsa da tayi da kuma mutuwar da jikinsa yayi ne ya sashi zamewa ya zauna bisa kujerar 3 sitter dake bayansa.
Ita kuwa zubewa tayi bisa guiwowinta cike da tsoro murya na rawa tace.
“Taj me nakeji? Me gaskiyar abinda Addawa ta faɗa?”.
Cikin wani irin matsanancin fargaba da tashin hankali gami da tsoron, kada itama Ishmah tayi mishi irin hukuncin da Yah Abana da Ummeeynshi sukayi masa, yana taraddadin kada tayi mishi yakicewar da zaisa ta nesantasu da juna, itace kaɗai sauran yaƙininsa a duniya, ya zata ɗauki waɗanan kalaman in ta gujeshi ina zai saka ransa?.
Jin ta daura hannunta kan guiwowinsa tana jijjigawa da ƙarfi tare da fashewa da kuka tana faɗin.
“Tajj ka gaya meke faruwa? Please kayiwa Allah da Manzonsa kada ka ɓoye min komai meyasamu Laylah?”.
Kanshi ya ɗago tare da zuba mata ido cikin Tsananin damuwa da fargaba yace.
“Ma'eesha nayiwa Laylah fyaɗ....
Da sauri ta tsananta jijjiga guiwowinshi ba tare da ta bari ya ƙarasa faɗar abinda yake son faɗamatan ba domin heart and brain ɗinta bazasu iya ɗaukar nauyi da munin kalaman ba ji take zuciyar tamkar zata fashe cikin tsananin kiɗima gigita gami da tashin hankali da tsananin tsanan furucinsa na karshe da ta katse shi ta hanashi ƙarasa tayi wani irin miƙa tare da jujjuya kanta tana yarfa hannunta na dama na hagu kuma ta ɗaurashi kan ƙirjinta dake barazanar fashe cikin rawar murya tace.
“Wallahi tallahi bazan ci gaba da zam....

*Littafin INDA RAI na kiɗine ki biya ki karanta cikin aminci da salama 1k ne kacal 0661110170 GTBank Aisha Aliyu Garkuwa, sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276 in kuma Niger kike 1000fc ne jaka ɗaya kacal kenan zaki biya. In kuma baki biyaba kika karanta min littafina wannan kuma kede Allah*

By
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 📝💉🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*INDA RAI*
*BOOK 2 PAGE 8*

Irin zazzafan ajiyan zuciya mai fizge numfashinta.
Da sauri ta miƙe tsaye saboda jin numfashinta na shirin barin gangar jikinta.
Ita kuwa Laylah da sauri ta nufi Parlour da gudu tana kiran Addawa da ƙarfi.
Wanda har Taj dake sauƙowa daga sama ya jiyota cikin mamakin yaxu gaba da sauƙowa saboda jin yadda Laylah ke aunawa Addawa kiran mafarauta, sai kuma ya fara sassarfa tare da sauƙa cikin kaɗuwa sabido jin Laylah na cewa Addawa.
"Aunty Ishmah ne tana ta kuka, Addawa ta kasa zama numfashinta fita da ƙarfi".

Kusan a tare suka shiga ɗakin.
Cikin tashin hankali ganin yadda numfashi Ishmah keyi sama da ƙasa ne, yasashi saurin isa hareta dai-dai lokacin da jiri ya fara ɗibanta.
Da sauri ya tallabota ta afka cikinsa, da ƙarfi ya ruggumeta tsam a jikinsa.
Addawa kuwa salati ta saka cikin kaɗuwa take kiranta.
"Yah Salam Ishmah meke damunki?  Afif mu tafi asibiti da sauri".
Cikin ji muryar Addawa can sama-sama, da ƙarfi ta rumtse idanunta dake kwaranyar da hawaye tamkar an buɗe igiyar ruwa, murya na rawan kuka tace.
"No Taj bana so, kada ka kaini hospital, ni lafiyata ƙalau".
Ta ƙare maganar cikin yayyankewar numfashi.
Da sauri ya tallabo kanta da tafukan hannunsa duka biyu, idonsa ya zuba cikin nata cikin muryar dake nuna damuwarta itace damuwarsa yace.
"Ma'eeshah numfashinki baya fita, ki bari muje asibitin, bana son rasaki, bana kuma son Ummeeyna ta ratsani ba tare da Yah Abana da Ummeyn sun yafe min ba".
Ya ƙare maganar da sunkuceta tsam kana ya nufi hanyar fita da ita, itama Addawa bayansu tabi da hanzari tare da juyowa ta kalli Zulaihat lokacin da suka fito Parlour.
"Zulaihat ku zauna a gida bari muje asibiti, ki kula da Laylah".

Cikin sanyi Zulaihat tace.
"Toh Addawa sai kun dawo".

Dai-dai lokacin da suka shiga Corridor ɗin da zai fiddasu wajen.
Da sauri Ishmah tasa hannunta na dama bisa ƙirjin Taj ɗin tana ɗan bubbuga cikin alamun a ɗimauce take mgna da fizgo murya.
"Yah Sheykh lfyata ƙalau please dan Allah dan Annabi kada ka kaini asibiti bana so".
Wani irin kallo ya zubawa fuskantar domin ya sani a iya tsawon zamansu in dai ta kirashi da Yah Sheykh to tabbas mgna ce ta gsky takeyi mishi, ba wasa ko ƙarya ciki kuma muddin ta haɗashi da Allah to yasan babban abune da take son a bari ko ayi shi, dan yana cikin abinda yasa bai taɓa cewa yana sonta ba, kafin aurensu domin da ake ta cewa son juna suke, yake cewa to ko dai gsky ne, ranar tayi ta roƙonshi da Allah da Manzonsa kada ya kawo makamanciyar mgnar nan a abotarsu ta rantse cewa, ba wannan mgnar shiyasa bai samu damar ida ƙudurinsaba saida tura ta kai bango.

Da sauri ya juya ya nufin kan steps ɗin da zai sadashi da part ɗinsa, saboda jin yadda taketa ɗan bubbuga kafaɗarsa tare da magiya gami da haɗashi da Allah.

Da sauri Addawa ta mara musu baya.

Suna shiga Parlour ya kwantar da ita bisa 3 sitter, sai kuma ya dire guiwowinsa ƙasa tare da ɗan ɗaura hannunshi kan goshinta kana ya ɗan sunkuyo kanta, tare da mannan lips inshi kan hancinta.
Hmmmmmmmmm taja wani irin na kasashshen numfashi saboda jin yadda yake bata taimakon gaggawa dan hana numfashinta ɗaukewa.
Zazzafan numfashi ya fesa mata kana ya zuƙo nata sassayan numfashi dake gab da komawa cikinta ya fizogoshi da ƙarfi.
Wani irin miƙa tayi tare da sauƙe ƙaƙƙarfan ajiyan zuciya da ya tabbatar da daidaituwar numfashinta.

Kusan a tare Addawa da Taj ɗin duka dire ajiyar zuciya dake nuna samun nitsuwarsu.
A hankali yake ci gaba da shafa goshinta tare da ɗan sa yatsarsa manuniya yana ɗan kwantar da gashin girarta ɗaya da ya hautsine.

Gefen kanta Addawa ta zauna bisa hannun kujerar murya cike da kaɗuwa da kulawa tace.
“Kina da Asma ne?”.
A hankali ta jujjya mata kai alamar a'a, shi kuwa Taj yatsarsa yasa kefen kuncinta ya goge mata hawayenta dake kwaranya, cikin sanyi murya yace.
“Ma'eesha meke damunki? Meya saki kuka? Ki gaya min koma menene zanyi maganin abin bazai sake sa min ke kuka ba”.
Ido a lumshe tace.
“Taj Laylah ke ƙara tabbatar min wai da gaske anyi mata fyaɗa wai ka maida ita tamkar matar aurenka, tun sanda kuka dawo Nigeria, Laylah tace min  a ɗakinta kake kwana, saboda duk sanda kake Ethiopia ne ake kwana mata a ɗaki, Laylah tace min bindiga kake nuna mata kasata dole ta tsiraita, kuma kaima ka tsi...”
Ina ta kasa ƙarasa kalmar dan tayiwa harcenta nauyi.

Addawa kam ido ta rumtse da ƙarfi, don ta fahimci kenan Laylah tayi mata cikekken bayanin kamar yadda tayi mata cikekken bayanin yadda  Taj ya maida ta, tamkar matarsa.

Cikin zubda hawayen ta miƙe ta fice daga Parlour'n tana mgnar zuci.
“Na sani Tajuddeen Namijine daya amsa suna na miji, na kuwa san cewa lafiyeyyene da yake da buƙatar mace a kusa dashi, wacce yake so take sonshi wacce zata iya ɗaukar nauyin buƙatar sa, a matsayin halittarsa ta cikakken namiji, duk da na ɗan fahimci ƙarfin tattalirsa da buƙatarsa gadon kakansa ne, gashi an aura mishi wacce baya so bata sonshi, ban yarda ko amincewa hakan zaisa Tajuddeen yayi fatali da iliminsa nutsuwarsa, kamalarsa har ya lalata ƴar da ya ɗauko amana daga hukumar kula da marayun Palastine ba, Tajuddeen an cuci yarinyar nan, an tozarta rayuwarta an liƙa maka baƙin fenti.

Amman na sani in sha Allah gskya zatayi halinta domin da wuya haƙƙinta da kai da zuciyata taƙi yarda zaka aikata ya bari waɗanda sukayi wannan makircin su samu zaman lfy.
Ko dan haƙƙin tarwatsa tsakaninka da iyayenka da matarka  duk da muna kyautata zaton zatayi haƙuri da kuskurenka inma kai ka aikata".
Koda ta iso Parlour bata iya amsa mgnar da Zulaihat da Laylah sukeyi Mataba, saboda ɓacin rai da mgnar zuci da take yi.

A can Parlour Taj kuwa, kife kansa yayi a gefen kanta, so yake yayi mgna Amman ina ya kasa sai wani irin rawa da lips inshi keyi kamar wanda aka saka cikin dusar ƙanƙara.

Ita kuwa Ishmah idanun ta dake zubda hawayen ta zuba mishi tare da ci gaba da yin sassayan kuka tana faɗin.
"Taj kayi mgna mana".
Cikin fizgo mgnar zuci yace.
"Kiyi haƙuri Babey wlh ni n..."
Da sauri tasa yatsunta ta toshe kunnuwanta tare da fashewa da kuka tana faɗin.
"No! No!! Nooooo!!! Taj kada kace min da gaskene".
Kife kanshi yayi ya kasa mgna sai karkarwa da jikinsa keyi.

Ita kuwa Ishmah kukan taci gaba dayi.

Ethiopia
Adaya ce kwance bisa gadon ta, sai juyi takeyi, tare da jan gajerun tsaki a jere a jere, hannunta ta manna bisa wuyanta.
Da sauri ta cire hannun saboda yadda taji jikinta, yayi zafi.
Juyawa tayi ta gefen hagunta tare da lumshe idanunta tana mai jin ɗan karen gajiya da zazzabin da yakeda nasaba da rawar data wuni yi kai kace injice itan.

Da kyar dai ta samu wuraren ƙarfe ɗaya. bacci yayi awon gaba da ita.

Doha Qatar.
A hankali take sauƙe ajiyan zuciya a jere a jere bisa alamu tana cikin kukan ne, bacci ya sureta.

Shi kuwa Taj ɗin a hankali yake sauƙe numfashi tare da taune lips inshi na ƙasa, so yake yayi bacci ko ya suma ko Allah zaisa yaji sauƙin zafi da ƙuna gami da raɗaɗin da zuciyarsa keyi masa, to ya zaiyi da rayuwar sa, ina zai shiga ya samu sassauci, kullum tabbatar a yiwa Laylah gyaɗe ƙara bayyana sukeyi ga batun cikin da akace tana ɗauke dashi, shine babbar matsalar rayuwar sa, ganin cewa ya cinye fiye da rabin daren a nazarin da bai samu mafita bane, yasa ya miƙe yaje yayi al'wala kana ya dawo Parlour ya rinƙa nafilfili tare da tilawar Qura'ani mai girma gami da tasbihai da neman sassaucin zafi da ƙunar ƙadaddarorinsa.

Washe gari ranar Friday, kasan cewar yau ba aiki dan a tasu doka da ƙa'idar ƙasar Jumma'a da

asabarne ranakun hutun mako, ranar Sunday to Thursday ne ranakun aikinsu.

Tsaye take a tsakiyar Parlour, tare da lumshe kumburarrun idanunta, ringing ɗin da wayarsa keyi ne yasata buɗe idanunta.
“Dr Abbas”. Ta furta saman lips inta lokacin da taga shine mai kiran.
“Na rasa meyasa Taj baya son riƙe wayar nan yanzu wayarda yasha cemin ta family insa ne da shaƙiƙansa makusanta shiyasa bai rabuwa da ita, yanzu kuma sam bai riƙeta ma, sai dai ya riƙe waccar da yake cewa layin ciki na al'ummar duniya baki ɗaya ne.”
Sai kuma tasa hannunta ta ɗauki wayar ganin kira ya kuma shigowa.

A dai-dai lokacin kuma Taj ɗin ne zaune, a balcony dake bayan dinning area ɗinsa, zaune yake bisa kujerar sai System nashi dake gabanshi bisa ɗan madaidacin table ɗin dake gabansa.
Yayinda ya kafa wayarsa yana video, a shafinsa  na TikTok inda yake karanta suratul Khaff kamar ko wacce ranar Friday domin tunasarwace ga al'ummar musulmi, kasan cewar yana bin ayoyin daki daki ne, so daga aya ta 59, 60, 61, 62. Yayi kana yayi saki video bayan ya ɗanyi rubutu a sama kaɗan, Don't forget to read suratul Khaff on Friday. Jumma'at Mabrooq to all Muslims Ummah.
A hankali ya gyara zamansa tare da lumshe idanunsa kana ya buɗesu yana kallon fuskarsa a cikin Camerar wayar tasa da yatsarsa ta ɗan taɓa, ya shiga kamar zai yi wani video ɗin.

Cikin sanyi ya kuma lumshe idanunsa da suka sauya launi tun ranar da Yah Abana ya koreshi basu sake dawowa asalin launinsu ba.
Wani irin rauni, bege, so, ƙauna, gami da  kewar iyayensa da ƴan uwansa da ahlinsa baki ɗaya yakejin.
Ji yake tamkar yayi fiffige ya ganshi a tsakiyar Parlour Yah Abana wanda ya sani yanzu haka suna can suna cike a Parlour, sun sashi a tsakiya, ji yake tamkar zuciyarsa zata fashe dan so da begen ganin Ummeeynshi da Yah Abana, so yake ya ganshi a tsakiyar yayunsa da ƙannensa, ji yake yi yayi rashin da bazai manceba, da ya kamata yaye kansa da kare kansa da haka bata faruba da yau shi ya limancin Yah Abana kamar yadda ya saba tsawon shekaru in dai yana Ethiopia.

Ishmah kuwa a hankali ta ɗan haura saman dinning area ɗin, ido ta zuba wa ƙofar da zai sadata da balcony ganinta kamar a buɗe da ɗan sauri ta isa gaban ƙofar, tana ɗan jan handily ɗin kuma taga ashe a buɗe take.

Shi kuwa Taj haka nan yakejin.
Wasu irin zafafan hawaye masu masifar ɗumi suna tsatstsapo mishi cikin jijiyoyin idanunsa, haka nan yaji wasu baitukan na dira kan harshensa cikin harcen Amharic murya can cike da sanyi gami da rauni ya fara baitukan.
“Da Babana nake, nakayin tutiyyyyah”.
Yaja ƙarshen baitin cike da raunin da yasa hawayensa bayyana cikin ƙwayar idanunsa da hakan yasa idanun nasa yin wani irin sheƙi da ƙellin hawayen suka bada wani special collar mai tafiya da hankalin.

Dai-dai lokacin Ishmah ta ƙarasa  fito hango shi zaune, ya dasa waya a gaba, kana ga wasu amintattun baitukan da yake yi wanda suka sa zuciyarta raunata har ta kai ga jikinta yayi sanyi, a hankali ta nufi inda yake zaune yana fuskantar ta, sai dai sam bai gantaba saboda zuciyarsa data raunata ga ruwan hawaye daya cika mishi ido.

Sassayan numfashi ta fesar tare da lumshe idanunta saboda taushin da zaƙin sautin muryarsa da ya wadaci jinta, a hankali ta zauna bisa kujerar dake fuskantar tasa dai-dai lokacin da ya sake maimaita baitin da yayi a forkon.
"Da Babana nake, nakayin tutiyyyah."
Sai kuma ya lunshe idanunsa wanda hakan yasa hawayensa kwaranyowa kana ya motsa lips inshi a hankali yaci gaba da raira baitukan.
"Zamana ɗansa na halal shine kwalliyata, ta rayuwata ta cikin duniya."
Sai kuma ya ɗan taune lip inshi na ƙasa da ƙarfi murya na rawa yaci gaba da faɗin.
"Yah Abana shine antal sababul zuwata duniyyyah".
Zuwa yanzu rawar da muryasa keyi ya tsananta bazai iya ci gaba da rairai baitukan ba,
Sai sassayan shesh-sheƙan kuka daya kufce mishi.

Sai kuma yayi saurin ɗago idanusa  ya kalli Ishmah da itama kukan ne ya kufce mata saboda tsananin tausayinsa.
Murmushin ƙarfin hali da jarunta yayi tare da miƙa hannunsa zai ɗauki wayar, dai-dai lokacin kuma itama Ishmah ta miƙa hannun ɗaukar wayar, hakan yasa wayar ta faɗi da sauri ta sunkuyo ta ɗauki wayar garin ɗauka kuma yatsarta yayi sending video ya tafi duniyar TikTok.

A kuma dai-dai lokacin kiran Dr Abbas ya sake shigowa, piking call ɗin tayi kafin ta miƙa masa, murya na rawa tace.
"Dr Abbas ne yaketa kira tun ɗazu".
A hankali ya ɗan ƙara matsowa gaba, ga zatonta wayar zai amsa, sai kuma taga ya kai hannunsa kan kuncinta tare da fara sharce mata hawayenta cikin sanyi da taushin lafazi yace.
"Kiyi haƙuri ki yafe min, inata zama sanadin saki zubda hawaye.
Na kasa cika alkawarin da nayiwa Abba na hanaki zubda hawaye, dole in nemi yafiyarsa bisa kasa cika mushi alƙawarin saki farin ciki".
Ya ƙare maganar tare da tallabe fuskantar da tafukan hannunsa.
Cikin sanyi ta ɗaura nata tafukan hannunta kan nashi daya tallabe fuskantar murya cike da tautasaya tace.
"Baka gazaba Yah Sheykh dan ba abinda ka rage ni dashi, nice na gaza zame maka mai share ma hawaye.
 Nice na ƙasa saka farin ciki, na gaza mantar da kai damuwar zuciyarka na kasa zame makar mar'atussaliha".
Ta ƙare maganar tana lumshe idanunta saboda jin yadda yake murza yatsunsa kan kumatunta.
Shi kuwa Taj wani irin lumshe ido yayi yana mai jin kalmar mar'atussaliha data kira yana mishi yayyafin sanyi a zuciyarsa.
Kiran Dr Abbas daya kuma shigane yasa ta ɗan janye fuskantar tare da cewa.

“Ayyah ka amsa tun ɗazu yake kiranka”.
Kai ya gyaɗa mata kana, ya amsa kiran tare da ƙara wayar a kunne yace.
“Wa alaikassalam, kun iso ne?”.
Cikin kufula Dr Abbas yace.
“Ban saniba”.
Ɗan guntun Murmushin yayi tare da cewa.
“Dr Amdaz da Bilal suna Airport ɗin ai tun da aka sauƙa sallan jumma'a suna can”.
Cikin tsuke fuska Dr Abbas yace.
“Na fika sani ai, tunda sun ɗaukoni har gani a Parlour Addawa harma naci abinci.
Kai da kai na jira sai in bushe a can ko”.
Ɗan gyara zamansa yayi tare da cewa.
“Barka da isa Ify”.

Da sauri Dr Abbas yace.
“Kaga kada ka kashe min waya, ka sauƙo ina jiranka, ga Dr Farida tana son isa masauƙinta”.
Cikin mamaki yace.
“Ha'a wai da gaske tahowa tayi?”.

“To ka sauƙo ai zaka ga zahiri”.
Cewar Dr Abbas.
Yana ɗan tsuke fuska yace.
“No kada ta jirani, Dr Amdaz zai bata key Bilal ya kaita, kai kuma da Dr Amdaz ku jirani”.
Yana ida faɗin hakan ya katse kiran.

Cikin sanyi Dr Farida ta miƙe tsaye bayan da Dr Abbas ya gaya mata yadda sukayi.
Da sauri Addawa tace.
“Bari a kawo miki  abinci ki tafi dashi”.
Ɗan Murmushin kirsa tayi tare da cewa.
“A'a barshi kawai in naji yunwa zanzo nan ɗin muyi dinner in kuma banji yunwaba sai da safe zanzo muyi breakfast”.
Cikin murmushi Addawa tace.
“To a huta gajiya”.
Daga nan Bilal ya ɗauketa suka tafi.

Tsakanin gidanta dana Taj ɗin a ƙalla akwai gidaje 8, kuma two bedrooms ne sai big Parlour and dinning area sai kitchen da ɗan ƙaramin store, kusan haka gidajen Doctors ɗin suke, sai dai akwai masu 3 bedrooms.

Suna shigowa Parlour'n Dr Abbas yayi murmushi tare da kallon Ishmah dake cikin Dubai Abaya onion color kai ya jinjina cikin jinjina kai ya ɗan rungume Taj tare da cewa.
“Masha Allah, ka iya zaɓi Allah ya baku zaman Ify ya sanya alkhairi”.
Yana ɗan buge ƙeyar Dr Abbas ɗin yace.
“Amin ya Allah”.

Sai kuma ya sakeshi tare da rungume Dr Amdaz.

Murmushin Addawa tayi jin Dr Abbas nacewa Ishmah.
“Ƴar sa'a ko ince sarkin sa'a, kin samu mijin da matan duniya ke ribibi in one time kinyi dace da nagartaccen miji ina tayaki murna, duk da kinyiwa abokan aikin mu shigar sauri”.
Ɗan murmushi mai cike da kamala tayi kana tace.
“Haka shima yayiwa wasu bugun kwab ɗaya”.
Cikin dariya Dr Amdaz yace.
“Ai shima dama tun a school bugu ɗaya yakeyiwa komai ya kwashi abinda wasu suka shekara suna bugawa basu samu ba, baya cewa yana son abu ya rasa”.
Suna zama Taj ɗin ya ɗan kalli Laylah da ta miƙe da sauri tabi bayan Ishmah data nufi ɗakinta.

Addawa da Zulaihat kuwa kitchen suka nufa.

Washe gari ranar asabar.

Mexico.
Arfah ne kwance bisa gadon yana riƙe da waya, video da Taj yayi na baitukan akan mahaifinsa ya tura Family group insu, yayi playing video yafi sau shida,
Hawaye ne keta zuba daga idanunsa.
Imran dake zaune gefensa ne ya ɗan kallesa cikin disashewar murya yace.
“Yauma ina ta kiran Uncle Taj baya piking call ɗin”.
Murya can ƙasa Arfah yace.
“Imran kalli yadda Uncle Taj yake kuka, wai wanne irin zuciya ne a ƙirjin Malam, wlh ni na tura masa video nan sai dai yayi min duk abinda yaga dama, wai so suke baƙin ciki ya kashe Uncle Taj ne, meyasa duk basu da imani”.
Da sauri Imran yace.
“Me malam ɗin yace? Yaga video ne?”.
Yana tashi zaune yace.
“Eh ya gani, baice min komai ba, a group ɗin mafa sai imojis na kuka kawai akayi ta turawa babu wanda yace ko ƙala”.
Cikin sanyi Imran yace
“Arfah ya za'ayi suyi mgn mahaifinsufa cewa yayi duk wanda yayi alaƙa da Uncle Taj ko ya kira sunansa bai yafe masa ba”.
Ya ƙare maganar tare da kiran Taj ɗin.

Qatar.
Zaune yake bisa Sallaya duk hankalinsa na kan System nashi bisa alamu abu mai mahimmanci yakeyi.
Ita kuwa Ishmah kwance take bisa 2 sitter dake bayansa.
A hankali ta ɗan buɗe idanunta ta zubasu kan System ɗin nashi, sai kuma ta kalli wayarsa.
“Imran ne fa kayi piking call ɗin kullum sai ya kirafa”.
ta faɗa cikin muryar bacci, kai ya jujjuya mata alamun a'a, sai kuma yayi piking call ɗin tare da

miƙa mata kana yayi magana a hankali.
“Kice masa na tura musu kuɗi, in akwai abinda suke so ba sai ya kirani ba”.
Jin Muryar Imran na faɗin.
“Hello Uncle Taj, kayi haƙuri bazamu iya nesanta da kaiba”.
Jin haka ne yasa Arfah saurin amsar wayar tare da cewa.
“Uncle Taj kasan saura mana wata biyu fa muyi huhu kuma bazamo Ethiopia ba, zaka zo ko”.
Kallon juna sukayi da sauri jin muryar Ishmah tana mgna cike da kulawa da alamun ta sansu.
“So sorry Imran Arfah Uncle Taj, ya fita ya bar wayar a gida, Amman in ya dawo zai kiraku”.
Da sauri Imran yace.
“Afwan wacece ke?”.
Wani sassayan numfashi Taj ɗin ya fesar lokacin da yaji tace.
“Aysha Abdullahi Matawalle, Aunty Ishmah.
*Mrs Uncle Taj”.*
Sake kallon juna sukayi da sauri sai kuma Imran yace.
“Ayyah Aunty Ishmah da gaske, ke matar Uncle Taj ne? yaushe kukayi aure? Yanzu a ina kuke?”.
Cikin son cire musu shakku tace.
“Wallahi kuwa ni matarsace ta Sunnan, last two weeks ago aka ɗaura mana aure A Adamawa Nigeria.
Yanzu kuma muna Doha Qatar.

Cikin sauri da jin gamsuwa da kalaman Ishmah Imran yace.
“Toh My Aunty na yarda, Amman Uncle Taj na kusa ko?”.
A hankali tace.
“Eh”.
Ta faɗi hakanne saboda alama da Taj ɗin yayi mata na cewa ta faɗi eh ɗin.
Da sauri Arfah yace.
“My Aunty kice yayi haƙuri ya amsa kiran mu, mu yana da mahimmanci a rayuwarmu, kuma ba ruwanmu da shara ɗin Malam dan mu ba yayansa bane jikokine, yayi ikonsa iya yayansa bandamu jikoki”.
Ɗan sunkuyar da kai Ishmah tayi kaɗan dan taji me yake cewa.
“Kice musu suyi haƙuri komai nada lokaci kada su rinƙa kirana, ki basu number'nki su rinƙa kiranki ke ko Addawa suna jin labarin mu, in kuma akwai abinda suke so, su rinƙa gaya Miki sai ki gaya min, kice kada su damu, ina cikin Ify dani dake matata da Laylah da Addawa da Zulaihat ɗin ta”.
Kusan a tare Imran da Arfah suka rungume juna dan sunji duk abinda yake faɗa.
Alhamdulillah yanzu sun ƙara gamsuwa Ishmah matarsa ce, gashi sunji yana Qatar kuma tare da Addawa da Laylah ɗin harda Zulaihat.
Sun ji sauƙin raunin gane yana da makusanta.
Cikin jin daɗi suka haɗa baki wurin cewa.
“Yess Uncle Taj, muji muryarka, kuma zamuyi yadda kace, zamuke kiran our Aunty, in mun samu hutuna zamuzo Qatar”.
Murmushin Ishmah tayi ganin shina Taj ya ɗan saki fuska sun mance cewa zasu iya jinsa tunda

ta matso da wayar.
Cikin sakin fuska tace.
“Uncle yace karku zo”.
Da sauri Arfah yace.
“Our Aunty ai wurinki da Addawa zamuzo ba wurinsa ba”.
Sai kuma Imran yayi sauri cewa.
“Yauwa Our Aunty dan Allah ki bamu number, ki kulan mana da Uncle Taj”.
Tana Murmushin ta basu number sabon sim ɗin daya mata na Qatar ɗin, daga nan sukayi sallama.

Numfashi ya ɗan fesar tare da ci gaba da abinda yake yi.
Cikin sanyi tace.
“Naga kamar takardar barin aiki kake rubutawa Ethiopia Airlines?”.
Yana ɗan lumshe idanunsa yace.
“Eh”.
Da sauri tace.
“To me yasa Taj pilot fa burinka ne! Ya za'ayi ka bar aikin!”.
ɗan juyowa yayi kalleta kana a hankali yace.
“Ba barinsa zanyi dukaba, Ethiopia Airlines ɗin zan bari, zan dawo Qatar Airways, dan har sun bani gurbin aiki”.
Sassayan numfashi ya fesar kana yace.
“Hakan yayi Miki?”.
Tana tashi zaune tace.
“Eh, fatan Allah ya bada Sa'a”.
Ta ƙare maganar tare da zama a gabansa, shi kuwa Amin yace yana kallonta cikin kulawa dan yaga zaman da tayi alamun so take suyi mgn.

Cikin sanyi tace.
“Dama so nake muje Al-AHLI AFISHA da Laylah, ayi bincike kan lafiyar ta akan fyaɗen da akace anyi mata da kuma batun cikin da akace, in ka yarda ka bani dama”.
Tunda ta fara mgna ya yi ƙasa da kanshi Saida yaji tayi shiru kana ya motsa lips inshi a hankali yace.
“Binci ken me kuma za'ayi bayan ita da kanta ta tabbatar miki da abinda akace nayi mata, kuma Doctors sun tabbatar da batun tana ɗauke da ciki.
Ma'eeshah wani binciken ya rage?”.
Da sauri ta fara jujjuya kanta cikin yaƙini da yarda na gsky tace.
“Ban yarda cewa kayiwa Laylah fyaɗe ba, kuma bazan taɓa yardaba, kawai ina tsorone kar wani yayi mata fyaɗen da gaske ne, shiyasa nake son tabbatarwa, sannan batun cikin kuma shine babban damuwata gwara mu tabbatar da sahihancin mgnar”.
A hankali ya ɗan gyara zamansa tare da jingina kansa da jikin gadon a hankali yace.
“Meyasa kika cika yarda da yaƙinin a kaina? Meyasa kike ganin cewa banyiwa Laylah fyaɗe ba?”.
Tana taune gefen lip inta na sama tace.

“Sabida nasan bazaka aikata hakanba, kuma baka aikata ɗinba, dan zuciyata bata yarda cewa ka aikata ɗinba, domin banji tsarkin ruhinka ya ragu a rainaba, domin na gamsu kai tsarkakekkene, kuma amintacce, ka yarda min muje asibitin in Allah ya kaimu gobe!”.
Cikin sanyi yace.
“Ma'eesha tsoro nakeji kar mgnar likitocin ya tabbata cewa tana da cikin Ma'eesha infa aka samu da gaske anyi wa Laylah fyaɗe zuciyata zuciyata zata buga, da wanne hujja zan kare kaina gaban Ubangiji da bisa amanar ta da na ɗauko a ƙasarsu da alƙawarin kare maraicinta”.
Cikin ƙarfin guiwa tace.
“In sha Allah alkhairi zamu jiyo kuma Alhamdulillah ko yanzu na ƙara samun yaƙini bakayiwa Laylah komai ba kawai gadar zare aka saƙa maka ita kuma aka tura tunaninta da yarintarta ta yarda kaine,  ka gayawa Dr Amdaz da Dr Abbas su shiryawa aikin sai kuma Dr Sahra duk su shiryawa aikin”.
Kai ya jinjina cikin jin taraddadin tunanin hakan bai taɓa zuwa mishi ba.
“Dan Allah kira Dr Abbas da Amdaz ka gaya musu tun yanzu, kadama ka mance!”.
Cikin sanyi ya kira Dr Abbas yayi mishi bayanin kaɗan tunda shi yasan komai dama Yah Aryan ya gaya mishi.
Cikin gamsuwa da shawarar Ishmah Dr Abbas ɗin ya kira sauran duk yayi musu bayanin.

Washe gari ranar Sunday ƙarfe tara dai na safe suka isa nufi *AL-AHLI AFISHA CONSULTINGS HOSPITAL.*
Suna shiga harabar Asbitin B.....!

Alhamdulillah Allah ya nufa munci gaba. Yah Allah ya nuna mana ƙarshen littafin nan left dani daku makaranta da iyayenmu, yayunmu, yayanmu, ƙannnenmu, da dukkan dangin mu, harda maƙotanmu, da dukkan musulmai.

By
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 🍇🍇 *INDA RAI* 🍇🍇

*BOOK 2 PAGE 9*

Ku danna link dinnan dan shiga Group din Hausa Novel mai suna ANA ZATON WUTA A MAKERA: https://chat.whatsapp.com/GOia2rQSpDk3ewFUbK1JoL

A hankali Bilal yayi parking cikin harabar tamfatsetsen asibiti na gani na alfarmar, irin asibitin nanne mai tsari na alfarmar ba matsin ko cunkoso kusan komai na asibitin yana kamanceceniya da.
*TAJMUH CONSOLATION HOSPITAL* asibitinsu na Ethiopia.
Sai banbancin suna da abubuwan da ba'a rasaba.
Daga can saman benen aka rubuta.
*AL-AHLI AFISHA HOSPITAL*
da manyan baƙi masu sheƙin zinari.

Harabar asibitin yalwataccen ne domin parking spaces ɗin nasu, mai faɗine, wanda a ƙalla zai iya ɗaukan motoci 25, zuwa 30 ba tare da wata ta matsi wata, ko ta gogi wataba.
Sai kuma doguwar katanga da tayiwa asibitin garkuwa, yayinda bishiyoyin dabino ke zagaye dashi iyakar ganinka, sai kuma ƙasansu wasu ƴan dagwai-dagwai ɗin bishiyoyin grapes ne guntaye, masu masifar ƴaƴa da ɗan karen zaƙi, gasu ringiz gwanin ban sha'awa.
Sai daga ƙasan farfajiyar kuma, tsirran flowers ne masu ƙamshi ke zagaye da lungu da saƙo.

Daga saman Benin dake fuskantar gate ɗin kuma an rubuta.
Admin Maternity and Surgery block.
Gaba ɗaya fuskar wurin marafen Glass ne mai garai-garai wanda zaka iya ganin kanka ras a ciki.

A dai-dai gaban wurin Bilal yayi parking, yayinda Mai gadi da masu bawa flowers  ruwa, sai kuma ma cliners dake ƴan share-share da goge-goge wanda tuni sun kammala aiyunkasu domin da dama moppa suke wankewa,  masu tura duzbin na turawa gaba ɗaya Asbitin sai sheƙi da kyallin sabunta da gyara da ƙamshi yakeyi.

Da sauri Bilal ys fito tare da zagayawa ya buɗe masa marfin motar, sai kuma ya ɗan jingina gefe kaɗan hannunsa riƙe da briefcase ɗin uban gidan nashi, tare da ɗan tsayawa gefen ƙofar, sukayi jim suna jiran fitowarsa.
Yess in da sabo ai ya kamata ace sun saba a ɗan kwanakin da sukayi tare dashi sun san halin sanyinsa.
Yakan iya kai 3 minute zaune a cikin motar duk da yasan sun iso, a da can baya ma, bare yau kuma da zuciyarsa ke cike da taraddadin wanne sakamako zai samu, sai kuma ya shaƙi sassayan ƙamshi turaren Ishmah dake gefenshi, lumshe idanunsa yayi saboda duk sanda ya shaƙi ƙamshin ji yake zuciyarsa da jikinsa na samun nitsuwa.

Dai-dai lokacin kuma a can cikin Reception ɗin nasu, Dr Farida ce zaune bisa kujerar office ɗinta, yayinda Dr Abbas ke ƙoƙarin fita, da alamu waya takeyi.
Ɗan juyowa yayi ya kalleta cikin tsokana yace.
“Ga fa Dr Afif a cikin hospital nan ya shigo”.
Cikin lumshe idanu Dr ta ɗan ɗaura tafin hannunta bisa ƙirjinta da take, jin yadda Heart ɗinta ke

beating so fast, sai kuma ta buɗe idanunta tare da cewa.
“Zuciyata ta rigaka sanarmin ai”.
Murmushin Dr Abbas yayi tare da buɗe ƙofar ya fita.

Ita kuwa Dr cikin sanyi ta longwaɓar da kanta bisa wuyanta saboda jin yayarta da suke waya da ita tana faɗin.
“Wlh kina bani tausayi Farida, saboda yadda kika ɗaurawa ranki son Dr Afif mutumin da baima san kinayi ba, ke kin hana kanki yin aure kinƙi ki saurari kowa saboda shi”.
Sai kuma tayi shiru jin Dr Farida na faɗin.
“Toh ya zanyi Aunty Hidrah.
Allah ne fa ya jarabceni da son shi a lokacin da ni kaina ban sani ba, dan da fari kafin in fara ganinsa a zahiri nayi zaton muryarsa da karatun Alqur'ani da yake yi yasa nake masifar sonshi, sai daga baya na gane cewa, sone irin na aure nakeyi mishi”.
Da sauri Aunty Hidrah tace.
“To shi baima fa san kinayi ba”.
Cikin sanyi tace.
“Eh ban damu da ya sani ba, ni dai fara aiki na a hospital ɗinsa yasa na fara jin cewa lallai shi miji nane in sha Allah, tunda gashi Allah yana ta kusantani dashi Kinga da ya bar Ethiopia ma, ya dawo Qatar gashi Allah yayi na biyoshi kuma ya amshini ya bani aiki, so in sha Allah zai amsheni a matsayin matar sa, duk da a ta biyu zanzo tunda mahaifinsa ya aura masa ɗiyar aminsa.”
Cikin sanyi Aunty Hidrah tace.
“Duk da ina ganin wautarki a wasu lokutan, Amman a wasu lokutan kuma in naga Dr Afif ko naji Voice ɗinsa nakan ce dole, ƴan mata su rikice su ɗiwauce da sonshi, saboda ya kai a soshi, haibarsa da nagartasa kuma ta isa ta hana ƴan matan samun damar isar da sonsu, toh muma da muke da aure ai sai dan kariyar Allah da darajar aurene yake hana shaiɗan samun damar farma zuƙatanmu wurin sonshi.”

Shi kuwa Dr Abbas a yana murmushin ya fito.
Ganinsa ne kuma yasa ɗaya daga cikin Nurse's dake tsaye cikin Pharmacy
ta fito daga Pharmacy ɗin, ta koma Registry, inda nanne wurin aikinta.
Ita kuwa dayar ta gyara zamanta tayi, dai-dai lokacin kuma Dr Amdaz ya fito daga Consultings room 1, ganinsa yasa duk suka nitsu.
Patients insu wanda a ƙalla sun kai 16 ya kalla tare da yi musu, ya masu jiki.
Kana ya wuce ya nufi inda Dr Abbas yake gaisawa sukayi tare da juyawa suka nufi hanyar fita.
A bakin ƙofar fita Reception ɗin suka tsaya tare da zuwa aminin nasu idanu suna sakin murmushi.

Shi kuwa Taj cikin nitsuwa ya fito daga cikin motar, tare da miƙawa Ishmah hannun, hannun ta bashi, haɗe tafukan hannunsu yayi tare da harɗe yatsunsa cikin nata, kana yayi mata nuni da hannunsa ɗaya tare da cewa.
“Bismillah fito Babey”.

Sassayan numfashi ta fesar tare da ziro sawunta waje.
A hankali ya ɗan matsa kaɗan tare da jawota ta ƙarasa fitowa.

Dai-dai lokacin kuma Bilal ya buɗewa Laylah dake gaba, marfin motar tare da cewa.
“Sai na fito da kene?”.
Kai ta ɗan jujjuya kana ta fito, ta tsaya gefenshi.

Shi kuwa Taj da Ishmah, tsayuwa sukayi a jere kai kace, wata da zahara ne, sai wani irin ƙyalli da sheƙi gami da sassayan ƙamshi da suke bazawa cikin shigar su da tayi kamanceceniya.
Shi Taj cikin shigar farin wondon jeans ne sai long sleeve shirt black blue color mai masifar kyau da sheƙi, daga sama can wurin wuyansa bai maƙala botur ɗin ƙarsheba hakan ne ya bawa farar fatar wuyansa zuwa saman ƙirjinaa mai ɗauke da yalwataccen gashi kwance lip-pli ya ɗan bayyana.
Daga ƙugunsa tsadadden belt ne shima Black blue ne ɗamare da ƙungunsa wanda hakan ya bawa surar jikinsa damar ƙara bayyana cike da haiba.
Sai siririn glass irin nasu na Doctors dake manne da idonsa, wani irin kekkyawan sheƙi da ƙyalli lips in shi keyi, hakama sajensa da yake kwance lip-pli gwanin ban sha'awa.
sai kuma Half cover shoe dake sawunsa, na kamfanin Gucci shima Black blue.
Ita kuwa Ishmah wata tattausar rigace fara ƙal a jikinta, short sleeve shirt, sai kuma wondon pallazo shima fari, ta ɗaura wandan kan rigar saman cikinta kaɗan hakan ne ya bawa lafeffen cikinta bawa ƙirjinta damar bayyana ra'anul ain.
Sai kuma after dress, black blue collar, data ɗaura a saman shigar tata, wacce ta ɗan haɗe igiyar tsakiyarta kaɗan, sai farin glaye tsiriri da tayi rolling kanta da shi, wanda ya bawa kekkyawar fuska tsaro na musamman da fidda haibar kyanta, pink lips inta kuwa sai sheƙi sukeyi, hakama gashin girarta dake kwance lip kana ya ɗan haɗe a tsakiyar saman hancinta ya bada siffar W. Farin idonta ya ƙara bayyana ne, sabida ɗan kollin data zizara.
Sai kuma siririn glass fari ƙal mai garai-garai data manna a idonta.
Sai takalmi cover shoe mai ɗan karen tsini Black blue da tasa, sai wayarta dake hannunta na hagu yayinda hannunta na dama ke cikin hannun Taj ɗin ya harɗe yatsunsu gam, yana murzawa a hankali.

Sai wani irin ni'imtaccen ƙanshin mai masifar daɗi sha suke bazawa, na turaren kamanin Gucci, intense Oud.

Kusan duk a tare Ƙananan ma'aikatan nasa sukayi mishi zobe, suna kwasar gaisuwa kamar yadda ya saba yiwa ma'akatan TAJMUH, haka ya fara, amsawa yana mai jinjina musu da basu ƙarfin guiwa yake cewa.
“Aikinku yayi, manyan ma'aikatana”.
Yayi mgnar da iya kar mutumtaka tare da ɗan jujjuya ƙwayar idanunsa ganin ko ina na cikin Hospital ɗin yayi fes-fes gwanin kyau sai ƙyallin sabunta yake.
Bilal ya ɗanyi murmushi tare da gyara riƙe hannun Laylah kana yace.
“Yah Afif karfa su Yah Amdaz suce kana bawa cliners matsayinsu fa”.
Kai ya ɗan jinjina tare da cewa.

“Hmmm Bilal ai matsayin su ya ɗara na Doctors da Nurse's, domin in babu su a asibitin, ƙazanta zata sa babu Dr da zai yarda yayi aiki anan, bare kuma patients su zo ko ba haka ba Ma'eeshah?”.
Yelwataccen murmushin da yasa dimples ɗita duka biyu lotsawa tayi, tare da amsa gaisuwar da cliners ɗin keyi mata kana tace.
“Sosai ma kuwa, dan duk Kyan wuri in ba gyara lalacewa yakeyi”.
Cikin jin daɗin karramasun da sukayi, suka rinƙa godiya kana suka juya kowa ya koma bakin aikinsa.

Shi kuwa Bilal kai ya jinjina cike da gamsuwa.

Shi kuwa Taj juyawa yayi ya ɗan fuskanci gefen gabas, inda wani tamfatsen gini na musamman yake shimfiɗe daga sama an rubuta Reception. Da manyan baƙi,
Cikin sauƙe numfashi suka nufi ƙofar shigan. Bilal da Laylah na biye dasu a baya, riƙe da briefcase inashi.

Murmushin mai nuna cikar jin daɗin Dr Abbas da Dr Amdaz sukayi tare da cewa.
“Wow Masha Allah, kaga wani haɗin Allah a nan”.
Kai Dr Abbas ya jinjina tare da zaro wayarsa ya fara yi musu hoto, a duk taku da motsin tafiyarsu suna masu nufarsu.

Shi kuwa Taj tsuke fuska yayi dai-dai lokacin da suka isa gab dasu, cikin sanyi yace.
“Kai kana nan kamar yaro duk motsin ka sai kayi hoto”.
Murmushin Dr Amdaz yayi tare da cewa.
“Alhamdulillah patients ɗin yau zasu samu ganin Sheykh Dr Afif dan da yawa ma suna zuwa ne da yaƙinin zasu samu ganinka, dan haka yau zamu huta tunda ga uban gayya”.
Shi kuwa Taj fuskarshi ya ɗan kwaɓe tare da yi mishi irin kallon nan na.
“Toh  bani hanya”. Fahimtar hakan ne yasa Dr Abbas yin saurin juyawa suka shiga cikin Reception ɗin.
Yana faɗin.
“Ya naga kamar Madam ɗin ma tamuce”.
Da sauri suka kalli juna jin Taj yace.
“Tawa dai”.
Cikin sakin fuska Dr Amdaz yace.
“Eh yana nufin kamar itama likita ce ko?”.
Ɗan mirza tafin hannunta yayi cikin nasa tare da cewa.
“Itace ma mai Hospitals ɗin ai”.
Kai suka jinjina tare da biyo bayansu.

Sassayan ajiyan zuciya, Ishmah ta sauƙe lokacin da taga duk ma'aikatansu suna ta fitowa.
Ido ta zuba wa, gabansu inda nanne Registry, sai kuma gefen hagu inda Nurse's Station ke jere da Pharmacy, sai kuma gefen dama inda Consultings room 1 2 and 3 ke jere, sai kuma Pay Point, dake tsakanin su.

Parlour ƙatone wanda ke ɗauke da wasu irin tsala-tsalan kujeru na al'farma, masu taushi, ke jere daga tsakiya, wanda zai iya ɗaukan mutum 20 zuwa 30, sai kuma babban TV dake manne jikin gini, sai AC daga can sama dake fesa sassayan iska mai sauke ƙasala.
Cikin yin ƙasa da murya yadda shi kaɗai zaijita tace.
"Masha Allah komai yayi kyau".
Yana ɗan ƙara jawota kusa dashi yace.
"Alhamdulillah tunda kin yaba nasan kowa zai yaba".

Kusan duk a tare suka fito, yayinda har hada baki sukeyi wurin cewa.
Good morning sir. Morning sir. Kai yake ɗan gyaɗa musu tare da ɗan motsa lips inshi a hankali yana faɗin.
"Morning".
Daga nan kuma suka nufi Office ɗin Dr Abbas dai-dai lokacin kuma Dr Farida ta fito daga cikin Office ɗinta.
Da sauri ta mara musu baya.
Ta shiga da sallama tare da faɗin.
"Good Morning sir".
Ta ƙare gaisuwar cikin yauƙi da kwarkwasa, sai kuma ta tsaida idanunta kan fuskar Ishmah dake ɗauke da yelwataccen murmushin mai fidda haiba da kwarjinin da yasata dole ta janye idanunta, ta maidasu kan Taj ɗin tare da yi mishi kallon dake bayyana zafin sonshi dake cikin zuciyarta.
Sai kuwa tayi saurin
rumtse idanunta tayi da ƙarfi ganin Taj ɗin ya ɗan jawo hannun Ishmah ya ɗaura kan lips inshi tare da ɗan sumbata kana ya ɗan fara goga bayan hannunta kan sajensa zuwa saman lips inshi, sai kuma yasa hannunsa ɗaya ya jawo kujerar baya kaɗan, kana ya ɗan juyo ya kalleta cikin narke ido da murya ya ɗan motsa lips inshi a hankali tare da ɗan ɗaga sauti yadda Dr Farida zata iya jinsa yace.
"So sorry Babey na barki a tsaye ko, Afwan my life zauna".
Wani irin yam yam tsikar jikinta ya amsa saboda jin sautin muryasa har cikin kwanyarta.
Dr Amdaz kuwa kauda kai gefe yayi.
Shi kuwa Dr Abbas ido ya zuba wa Dr Farida data ƙara diriricewa tuni launin fuskantar ya sauya.

Shi kuwa Tajj har ranshi yana hakane dan Dr Farida ta samawa ranta salama ta daina bibiyarsa da kallon kura yaga ɗanyen nama.

Bilal da Laylah kuwa  gaida Dr Farida sukayi sai dai ina ta gaza amsawa saboda firgincin ganin kyaun sura da haibar Ishmah da kuma ganin zallan zazzafan so da ƙaunarta cikin ƙwayar idanun mutumin da tafi so fiye da kowa a duniya.

A hankali ta zauna tare da kallon Dr Farida cikin girmama kai tace.
"Dr Farida ko?".
A diririce Dr Farida ta gyaɗa mata kai tare da gaida ta, ta ɗaura da cewa.

“Kin sanni ni kuma ban san ki ba”.
Da sauri ta maida kallonta kan Taj ɗin daya ɗan shafi gefen fuskar Ishmah yace.
“Matatace. Aysha Abdallah Matawalle, Mrs Dr Afif Muhammad Taj.”
Wani zazzafan numfashi Dr Farida ta fesar tare da rumtse idanutan kana a hankali tace.
“Masha Allah”.
Ta ƙare faɗar hakan da nazarin, to dama wannan ce matar da mahaifinshi ya aura masa, kuma Dr Abbas yace mata baya sonta bata sonshi, kenan ƙarya Dr Abbas yayi mata, ai waɗanan ko mahaukaci ne ya kallesu yasan akwai true love a tsaka ninsu.”

Shi kuwa Taj files ɗin patients dake jibge kan Table ɗin Dr Abbas ya kalla kana ya kallesu tare da ɗan gyara zamansa yace.
“Kamar akwai patients da yawa, ayiwa Dr Priter mgna taji dasu, ku kuma ga patients ɗin ku.”
Ya ƙare maganar da nuna musu Laylah dake gefen Bilal.
Sai kuma ya miƙa Bilal key tare da cewa.
“Kai kuma kaimin briefcase ɗin Office na sai kaje ka dauko Dr Priter”.
Da sauri Bilal ya amshi key ɗin tare da cewa.
“To”.
Kana ya juya ya fita,

Dr Amdaz kuwa da ido ya rakashi kana ya jujjuya kai tare da cewa.
“Hmmm Bilal ya samu abinda yakeso shiyasa ko gida baya komawa, shi a rayuwarsa in dai za'a bashi mota yayi taja to burinsa ya cika”.
Kai Taj ya jinjina tare da cewa.
“Naji kuma ya yace min ya kusa komawa school”.
Da sauri Dr Abbas yace.
“A ina yake karatu ne?”.
Dr Amdaz na ɗan riƙo hannun Laylah yace.
“AL-Jami'atul Madina yake, karatu ni naso a rinƙa hanashi zuwa hutun ma”.
Cikin sauri Dr Abbas yace.
“To ku daina biya mishi kuɗin dawowa mana”.
Juyowa yayi ya ɗan kalli Taj jin yana faɗin.
“To ai hukumar makarantar ne suke biya dalibansu kuɗin zuwa Hutu suga iyayensu duk shekara-shekara kuma ma yaro nason ganin iyayensa a hanashi dawowa.”

Murmushin Dr Amdaz yayi kana yaja hannun Laylah tare da kallon Dr Farida dake kallon Ishmah tamkar madubi yace.
“Mutafi ko”.
Da sauri tace.
“Ok Laylah zo mu tafi”.
Ɗan kwaɓe fuska Laylah tayi tare da kallon Ishmah cikin sanyi tace.
“Aunty Ishmah muje tare”.
Cikin kulawa Ishmah ta miƙe tsaye tare da cewa.
“To Laylah”.

Cikin ɗan tsuke fuska Dr Farida tace.
“To ke me kika sani akan aikin likitanci? Ai sai dai Dr Afif yazo muyi aikin tare dashi”.
Cikin tsuke fuska Taj ya ɗan kalleta a fakaice kana yace.
“She's a big Gynecologist Dr, ki san abinda zaki faɗa”.
Yayi mgnar cikin kausasa murya.
Da sauri ta ɗan rusunar da kanta tare da cewa.
“Sorry Sir”.
Kai ya kauda gefe tare da kallon Ishmah Innocent face ɗinta ya kalla tare da sakin murmushi gefen baki kana ya kalli Dr Abbas da Amdaz yace.
“Kuje kuyi aikin da kulawa”.
Sai kuma ya ɗanyi ƙasa da murya yace.
“Babey kuje, Allah yasa muyi farin ciki da zuwan”.
Ya ƙare maganar tare da ɗan jawota yayi mata yar ruggumar gefen nan da yasa Dr Farida juwa ta kama hanyar fita.
Ita kuwa Ishmah murmushi tayi tare da cewa.
“In sha Allah zamuyi farin ciki”.
Daga nan taja hannun Laylah suka bi bayan Dr Farida, da Dr Amdaz,. Dr Abbas kuwa ya mara musu baya.

Kai tsaye ɗakin gwaje-gwajen su na musamman suka nufa wanda yake tsakanin Laubor room, da ɗakin Tiyata.
Ɗakin ɗauke yake da sabbin gadaje biyu, sai sabbin na'urorin na musamman, na gwaje-gwaje da kuma na haske.

Cikin 40 minutes suka gama shiryawa komai da zasu buƙata.

Cikin kulawa Ishmah ta jawo Laylah tare da yin hikinar ɗan ɗaure hannunta ta samu ta debi jininta.
Shett tace lokacin da taji zafin zira mata allurar da akayi.
Shafa kanta Dr Abbas yayi cike da tausayawa yace.
“Sorry”.
Ita kuwa Ishmah miƙawa Nurse's ɗin dake gefentan tayi tare da bata umarnin taje a goda komai na Ifyar jikinta tana jiran result.
Amsa tayi ta fita, daga nan su kuma ita da Dr Farida da Dr Amdaz suka fara bincikan Ifyar budurcin ta...

Shi kuwa Taj, tunda suka fita ya koma ya zauna bisa kujerar, tare da lumshe idanunsa ya fara karanta suratul Yusuf daga forkonta.
Haka nan yake jin masifar bege da kewar iyayensa na sakar masa raunin dayayi sanadin sinkowar ruwan hawayensa.
Sosai hawayen nasa suka tsananta zuba a dai-dai lokacin da yake karanta aya ta. 11.
“Qaalu yaa Abana malaka laa ta'amanna alaa Yoosufa wainna lahu lanasihuu”.

Kalmar Ya Abana da kuma fassarar ayar da take mgn kan yayun Annabi Yoosufa d suke yiwa mahaifinsu daɗin bakin ya basu Annabi Yoosufa suje kiwo dashi, yasashi tsananta rauninsa da hawayensa.
Suma kenan Banu Israel bare kuma yayunsa da ba komaiba mai zai hana shaiɗan nasara a zuƙatan wasunsu.

Da sauri yaci gaba da karatun domin baya son ya zargi wasu daga cikin yayunsa akan ƙaddararsa,
Musamman da yayi tuni da hadisin nan da Manzon Allah Sallallahu alaihi ke cewa.
“Azzannu zambu walau kana haqoon”.

Ethiopia.
Malam ne zaune a tsakiyar Parlour'sa yayinda duk ƴaƴanshi mazan ke zagaye dashi duk suna zaune gabansa sunyi ƙasa da kawunan su.

Doha Qatar.
Bayan fitarsu Ishmah da kamar awa ɗaya da rabi.
Yaji an banko ƙofar Office ɗin da ƙarfi.
Cikin sauri ya ɗago kansa,
Idanunsa ya zaro baki ɗaya ganin wani irin taku da Ishmah keyi tare da nufosa gadan-gadan.

Tana riƙe da takardun Result's ɗin gwaje-gwaje da sukayi wa Laylah.

Wani irin kiɗimemmen numfashi ya fesar da ƙarfi tare da rumtse idanunsa da azaban ƙarfi lokacin da yaga ta watso mishi ta....!

Kuyi haƙuri ba editing zakusha typing errors.

*Littafin INDA RAI na kuɗine 1k ne kacal ki biya ki karanta cikin aminci ba haƙƙin kowa a kanku 0661110170 GTBank Aisha Aliyu Garkuwa sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276.*

By
*GARKUWAR MARUBUTA*
[4/30, 10:43 PM] +234 706 616 8286: 🍇🍇 *INDA RAI* 🍇🍇

*BOOK 2 PAGE 10*

*Yauwa Lahadi 😭😭😭28/04/2024. Wanda yayi dai-dai da cika watanni uku cib da rasuwar ɗan uwana! Ƙanina Hamisu Aliyu Garkuwa, Yah Allah kaine mahaliccinmu kuma kai mai yawan gafara da rahama ne a garemu duk da yawan zunubanmu. Ya Allah ka jiƙan wannan bawa naka Hamisu kayi mishi gafara da rahama ka yafe mishi kura-kuransa ya rabbil alamin ka yalwata makwancinsa ka faɗaɗa mishi ka haskaka mishi, ka ni'imta mishi kasa kushewarsa ta kasance mishi dausayin Jannatul Firdausi dashi da mahaifiyarmu da ƴan uwanmu Abubakar da Auwal. 😭😭😭 Ya zuljalalu Wa ikrami ka yafe dukkan magabatanmu musulmai*
*mu kuma ka bamu lafiya da nisan kwana da imani da dauwamemme. Ka bamu kekkyawan rayuwa da ƙarshe kasa mucika da kyau da imani. Ya Allah kasa mana haƙuri da juriyar rashin iyayenmu da yan uwanmu🙏🏻🙏🏻😭😭😭 yan uwa makaranta inayiwa Ɗan uwana Hamisu barar addu'a Qulhu ƙafa uku uku a gareku Allah ya kai haske kushewarsa*

*Dan Allah in dai kinsan baki shirya sayaba kada kimin mgn, masu cewa wai sun goda suga number'n nayine, ko kuma a'a bari dai in na shirya zan sake miki mgn, ko kuma yanzu dai kuɗin bai cikaba tukun sai sun cika, ko kuma a wanne gari kike, kai munyi nisa, toh in ba iyayiba ai duk nisan state da kike ba ruwan mota ba inda bazai kai mikiba, nake turawa ƴan ƙasashen wajema. Kuyiwa Allah da Manzonsa in dai in kinsan Baki shirya sayan kaya ba ku daina min mgnar ku bari sai kun shirya,kada kizo ki ɓata min lokaci a banza, wlh ni na tsani harkar karanta, duk bayani na gamayi in dai saya zakiyi ga kuɗin kaya ga account no ga numberta ai sai ki biya kawai kafin kimin mgn. Tunda dai ga alamominshi da duk illar da yakeyi na faɗi in kina dashi faƙat in babu kada ki wani zo kice min bayani dan ko kinzo iya bayanin da zan miki kenan*
Alamomin infection sune kamar haka. Rashin sha'awa. Kaiƙayin gaba Kiji idan ya fara miki ƙaiƙayi kamar zakiyi hauka. Warin ko ƙarnin wurin. Fitar farin Ruwa mai fatsi-fatsi. Ƙurajen su ɗan fetso ƙananan ko ƴan manya, melewar fatar wurin, Tusan gaba. Bushewar gaba, Rashin ni'ima. Buɗewar gaba, domin har budurwa infection na iya buɗata. Ciwon mara ko ciki mai tsanani yayi al'ada, rashin haihuwa, domin har baƙin mahaifa take toshewa. Ko kirinƙajin wani abu na miki yawo ƙasan mara, ko jin zafi yayin yin fitsari, da kuma saduwa, da dai sauran abubudann ban lissafa. Sune manyan alamomin infection.
Shin kin kuwa san illar da infection keyi miki, amman kinajin ɗaya daga cikin alamominta kinyi bulum buƙui da ita a jikinki. To bari kiji illolin infection wato cutar sanyi.
Rashin haihuwa, ƙyara da hantara a wurin miji domin muddin kina tare da ita baki da wata daraja a idanu nai, sabida ƙyamas kike ba damshi bare wata ni'ima mai Taste, Kinga kenan shinfida ta lalace, in kuwa shinfiɗa ta lalace dole kiga sauyin fuska, domin su maza dole sunason wurin da kwaranya, zaki kasance baki da wani daɗi da ɗumin da mai gida ke buƙata. Kinga duk tsabtarki da kyanki da iya girkinki shinfidarki ta zama lami. Kiyiwa Allah ki nemawa kanki lafiya ki samawa mijinki da ke kanki nitsuwa.
KADA KUJI IYA WANNAN DOMIN AKWAI MUGUN INFECTION WANDA BAYA BAYYANA KANSA. Wanda kawai sai dai kijiki, kamar kwalta kin bushe ƙyamas ya dauke miki dukkan sinadaran ni'imomin ki, da sha'awarki, duk kayan matan da zakisha a wofi zadai kiji ƴan uwa da abokan arziki da ƙawayenki na yaba miki magunguna GARKUWAR MA'AURATA, amman ke in

kinsha jiya I yau,  duk nacin oga da yi miki wasannin bazaki ji sha'awa ba, toh wlh muguwar infection ce, wacce bata bayyana kanta har sai ta gama yi miki rugu-rugu. Ta lalata miki zaman aure. Lokacin da zata bayyana sai kiji Doctor's suna kira miki, ovarian cyst, ko kuma fibrod duk a cikin chronic infection ne yar uwa.
INFECTION set ɗinmu na kowa da kowane Mata, Maza, Bazawara, Budurwa, Maijego, Yara, Ke yar uwa Wlh har maiciki zatasha, bashi da matsalar komai Maganin na Gargajiya ne mai rakake INFECTION ya fito miki dashi, wlh duk nacin infection koda na cikin mahaifane bi'izinillahi ta'ala zaki rabu dashi, cutar infection cutace mai masifar naci, so yar uwa kana dole ki nace masa da maganin set ɗin na 10k ne kuma maganin kala biyarne nasha da kala uku na tsarki ɗaya na shafawa ɗaya. Yar uwa idan har kin saya to kiyi ƙoƙarin kisha da mijinki, in akwai abokiyar zama, kisa miji ya saya mata, domin ko kin rabu da shin dai ita tana dashi tofa kin kashe macijine baki cire kaiba, ma'ana zai sake dawo miki, idan kuna da yara suma a saya musu, domin tsoron kada ya riƙa a jikinsu musamman ya'ya mata ya buɗa miki ƴa tun tana ƙaramarta, ki aurar da ita miji na muku kallon lalatattun iyaye da baku iya bada tarbiyaba. Saboda yamayin garin yasa ina raba rabin set ɗin in sa miki komai rabi-rabi 4k amman set ɗin 8k ne. Idan kin san a shirye kike ga account number na nan 0005388578 Jaiz bank AISHA ALIYU GARKUWA, ki turo kuɗinki kafin kiyi min mgn ta WHATSAPP NUMBER'N na 08069423567 sai ki turo min shaidar biyanki, domin akwaishi Available ko yau kika tura kuɗinki, gobe kayanki zai taho, ina bada sari ko sayan ɗaɗɗaya. Farashin Sari da sauƙi daga kan mutum 3 ko 6 ko 12. Kai ko na mutum 24 kikeso in Sha Allah zaki samu. Please dan Allah in dai kinsan baki shirya sayaba kada kimin mgn ki bari sai kin shirya. Taku ce dai GARKUWAR MA'AURATA.

Tattausan murmushi mai cike da matsanancin jin daɗi ta watsa mishi, tare da ƙara sawa gareshi cikin sassarfa.
Buɗe idanunsa yayi da sauri lokacin da yaji ta Abka jikinsa, tayi mishi wani irin amintaccen ruƙumar dake nuna tsananin farin cikin da take ciki mara adadine.

Kar-kar haka jikinsa ya saki wani irin tsuma da ɓari da yasa shi ware hannunsa duka biyu yayi mata wani irin sahihin rugguma, tare da cusa kanshi tsakanin wuyanta da kafaɗarta.

Cikin Muryar dake bayyana samun salama, aminci, yaƙini, gamida nutsuwa mai tafe da tsananin farin ciki ta fara magana.
“Alhamdulillah Yah Sheykh na godewa Allah, ya tsarkake min kai ya nesantaka da kaidin magautanka, ya kare Laylah da mugun fatan, mun tsallake makircin makiran dake saƙa maka gadar zaren Allah ya warware mugun saƙansu.
Yah Sheykh Wallahi! Tallahi! Laylah tana nan da budurcinta, babu abinda ya sameta, kuma bata da ciki, namiji bai taɓa raɓar jikintaba she's varging Yah Sheykh ba abinda ya samu ƙuruciyarta bata da cikin da akace ma duk ƙarya ne”.
Rungume juna sukayi ƙam-ƙam tare da fara sakin numfarfashi a Jere a jere.
Ya ilahi ya mujibat da'awati yah hayyu ya ƙayyum bi rahamatika astagis.
Sune tasbihan da Taj ya fara jerowa a saman lips inshi, tare da ƙara matseta a ƙirjinsa tamkar zai maida ita jikinsa, sai wasu irin amintattun ajiyan zuciya da numfashi yake sauƙewa a jere a

jere yadda kalaman Meymey na cewa Laylah nada ciki kuma shi yayi mata ciki suka gigitashi tare da fiddashi daga hayyacinsa da ɗimautashi da janye kuzarin sha'awarsa na komai a duniya.
A kuma lokaci ɗaya kalaman Ishmah suka dawo da mishi nutsuwarsa, lafiyarsa, tunaninsa, farin cikinsa, harma da kaso 60 cinin ɗari na sha'awarsa suka diro mishi in one second, sai ragowar kaso 40 da fushin Yah Abana da kewar Ummeeynshi ya danneshi.

Ethiopia
Cikin tsuke fuska da bayyana fushi da juya harshe ih zuwa bada umarni Malam ya kalli yaran nasa tare da yin gyaran murya yace.
“Na taraku ne, domin in gargaɗeku, in kuma baku umarnin ku gargaɗi fitsararrun ƴaƴanku more especially, Arfah da Imran da Hameedah kada wanda ya sake turo min hoto ko vidios ɗin Abban..”.
Sai kuma yayi saurin katse mgnar da zai ƙarashe da kiran sunan da yake kiran Taj dashi
Sai kuma ya ƙara tsuke fuska.
Jin Yah Hafiz na cewa.
“Afwan Malam kayi haƙuri ka gafarcesu, in sha Allah zamu ɗauki mataki a kansu”.
Juyowa yayi ya kalli Yah Aryan da yayi ƙasa da kansa cike da takaicin Arfah yace.
“Kai Aryan ka gayawa ɗanka Arfah ya goge Number ta a wayarsa tunda shi yafi kowa tsaurin ido da rashin kunya, har ni Arfah zai turawa video Afif harda cemin, in dai da ɗingon imani a zuciyarka dole kaji tausayin Uncle Taj kuma dole ka dawo dashi cikin ahlinka.
Aryan har ka haifi ɗan da zai nuna min cewa banida imani ko ɗigo kenan, shi ya haifa min Afif ɗin ne? Ko shi zai gaya min yadda Zan hukunta ƴaƴana in sunyi laifi, to Wallahi ka rabani da Arfah kafin in rabaka da kaina”.
Cikin tsoro Yah Aryan ya rinƙa girgiza kai tare da cewa.
“Afwan Malam in sha Allah haka bazata sake faruwa ba, zanyi maganin Arfah da yardar Allah.”
Sai kuma duk suka juyo suna kallon Yah Abduraham da suka ji shesh-sheƙan kukansa na tashi a hankali murya na rawa yace.
“Malam kayi min izini in tashi, in fita tunda ni dai bani da ɗa, ko ƴa kaga bana cikin masu laifin ko!? fatana kuyi min addu'o'in Allah ya bani ɗa mai kama da Afif mai irin halinsa da nagartasa da tarbiyarsa, zan soshi zan kusanta kaina dashi koda kuwa ace irin ƙaddarar sharrin data faru akan Afif ta faru a kansa sau uku ne, ni zan soshi bazan nesanta da shiba, tunda ni ƴaƴan basu dayawa bazan koreshi in nesan tani da shiba, dan ina jin ina da wasu kusa da niba. Yah Allah ka azurtani da ɗan kamar Afif, zan riƙeshi kamar yadda kace su ƴaƴan amanace ga iyayensu kuma ababen kiyayewa da tambaya ne”.

Wani irin murmushin mai haɗe da ruwan hawaye Yah Yusuf yayi sabida fahimtar Abduraham nayiwa mahaifinsu tunasarwa ne kana abinda yayiwa Taj dan yana ganin Allah ya bashi yara da yawa, ya kuma mance cewa suma ƴaƴa amanane akan iyaye, ya haɗe mgnar da nuna mishi ita ƙaddara ba'a guje mata.

Shi kuwa Malam ido ya zuba wa Abduraham har Saida ya dasa ayar ƙarshen mgnar kana yace.

“Ka gama!?”.
Cikin sanyin Yah Abduraham ya gyaɗa mishi kai alamun eh ya gama.
Numfashi mai zafi ya fesar kana yayi gyaran murya tare da tsuke fuska yace.
“Na fahimci cewa kai ke zuga Arfah da Imran da  Hameeda yar Yusuf na fahimta ashe kaine ke ingizasu da tsara musu abinda zasu faɗa min kamar an sauƙo maka da wahayin maganar ba shakka Abduraham ka iya falsafa.”
Da sauri ya fara girgiza kai hawaye na zuba yace.
“Kayi hakuri ya kai mahaifina, wlh tun ranar da kace baka yafe mana muyi alaƙa da Afif ba, ko sunansa ban sake kira a saman lips ɗina ba, sai dai kayi haƙuri da aikin gafara, domin duk sanda nayi salla inayi mishi addu'o'in a cikin dukkan sallolina, tunda bakasa yi mishi addu'a a cikin sharaɗinka ba”.
Cikin tsuke fuska ya nuna mishi hanyar fita, da sauri ya miƙe tare da cewa.
“Ka gafarceni malam”.
Daga nan ya fita, su kuma sukaci gaba da zama suna jin gargaɗin mahaifin nasu Yah Hafiz kam sosai yaji daɗin kalaman Abduraham domin ko ba komai ya tunasar da mahaifin nasu cikin hikima.

Qatar.
Kusan gaba ɗaya ido suka zuba wa Taj da yayi sujudushukur a Office ɗin Dr Abbas ɗin.
Murmushin Dr Amdaz yayi tare da zama bisa gadon dake can gefe.
Dr Abbas ɗin kuwa ɗaga Laylah yayi ya zaunar da ita gefen Dr Amdaz.
Dr Farida kuwa ido ta rumtse cike da kishi ganin yadda Taj ya kuma sake ruggume Ishmah tare da tallabe fuskantar da tafukan hannunsa duka biyu lips inshi ya manna kan goshinta tare da liƙa mata amintaccen kiss bisa goshinta.
Cikin Muryar dake nuna zafin so da ƙauna da matsayinta a rayuwarsa yace.
“Duk sanda na shiga duhu kece ke isowa inda nake duk tsananin duhu, sai kin iso gareni sannan ki haskaka min wurin, duk sanda na zubda hawaye kece ke shara minshi, ko a mafarki baki taɓa barin na zubda hawaye ba, in kin bani shawara ko yaya sai na samu al'khairi a cikinta, shiyasa koda a mafarki kika ban shawara sai na bita.
Ma'eeshah kin zame min Noor ala Noor. Laisa lee misluki abadan Hayateeh ana uhubbiki Hubban shadidan wa axeeman wa kabeeran Yah Hayateeh.
Duk ƙanƙamtar munin furuci ko suffa bakya kusantani dashi kinyi min yardar da har abada babu macen da zata yi min wannan yardar.
Tukucinki in soki ke kaɗai in killace ki a zuciyata ke ɗaya, in hana ko wacc mace  kusantar zuciyata, Babey ni zanyi miki kishin kaina da kai na. I love You Every second every minute, of every day.
Sai kuma ya ɗan ƙara ruggume ta tare da kwantar da kanta ƙirjinsa cikin sanyi murya yace.
“Ma'eeshah kin min yardar da ko Ummeey wa Abeey basuyi min irinsa ba”.
A hankali ta ɗan fara janye jikinta saboda jin wani irin buga ƙofar da Dr Farida tayi bayan ta fita.

Shima saketan yayi tare da komawa ya zauna, kana ya nuna mata kujerar kusa dashi ta zauna.

Cikin sanyi yace.
“Maeesha ba mafarki nakeyi ba ko!?”.
Cikin yaƙini da sanin aiki da iyawa Dr Abbas yace.
“Ba bacci kakeyi ba, idonka biyu, kuma tabbas abinda kaji hakane Laylah bata san namiji ba, kuma bata da ciki”.
Cikin gamsuwa da mamaki yace.
“Toh Amman meyasa duk kamanninta suka sauya har amaifa takeyi, gashi tayi wani irin fari irin na masu ciki gashi sai ƙara girma takeyi”.
Cikin nutsuwa Dr Amdaz yace.
“A binciken da mukayi mun gano cewa,
Allurar sauya launin fata  akayi mata shi yasa taketa ƙara zama kalar masu ciki.
Sai kuma allurar super appatite shine yake sata yawan bacci da kasalar, kuma ƙarfin da yayi mata Shiyasa take yawan amai dan shekarunta basu kai ɗauka ba, shiyasa madadin ta yawaita cin abinci sai yawan amai.
Amman Alhamdulillah yanzu duk anyi maganin matsalolin an haɗa mata maganin da zatayi tasha ya kauda ƙarfin alluran, sannan batun budurci ta kuma.
Duk inda za'aje a duniya a gwada amsa ɗaya zai baku so ba dalilin yin ciki”.
Ita kam Ishmah shiru tayi tana nazarin tabbas akwai lauje a cikin naɗi akan likitocin da sukayi ta gwada Laylah a Ethiopia.

Numfashi mai nauyi ta fesar tare da kamo hannun Laylah ta jawota jikinta a ranta take nazarto. Lallai an shirya wa makircin tunda anyi nasar  sa Laylah tsoron Taj, har take bada tabbacin lallai ilaihin tabbas Taj yana zuwa ɗakinta ya kwanta.
Cikin sauƙe numfashi ta kalli Taj daya miƙe tsaye ruggume juna sukayi da Dr Amdaz kana ya ruggume Dr Abbas, sai kuma ya matso kusa dasu, shafa kan Laylah yayi wacce ta bishi da idanu cikin alamun tsoronshi ya fara ɗan raguwa a ranta, tun lokacin da aka shaida mata ciki da bayanan da Ishmah tayi mata,
Cikin tsananin farin ciki yace.
“Laylah ce Alhamdulillah”.
Cikin sanyi tace.
“Alhamdulillah Uncle Taj”.
sai kuma ya riƙo Ishmah kana yace.
“Mu tafi”.
Ya ƙare maganar yana ɗan murmushi.

Kusan a tare suka fito da rakiyar su Dr Abbas.

Suna fita Bilal na isowa, shiga motar sukayi kana yaja suka tafi gida.

Nigeria.
Abba ne zaune a Parlour'n sa Khalid da Mahamud da Minat ne zagaye dashi cikin jin daɗi Khalid yace.

“Abba Daddy'nmu ya yarda in na gama Secondary School zan koma wurin Mamey na, kuma yace ma, in an bamu hutun Ramadan zamuje”.
Murmushin Mahamud yayi tare da cewa.
“Yaro ana jirgaka yanzufa kusan wata shida ne ya rage Ramadan ɗin”.
Da sauri Minat tace.
“To ai zaizo kamar yau, wlh Daddy ya yarda yace zamu je”.
Cikin so da ƙaunar jikokin nasa yace.
“To Allah ya kaimu lokacin bisa rai da lfy, yau ma kwana zamuyi sai gobe ku koma ko?”.
Kai Minat ta jujjuya tare da cewa.
“To ai gobe Monday akwai school”.
Da sauri Khalid yace.
“To ai dukanmu sai 12:00 zamu tafi, zamu ƙara kwana da safe Uncle Hamisu yace zai maidamu”.
Kai Minat ta jujjuya tare da cewa.
“Amman kasan za'ayi mana faɗa mun ƙara kwana ɗaya kan ɗaya da aka bamu ko”.
Gyaran murya Abba yayi tare da cewa.
“Ba komai zan kira Daddyn naku in tambaya mana shi”.
Sai kuma duk suka kalli ƙofar shigowan jin Hamisu na cewa.
“Ai na tambayeshi ma, yace ba matsala da safe in maida su”.
Tsalle suka fara cikin jin daɗin, sai kuma Khalid ya tsuke fuska tare da cewa.
“Kuma tun da safe nake cewa ku kira min Mamey na baku kira min ita ba”.
Hannunshi Hamisu ya kamo tare da cewa.
“Zo mu tafi ball sai anjima in sake kiranta, na kirata sau biyu bata kusa”.
Daga nan suka fita.

Qatar.
Addawa ce ruggume dasu duka biyu Taj da Ishmah, cikin tsananin farin ciki, sai kuma ta sakesu tare da fuskantar alƙibla tayi sujudushukur, sai kuma ta tashi tare da fara ƴar rausayawa irin tasu ta tsoffi.
Kelƙelewa da dariya Laylah tayi harda riƙe ciki
Zulaihat ma dariyar takeyi.

“Alhamdulillah Allah kaine abin godiya, Ubangijin talikai maiyin yadda yaso a lokacin da yaso, mu dai yau haske yazo ya yaye duhun zuƙatanmu, nayi sujjadar godiya a gareka Allah ka ƙara amintar da gskya a cikin zuciyar bawanka Muhammad ya yarda dq nagartar ɗansa Tajuddeen”.
Cikin sanyi Ishmah tace.
“Amin Ya Allah”.
Sai kuma ta nufi Dinnin area da sauri tare da cewa.
“Ishmah ku taho kuci abinci, muyi farin ciki mu godewa Allah”.
Hannun Laylah Ishmah taja kana suka nufi Dinnin area.

Zama sukayi tare da jawo plate dan Allah ya sani yunwar sukeji dan basu karya ba suka fita.

Cikin kulawa ta kalli Taj dake zaune bisa kujerar 3 sitter bai tasoba.
“Yah Sheykh kazo muyi breakfasts”.
Kanshi ya ɗan jinjina tare da yi mata kallon aminci kana ya taso yazo.

Bayan sun ci abinci a hankali ya miƙe tare da kallonta kana ya kalli Laylah dake sauƙa daga kan steps ɗin cikin sanyinsa yace.
“Kinyi komai saura ki cire tsorona, a zuciyar Laylah ki tabbatar mata cewa ni matsayin uba nake a gareta, ni tamkar yata ta cikina nake jinta”.
Cikin jinjina kai tace.
“In sha Allah kuwa”.
Gefen fuskarta ya ɗan shafa tare da cewa.
“Zan shiga ciki in ɗan watsa ruwa in tafi masallaci, sai na dawo ki kai min tea”.
Kai ta gyaɗa tare da kallon time ɗin wayarta kana tace nima bari in shiga.

Daga nan ya haura ita kuma ta shiga bedroom ɗinta.

Wanka tayi tare da sauya shiga zuwa doguwar rigar  atampa pink color da ɗan ratsin golding collar and white.
Ɗas rigar ta zauna a jikinta, hijabi tasa tayi salla bayan ta idar, ta ɗan ƙara turaruka a jikinta tare da mirza ɗaurin asetta.

Jin wayarta nata ringing ne yasata saurin ɗauka.
“Babeyyy!”.
Yayi mata kiran can ƙasan maƙoshinsa da wani irin salon da yasa tsikar jikinta amsawa cikin sanyi tace.
“Na'am”.
Gyara zansa yayi a kan carpet ɗin Parlour shi tare da cewa.
“Zan sha tea”.
Tana fitowa Parlour'n tace.
“To gani nan zuwa”.

Addawa kuwa tana shiga ɗakinta ko sallan bata yiba, saida ta kira Ummeey Taj tana ɗagawa tace.
“Alhamdulillah yau dai dole in nemeki kuma inyi miki maganar Afif tunda cikin sharaɗin mahaifinsa babu batun in kinyi mgnarsa dani akan aurenki”.
Cikin sanyi Ummeyy dake zaune kan salla tace.
“Ai dama kullum ina son tambayarsa fushikin nake tsoro na cewa kada in dameki da magarsa nake shiru yana Ify?”.
Cikin farin ciki Addawa tace.
“Toh Alhamdulillah, yana Ify matarsa na Ify. Laylah tana Ify nima ina Ifya Zulaihat na lafiya, uwa Uba kuma yau a Asbitin suka wuni shida matarsa da Laylah, anyiwa Laylah duk gwajin da ya dace, wlh bata da ciki kuma ba'ayi mata fyaɗe ba”.
Tunda Addawa ta fara mgn tayi kasake sai jin kalaman Addawa na ƙarshene yasata faɗawa tayi

sujudushukur tare da yiwa Allah kirari.
“Yah Allah masanin zahiri da baɗini, ya Allah kaine mafi ƙololuwar sani, kasan cewa ɗana tsarkakekke ne ya Rabbi kasan waɗanda suka shirya mishi wannan gadar zaren, ya hayyu ya ƙayyum bi rahamatika astagis Allah dan tsarkin Alkur'ani mai girma da nauyin kujerar al'arshinkan Allah ka hana duk wanda ya samu cikin wannan masifar samun farin cikin rayuwarsa, kasa ya tonawa kansa da kansa asiri ya rabbil izzati ka ƙara fidda gskyar mai gsky ka huci zuciyar mijina mahaifin Bawanka Tajuddeen ya yafe masa ya barni in kasance tare da ɗana kamar ko wacce uwa da ɗanta”.
Tunda ta fara jero addu'o'i da Amin Amin Addawa ke amsa mata cikin jin daɗi.

Tana gama waya da Addawa duk ƴaƴanta mata ta kirasu ta basu labarin yadda akayi, hakan yasa kaso 40 na ɗarin cikin damuwarsu ya bar zuƙatansu sun huta.

Ajiye cup ɗin tea ɗin yayi bisa Tray kana ya ɗan turashi gefe,  ya kalli Baby face ɗin cikin kulawa yace.
“Babey Are you okay?”.
Sassayan numfashi ta fesar tare da lumshe idanunta murya a kasalance tace.
“A I'm so tired, bacci nakeji”.
Ta ƙare maganar tare da buɗe idanunta a hankali ya ɗan gyara zamansa tare da matsowa kusa da ita, hannunshi yasa ya jawota jikinsa, sai kuma ya ɗan jingina bayansa da jikin kujerar dake bayansa.
Ware sawunsa yayi ya sata a tsakiyar sawun nasa kana ya miƙe sawun.
A hankali ya ɗan ƙara jawota, jikinsa tare da kwantar da ita kan cikinsa ya manna kanta kan ƙirjinsa.
A tare suka sauƙe numfashi gami da lumshe idanunsu.

A hankali ya manna lips inshi kan goshinta yayi mata sassayan kiss.
Hmmmmmmmmm suka ja numfashi tare  shaƙan ƙamshin jikin junansu.

A hankali ta ɗan gyara kwanciyarta bisa jikinsa.

Gefen lip inshi na sama ya ɗan ciza da ƙarfi saboda yadda yaji lafiyar jikinsa na amsa yanayin da tunda ya shiga iftila'in nan bai sake jinsa ba.

Dogon numfashi yaja tare da maida kanshi ya jingina.

Ethiopia.
“Ummi ce tsaye gefen Adaya dake zaune bakin a Dinnin table tare da matse ruwan Lemon ɗin data yanka cikin peppered chicken da takeci, da sauri ta yamutsa fuska saboda gani take kamar ita ke cin masifeffen yajin da ake gaurayeshi da tsamin.
“Kici a hankali mana”.

Ta faɗa tana zama gefenta.
“Sauri nake zan tafi”.

“Wurin rawa ko?”.
Ummin ta tambaya cike da takaici.
“Tana ɗan matse lemon ɗin tace.
“A'a zamuje ayi mana E passport ne”.
Cikin sauri tace.
“Na zuwa ina”

A taƙaice tace.
“India”.
Cikin takaici tace.
“Da izin waye zakije”.
Miƙewa tsaye tayi tana goge bakinta da Tissue tace.
“Da izinin Ubangiji, in dai Allah ya yarda zanje, yardarsa kaɗai kuma nake buƙata”.
Ta ƙare maganar tana sauƙa daga kan steps Dinnin table ɗin tare da jujjuya ƙugu da ido kawai ta iya rakata, dan tasan Adaya bata tsoronta bare shayinta kai Abpu ma ba tsoronsa takeji ba. Aminullah dake kwance a Parlour'n ya ɗan ja gajeren tsaki, haransa tayi kana ta wuce ta tafi tana faɗin.
“Ni dai kuyi min addu'a Allah ya bamu sa'a, tunda dai kun san cewa nasarar nan dai ba tawa bace ni kaɗai, ina samun nasara tamkar ku kuka samu, musamman Abpu dan sai na fiddashi waje anyi mishi aiki”.
Kasake kawai sukayi suna kallonta, har ta ɓacewa ganinsu.

Qatar
Da dare misalin ƙarfe goma,
Kwance a kan gado tayi ruf da ciki, ta ɗan ɗaura ƙirjinta bisa pillow tana riƙe da wayarta video call takeyi dasu Khalid a wayar Hamisu sai kuma tace a kaiwa Abba wayar. Bayan sun gaida ne tayi Murmushin cikin jin daɗi tace.
“Abba yanzu dai Hamisu ya daina kuka ko?”.
Yana kallon Khalid da Minat dake matsowa yace.
“Ah sosai ma, yanzu shike tausar Rahama ma kafin su tafi Gombe ita da Khadijah”.
Cikin sanyi tace.
“Yauwa Abba to batun zuwan Hamisu fa, wata biyu kaɗaifa zaiyi ya dawo”.
Ta ƙare maganar tare juyawa da sauri dan jin motsin mutum ya kwanta kusa da ita, kana yayi mgn.
“Barka da dare Abba”.
Murmushin jin dadi Abba yayi tare da cewa.
“Barka dai Tajuddeen ya koke-koken Boɗɗi na”.
Ɗan juyowa yayi ya kalleta ganin ta ɗan matsa gefe.
Sai ya ɗan ƙara matso da kanshi cikin girmamawa yace.

“Abba ta ɗan rage”.
Sai kuma yace.
“Yauwa Abba dan Allah a tsamma mana Hamisu yazo ko wata biyu ne muyi, Please Abba dan Allah”.
Kai Abba ya ɗan jinjina tare da cewa.
“To yanzu dai ga ƴaƴanku sun dameni in basu waya, sai da safe mayi magana Allah yayi muku al'barka”.
Ya ƙare maganar tare da miƙawa Khalid wayar wanda yaketa turo kai yana faɗin.
“Hi Uncle Taj”.
Murmushin Yayi tare da cewa.
“Hello my Son ya kake? Ina my Daughter da Dr Mahamud”.
Yayi mgnar cikin son yaran.
Tsalle Khalid yayi tare da cewa.
“Gasu can suna game ni uncle Hamisu yace in kawowa Abba waya”.
Yana ɗan ƙara matsowa jikinta yace.
“To kace ina gaidasu.”
Da sauri yace.
“Toh Uncle yaushe zaka kawo mana Mamey na. Nayi missing nata, Mamey I miss You so much”.
Murmushi tayi tare da cewa.
“Miss U to autana Mamey, ba kace Daddy ya yarda zaku zo a Ramadan ba”.
Da sauri yace.
“Ehh, kuma nace miki Ni ba auta bane ina son ƙanne masu cemin Yaya in samu ƙanwa muyi ta faɗa kamar yadda Uncle Hamisu da Aunty Rahama sukeyi, kuma ai Kinga Daddy ma da mace tayi auta”.

Ɗit-ɗit wayar ta bada sauti alamun Data ya ƙare.
Da sauri ta ɗan zaro idanunta waje dabida jin yadda yasa yatsunsa biyu ya ɗan matse lips inta fuska a kwaɓe yace.
“Kar ki sake cewa Khalid auta, kinji shima baya so, yana son ƙanne ahli Afisha.”
Ya ƙare maganar tare da ɗan zaro harshen sai ya ɗan lashi lips inta da ta cinno gaba.
Murmushin yayi ganin yadda ta rufe idanunta.
Lips ɗin ta ya zubawa ido,  tare da shaƙan ƙamshin jikinta.
Sassayan numfashi ta fesar tare da ɗan turo tongue ɗinta ta ɗan lashi lips inta da.
Allah mai komai maiyin yadda yaso a lokacin da ya ga dama, wai ni da Taj ne a matsayin ma'aurata gamu ƙasa ɗaya gari ɗaya gida ɗaya gado ɗaya.
A hankali ta buɗe idanunta saboda jin ya ƙara matsowa gareta, kanshi ya ɗaura kan pillow da kanta yake, haka yasa suka zama suna fuskantar juna.
Ido cikin ido suke kallon juna, tamkar yau suka fara ganin juna.
A hankali ya ɗan mirgino ya matsota sosai.
Uhmmmm, suka dire numfashi a tare lokacin da ya manne lips inshi da nata.
Sai kuma yasa hannunsa bisa wuyanta, tare da fara mirza babbar yatsarsa ƙasan kunnenta zuwa bayan kunnen.

Yana mai lasar saman lips inta tamkar ya samu lollypop.
A tare suka rufe idonsu kuma a tare suka buɗesu.
Jawota jikinsa yayi tare da yi mata sahihin rugguma a haka bacci yayi awon gaba da su.

Da asuba hankali ya ke kiciniyar buɗe ƙofar Parlour dan so yake ya koma side ɗinsa yayi al'walan tafiya sallan asuba.
Addawa kuwa da tun fitowarsa taji alamun takun mutum ne yasa ta ɗan buɗe ƙofar ɗakinta, Ido ta zuba mishi ganin ya juyo ya nufi ɗakin Ishmah.

A tsakiyar ɗakin ya sameta tsaye bisa alamu yanzu ta sauƙo kan gadon, a hankali ta ɗan sunkuyar da kanta tare da kallon rigar baccin dake jikinta wacce cibiyar ta ke fili, sai kuma wondon da iyakarsa guiwa cinyoyinta sunyi santal-santal a ciki.
A hankali ya kamo hannunta cikin sanyi yace.
“Babey ƙofar ba key a jiki ina kuke ajiyewa, muje ku buɗe min”.
Kai ta ɗan jinjina tare da yin ƴar miƙa tace.
“Kan Dinnin table Addawa ke ajiyeshi”.
Hanya ya nuna mata tare da cewa.
“Muje to”.
Kai ta gyaɗa mishi kana tayi gaba.
A hankali take takun Amman duk da haka bai hana mazaunanta yin mazarin da yasashi liƙa idanunsa a kansu.

A haka suka fito Dinning area ta nufa shi kuwa yana biye da ita a baya.

Ita kuwa Addawa ido take binsu dashi fuska ɗauke da murmushin jin daɗi a fili tace.
“In sha Allah farin cikinka zai dawo Taj domin kayi dace da Mar'atussaliha”.
Ta ƙare maganar a hankali.

Sai kuma ta kuma ware idanunta dai-dai lokacin da suka isa bakin ƙofar Parlour.
Key ɗin ta zira cikin ƙofar.
Shi kuwa Taj a hankali ya ƙarayin taku biyu zuwa uku, har dai ya isa gab da ita.
A hankali ta ɗan juyo lokacin da taji ya kife tafukan hannunsa kan hips ɗinta.
Sai kuma ya ɗan manna ƙirjinsa da bayanta, tare da cuso kansa tsakanin wuyanta da kafaɗarta juyowa ta ɗanyi, hakan yasa fuskantar mannewa da tasa cikin yin ƙasa da murya cike da raɗa yace.
“Ganinki a haka zaisa na gaza cika ƙudurina Ma'eesha Taj ɗinki zalamemme ne, Amincin zuciyarki ne burin rai da ruhi da jinin jikina a yanzu, shi kaɗai zai hanani ratsa mallaki na, Please Babey ki soni dan Allah”.
Cikin sauri ta rumtse idanunta saboda jin yadda lfyarsa ke bayyana a jikinta, murya can ƙasan maƙoshinta tace.
“Taj lokacin salla fa yayi”.
A hankali ya juyota gareshi ruggumeta yayi tare da ɗaura hannunshi kan mazaunan nata, ya ɗan mara tare da ɗan matsesu.

“Washhh Allah na Taj zafi fa”.
Tayi tambayar cikin narkekkiyar murya.
Murmushin yayi tare da ɗan lakace hancinta kana a hankali yace.
“Raki ko? Shogoɓatuna ki koyi jarumta fa, saboda ke ba matar ragwo bace”.
Ya ƙare maganar tare da matse cinyoyinsa.

Ita kuwa da sauri ta buɗe mishi ƙofar tare da nuna mishi hanyar fita.

Da sauri Addawa ta janye kanta sabida hango yadda surarsa ke tsaye cir a cikin jallabiyar.
Kan sallayarta ta koma tana istigfari tare da yiwa kanta faɗar abinda tai bai daceba na tsayuwa kallon ma'aurata da tafi kowa sanin zuƙatansu cike da begen juna suke.

Ita kuwa Ishmah ido ta rumtsa kana ta juya  da sauri ta nufi ɗakinta.

Washe gari da yamma suna tsakiyar Parlour, miƙa mishi E passport ɗin tayi tare da zuba mishi ido dan so take taji me zaiyi dashi.
“Ina zakuje?”.
Addawa tayi tambayar dan taga alamun tafiya yake so suyi.
Yana mai ɗan taune lips inshi na ƙasa yace.
“Jordan zanmu je, Amman zamu fara ta Dubai?!”.
Da sauri ta kalleshi cikin jin daɗi yes Allah ya sani kuma duk wanda yake tare da ita yasan tana son zuwa Qatar da Jordan, Dubai ne ma bai wani cika damunta ba.
Girarsa ɗaya ya ɗan ɗaga mata.
Addawa kuwa da sauri tace.
“Afif ba Umrah zakuje ba, sai Jordan da Dubai.”
Yana ɗan jujjuya E passport ɗin yace.
“Ehh akwai abunda zanyi a Dubai da Jordan ɗin ne, masu mahimmanci.
Umrah sai mun dawo zamuje”.
Cikin sanyi Laylah dake gefen Ishmah ta ɗan kalleshi a hankali tace.
“Uncle Taj mu kaɗai da Addawa kawai zaku bari”.
Kanta ya ɗan shafa cike da son cire mata tsoronsa yace.
“Uncle Hamisu zaizo, shi zaike kaiku school”.
Da sauri tace.
“Yaushe zaizo?”.
Kai ya ɗan jinjina kana yace.
“Eh Next month”.
Cikin jin daɗi ta fara tsalle.
Ita kuwa Ishmah Addawa ta kalla jin tana cewa.
“Ku kuma yaushe zaku tafi?”.
Yana ɗan juyawa yace.
“Tuesday !”.
Cikin mamaki tace.
“jibi-jibi kuma?”.

Yana ƙoƙarin fita yace.
“Eh saboda akwai zaman da zamuyi da shugaban kamfanin sufurin jiragen sama na U.A.E  da Qatar Airline, shiyasa sukayi min komai na tafiyar, basu san inada mataba, sai yanzu da na gaya musu to suke neman E Password ɗin nata, dan su haɗa tafiyar tamu”.
Ya ƙare maganar yana fita.
Yana kuma mgnar zuci.
Dole in samu lokaci na musamman a ƙasa ta musamman a wurare na musamman domin in adana soyayyata a zuciya ta musamman, in tabbatar da Ma'eesha na a matsayin matar aurena ta musamman da fatan samar da zuriya ta musamman”.

Ita kuwa Ishmah ɗakinta ta nufa, tana shiga ta amsa kiran Garkuwa, a bakin gado ta zauna tare da gaisawa kana ta ɗaura ta ce mata zasuyi tafiya.

Cikin Murmushin Garkuwa tace.
“Ko kin fahimci cewa, mijinki na son samun dukkan lokacinki ne, da kulawarki, wata ƙil gani yake Qatar tayi muku matsin kusancin su Addawa shiyasa yake son ku arce Dubai da Jordan. Saboda so yake ku gina rayuwar da har gaban abadan bazaku manceba, Ishmah Taj yana da tsari a kanki, kiyiwa Allah da Manzonsa ki ɗauki magungunan ki da baki shanyeba ki tafi dasu. Ki kula da kanki”.
Cikin sanyi tace.
“Ni banda Ify ma fa, kwanan duk marata ke fitinata wlh dauriya kawai nakeyi”.
Da sauri Garkuwa tace.
“To kiyiwa Allah da Manzonsa ki ki samawa kanki da mijinki Ify, kayyakine, na ɗura ma ki su kin shasu kin tsumi, sannan kin hanasu damar fidda aikinsu, dan Allah ki bada himma kiga amfanin gyara”.
Ta ƙare maganar cikin yin ƴar dariyar da tafi kama data mugunta.
Tana ɗan kwanciya tace.
“Nifa ba wani abu bane  ni wlh ba ruwana”.
Cikin dariya sosai Garkuwa tace.
“Eh ai nima bance da ruwanki ba, ai Taj ne kaɗai zai gane da ruwanki ko ba ruwanki”.
Daga nan dai kuma tayi ta bata shawarwari na musamman.

Washe gari  zaune suke ita da Addawa Laylah na tsakiyar su, cikin kulawa da son cire mata mugun tunanin da aka sawa yarinyar ta kamo hanunta cikin sanyi murya tace.
“Laylah ki daina tsoron Uncle Taj, shi ba mugu bane! Kuma ba shi bane yake zuwa ɗakinki, ke kin sani Uncle Taj yana sonki bazai so abinda zai cutar da keba, bare har yace zai kasheki, ko akwai wani abu na mugunta da ya taɓa yi Miki!?”.
Da sauri ta fara jujjuya kanta cikin yaƙini tace.
“A'a bai taɓa min ko tsawa ba, kuma na sani shi ba mugu bane”.
Da sauri tace.
“To ki daina tsoronsa babu abin da zai miki wancan ma ba shi bane sharri akayi mishi”.
Cikin sanyi ta ɗan jinjina kanta tana tunano wasu abubuwan da suka gabata sai kuma ta kalli

Ishmah tare da cewa.
“Allah ko Aunty Ishmah?”.
Cikin son sama mata nutsuwarta tace.
“Wallahi sharri ne Laylah ki yarda dani”.
Cikin sanyi tace.
“Na yarda Aunty Ishmah nasan Uncle Taj ba mugu bane”.
Cikin jin sanyi Addawa tace.
“To ki daina tsoronsa ba abinda yayi miki kuma ba abinda zai miki”.
Cikin sanyi ta gyaɗa kai alamar to.

Washegari ranar Tuesday.
Da safe misalin ƙarfe bakwai saura jirginsu ya ɗaga Hamad International Airport Doho Qatar, suka miƙe zuwa Dubai kasan cewar tafiyar.
1 hour and 12 minutes ne Qatar, Doho to Dubai, shiyasa ƙarfe takwas da kwata dai-dai jirginsu yayi landing.

Suna isa suka samu tarba ta musamman daga shugaban Dubai Airline ɗinsu da zai shugabanci taron da zasuyi na yankin Larabawan.

Cikin sauri ta juyo ta kalli Taj ɗin dake zaune gefentan dai-dai lokacin da taga sun kutsa cikin...!

*Littafin INDA RAI na kuɗine ki biya kuɗinki ki karanta cikin aminci ba haƙƙin kowa a kanku. 1k ne kacal 0661110170 GTBank Aisha Aliyu Garkuwa sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 09097853276*

By
*GARKUWAR MARUBUTA*

********************** ? **************************
********** Ai Hausa Novels ****************
************************? **********************

DOWNLOAD More complete Hausa Novels, Education Books, Adventure, Drama, Mystery, Religion, Fiction, Non-Fiction, Romance, Meimor, True Life Stories & Others from our blog.

Visit > https://www.aihausanovels.com.ng

Ka tura mana sako ta adireshinmu na email, domin tuntubarmu ko turo mana hausa novel ko

kuma post.

Email > aihausabooks@gmail.com

******* FOLLOW US ******

Facebook: Ai Hausa Novels

Twitter: Ai Hausa Novels

Telegram Channel: https://t.me/Aihausanovels

WhatsApp Number: 08138873799

Haka kuma domin shiga kowanne daga cikinsu za ku iya ziyartar shafin ku yi search na AI HAUSA NOVELS, hatta facebook group dinmu ma za ku samu.

********************** ? **************************
*************** Ai Hausa Novels ****************
********************** ? **************************